Copied By
YAYA HAYAT
(admin
Hayat hausa novels
Hausa novels and fashion
Cool novel, makeup and kitchen1
AND
Cool novel, makeup and kitchen2)

WHATSAPP NO:
+2347039625239
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(1)

Danja na tsayar da motocin bakin titi suka taho a guje kowa da abin siyarwarsa kowa na tunkarar motar da yake kyautata zaton dacewa dan ya siyar da abinsa,

Da saurinta ta tunkari jar motar da wani ya matsa dan rashin daidaituwar cinikinsa da mamalakin motar, tana karasowa ta dago farantin hanunta tace" ga gwonda, ga abarba, ga ayaba Hajiya zaki sayi ?

Matar dake cikin motar ta dan kalota ta yatsina fuska ganin macece mai siyarwa sannan ba yarinya, cikin Isa ta ce " nawa

Yarinyar ta ce" Hajiya gwonda dari bibiyu, abarbar dari biyu da hansin ayabar kuwa naira arba'in arba'in

duda kudin da ta fada bai kai na Wanda hajiyar ta kasa saya ba aman sai da ta ce" ke ga dubu guda kiyi ki zuba min aman a kowane na cire naira ashirin idan kinyi ki zuba idan baiyi miki ba sauran sakan 10 danja ta saka sai ki kara gaba domin karnin rana kike

Da saurinta ta ajiye ta zubawa hajiyar ta mika mata inda ta cilo mata kudin ta duka ta dauka jikinta na kyarma,

Tana jiyowa taji wani shima da wata matar ta cilo masa yana fadin Hajiya saura naira ashirin da biyar ta ce" bani da ita

ya girgiza kai da yake shakiyi ne sai yace " Allah ya baku a nan, mu kuma ya bamu a can

ta bude gilas din motar ta ce" kan uba... Sai jama'a suka dameta da Horn domin danja ta saka ga mutane da gajen hakuri, haka ta leko ta maka masa dakuwa ta gilas din motar shi kuwa yayi mata gwalo

à haka suka samu suka koma bakin titi kowa da abinda ke kansa

karfe 1 na rana du suka kama hanyar kai balas domin yawancinsu basuda jarin yin hakan à gidajensu sai dai su je wajen masu yi su dauka su je tallah abinda suka yi à fita hakinsu

à hankali ta kali na kusanta Wanda da alama shine jininsu yafi haduwa tace " Sabiu, ka dan rike min kudin nan mana, na gyara zaman abarbar nan tayi nauyi da yawa gashi kuma tafiyar tamu da nisa

Wanda aka kiraya da Sabiu ya karba yace " haba bari dai, yau ai sai hamdala ke ai naga kinyi ciniki, nifa dari uku kawai nayi

daga can wani ya dauki magana inda yace " ba dole tayi ciniki ba, tana cinye hakin al'umah, wannan Hajiyar ai ni na fara zuwa wajenta aman da yake ita kinibabiya ce sai ta rage mata kudi dan ta Riga kowa siyarwa, ai ta Allah ba taki ba yau kema kinyi tsawar

Sabiu yace " kaga dai bala bata tanka maka ba, dan haka ba abinda ya dameka da ita, injin dai ai kowa rabonsa yake ci ko

bala yayi kwafa yace " eh hakane, aman wani na cin rabon wani, ni inba jaraba bama mai hadin mace da tallah da shiga cikin maza, yanda zamu fita da gudu haka itama, yanda zamu yi ihu da kugin tallah haka itama, ha jaraba bata Gajiya KO kadan, yanzu tana komawa ta kuma daukan wani tallar sannan ita ba wani ganinsa ake à jikinta ba sai dai ta je ta kashewa tsohuwar da KO yanzu KO yanzu, aman mu ta hana mu samu

sai a wannan lokacin yar budurwar nan ta mika hanu ta karbi kudin da ta baiwa Sabiu riko, ta juyo ta dan kali bala ta ce" Bala abinda ya kamota ka tabatar Yana nan yana sandonka, yau KO ba tsufa akoy mutuwa, gwara ni ina anfanar wani, sannan ina rokon Allah da ya salihe min, Alhamdulilah yau bada'ace min barauniya ba, KO karuwa, KO marokiya ba domin kuwa du talaucin mu ni nan *NEMAN NA KAINA* nake,

tana gama fadar haka ta juya cikin nutsuwa ta dauki wani layin daban dan kuwa bazata juri tafiya da bala ba domin shi à kulun neman fitina yake da ita

kafin su karaso har ta kai kudinta da abinda ta rago ya cire naira dari uku ya bata, inta ta dauki hanyar dan kangon su duda irin nisan wajen,

à hanya ta tsaya ta sayi garin kwaki ta sayi siga, ta karo da shinkafarta da yan kayan miya ta rike canjin talatin da biyar à kudin ta nufi dan takulalen bahun da sukayi kofa da shi

tana zuwa tayi salama, Inda ta karasa cikin gidan bakin inuwar mainan da à nan wannan tsohuwa ke zaune tana dan shan iskan wajen, tana hango wannan budurwar sai ta fara dan washe dadashinta domin kuwa ba hakori KO daya à bakin

budurwar nan ta karaso cikin nutsuwa tace " ina, kin gaji KO ? Kiyi hakuri, bara na kama ki kiyi sallah na baki abinci sai na je daukan gwonjo, kinga yau harda shinkafa irin ta gwomnati na bada aka zuba min sai na dafa miki KO ?

à hankali ta tayar da tsohuwar inda ta dago da kanta ta zubawa fuskar yarinyar ido, can cikin irin muryar tsofafi wa'inda suka jigata tace " Allah yayi miki Albarka *NURIYAH*

Nuriyah tayi murmushi ta dan share hawayenta ta kara kama ina da kyau dan dorata a peau tayi mata alwallah tayi sallah

bayan ina ta salamce sallar da ta kwashi wajen minti talatin domin kafin ta duka kadai aiki ne, ta juyo à hankali ta yafito Nuriyah,

Tana zuwa sai ta dan suko tana juya garin da ta dama cikin nutsuwa, Ina tace " shin bakya kyankyamina ? Bakya tsoron cutar dake jikina ? Kinsan fa ana daukanta , Nuriyah ki ringa kiyayewa dan Allah domin duka duka shekarunki 18 , baki ma fara rayuwa ba Nuriyah,

tari ya turnuketa domin hakane kadan tayi magana mai dan tsayi tofa sai tari yace bismillah, abinka da tsufa kuma sai fitsari yace bazai tsaya ba,

Nuriyah bata ce komai ba ta dan girgiza kanta taTa girgiza kanta ta Mike ta.....

Somin tabi kenan, taku ce yar mutan Niger
ϘϘϘ NEMAN NA KAINAϘϘϘ

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(2)

Nuriyah ta dan girgiza kanta bata ce komai ba ta Mike ta dauko wani zanin dake shanye a jikin igiyar hanyar da ta kula ta kama ina ta canja mata na jikinta bayan ta zuba mata ruwa a fitsarin , à hankali ta goge wajen ta dan jingina ina da jikin mainan tsakar gidan Wanda da alama nan ne wajen hutunsu su duka, cikin nutsuwa ta dauko garin nan da ya gama jikuwa da ruwa da dan siga kadan ta gyara zamanta tana baiwa ina a bakinta tana goge mata idan ya zubo, à haka har ta gama bata ta kara goge mata sosai, ta gyara mata zamanta,

Ta saka Inna gaba tana kalo har baci ya fara daukanta a haka, cikin sanda ta mike ta darwaye kofin ta Adana sannan itama ta dauko nata kofin ta jika garin Yana gama jikuwa ta kunshe shi a farar ledarta ta sauran sigan ta juyo a hankali ta furta sai na dawo innata

Haka ta kada kai ta fito ta dauki Baban layi inda ta dire a layin yan gwonjo, tana zuwa ta dan dakata ya gama ciniki da wasu mata

Yana gamawa ya juyo ya watso mata kalon kaskanci cikin izgili yace " ke malama meye kuma ?

Nuriyah ta sada kanta cike da fargaba da tsoron yau fa an tabo shi Allah ya sa ya yarda ya bata gwonjon, cikin ladabi tace " daman nazo daukan na tallah ne

Ya kwasheta ya jefar da idanuwansa ya ce" kinga baiwar Allah, kawai ki tashi ki kara gaba, domin kinga dai bana son masifa, haka kawai ina zamana, ni ai canma bansan cutar dake damun kakarki kenan ba, ai da ban wani taimaka miki ba, à gaskiya bazan dauki kasadar karin rabarki a kusana ba aje kema cikin cutar kike na gogi jaraba, dan haka kar na kuma ganin kafafuwanki a nan wajen idan dai ba sayen gwonjo kika Zo ba, ke kuwa talauci yayi maki kanta ba ke ba iya sayen gwonjo dan haka kawai Allah ya raba hanyar mu

tunda ya fara maganar nan idannuwanta suke kansa, ranta a mugun bace, zuciyarta na tafasa, ta nikaf dinta take kalonsa, can ta girgiza kai ta mike tana share hawayen idannuwanta, kanta ya mugun daukan zafi, ita ta rasa kan al'umah, shin daman haka dan Adam din yake ? Daman su musulman nan haka suke ? Ita sai ta rantse à rayuwarta mutanen da ta sani basu yi mata gorin rashin lafiyar inna ba, ta rasa mai yake damun wasu mutanen, yanzu shikenan dan abincin da suke samu suna ci suna rufawa kansu asiri shima sai an bi an lalata kenan ? Yanzu idan ta rasa sana'ar yi ina zata dosa, ya zatayi da cikin innarta ? Gashi kuma Inna na bugatar abinci sosai duba da yanayin rashin karfin jikinta,

À hankali ta kali sama tace " Allah gagara misali, Wanda baya baci, kafi kowa sannin halin da nake ciki, ni kaina ka fini sani, ya Allah ka sanyaya min zuciyata, ka kashe min wutar dake kokarin kuno kaina,

Batai kasa da gwuiwa ba ta bi layin yan buga hula, inda ta samu wani datijo Yana irin laya sun nan, ta duka har kasa tana gaishe shi

dan dakatar da abinda yake yayi Yana amsa gaisuwarta Yana Yi mata kalon karin bayani

À hankali tace " dan Allah baba taimako nake SO, à bani aikin yi, koda zubar da ruwan buga hular nan ne, KO wankin hular, KO zuwa na siyar

Ido ya zuba mata, ita dai gashi gaba daya jikinta kaya ne bakake ba'a ganin koda tafin hannunta duda irin zafin garin aman komanta à rufe ruf, ita dai ta haka bazaka iya gane shekarunta ba duda muryarta ta yara ce, aman ba wani iya kiyasta mata shekaru zaka yi ba, kuma tazo tana neman aiki irin na maza, ya dan girgiza kansa, ya sani wannan talauci kadai zai sakata yin hakan, sannan dai cikin biyu tabas ta kasance daya, idan har ba barauniya bace tofa ta cika tsoron Allah à zuciyarta domin yan matan zamanin nan da wuya kaga mace yar budurwa du muninta tana *Neman na kanta*, Sam sai dai su bi wata hanyar dan à ganinsu itama sana'ar ce, hakan ya saka shi dan tsorata da lamarinta ya ce" Baiwar Allah, ke macece, yanzu a nan wani kalar aiki ne zan baki ? Kinga dai wankin hula idan mun dauki yan kama mana aiki du hula guda komai datinta KO rashin datin naira talatin ne muke bayarwa domin muma à ciki muke ci, kinga kuwa ranar da babu huluna da dama bazaki Sami wani abin ba,

Nuriyah Ta ce" koda da naira talatin din na tashi alhamdulilah, dan Allah ka taimaka min da aikin nan domin sai *Na nemi na kaina* dole nake ciyar da innata

Ba karamin tausayinta yaji ba, hakan ya sa yace ta dawo daga gobe ta fara aikin tunda sasafe domin anfi SO rana ta busar da su wa masu su

Ba karamin dadi taji ba ta duka har kasa tana godiya ta juya ta nuinufi Hôtel din da take samun dan wankewanke Idan ta gama a bata Bata sauran abincin da mutane suke saya su raga,

Haka ta gama ta taho gida da jidijidin abinci domin kuwa a ranar an Sami saura da yawa, tana zuwa sai da ta dauko buhun da ta yaga take hanyar sauran abincin nan, ta kara kade shi da ruwa ta shinfida ta juye abincin tana yi tana kalon Inna dake murmushin gannin yau sun Sami sauran mai yawa, ta dan karaso ta ajiye Wanda ta debar masu zasu ci ta ajiye A gefen Innar sannan tace " Inna bara na sayo omo na wanke kayan mu, kinga sunyi dati ko

Dan lumshe mata ido innar tayi alamar ansawa ,ta juya ta fita dan sayo omon ashirin tayi musu wanki

Bayan ta sayo ta taho a hankali sai ga Yayan gidan saratu, suna KO ganninta suka fara"" mace mai bin kasuwa, balagaza, mai bin shaguna, tunkiya, mace mai neman kudi barauniya, yar gidan mai *KAnjamau* mataciya

Nuriyah ta kara sauri dan ta karasa gida tayi musu wankinsu domin kuwa inda sabo ai ta saba da irin cin kashin da ta'innan bayin Allahn ke yi mata,

Tana shiga ta dauko dan bokicin su da ta saya ta jawo ruwa ta zuba ta fara tsoma kayan innarta yan zannuwanta ta shiga wankewa ba tare da ta juya tayiwa innar magana Ba gudun kar ta gane halin da take ciki,

Juyowar da zata yi dan shanya zanen innar kawai sai gani tayi innar à wani sankare idannuwanta à kakafe, bakinta à dan bude, da alama dai Inna bata lumfashi, ai Bata san lokacin da tayi facali da kayan wankin ta nufi innar da gudunta tana fadin Inna, Inna, cikin wani irin karaji da tashin hankali

😑 ya rab shin Inna ta rasu ne KO kuwa ? 😑, Inna kakar Nuriyah ce KO kuwa ? To su basuda dangi ne ? ♀♀♀♀♀ , , inda na kuskure ayi min uzuri, taku ce *Sajida*

Copied By*♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀*

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(3)

Cikin tsoro da sasarfa ta karasa à hankali ta daba ina bakinta na rawa tace " Innata, Inna lafiya ? Inna jikin ne ?

Ina ai Sam bata motsi, hakan ya kara firgitata ta fice da gudu, tana fala gudu har ta iso kofar wani dan madaidaicin gida, ginin suminti, tana isowa zata tura sai ga wata yar karamar mota ta tsaya à kofar gidan hakan ya sa ta dan dakata jikinta na bari

Na cikin motar ya fito wani dajito à kala zai kai shekara arba'in da kamar shida, yana ganninta ya hada rai ya ja uban tsaki ya matso ya ce" ke lafiya ? Mai ya kawoki gidanna ? Mai kike neman min à nan ?

Nuriyah ta langwabar da kai tana shashekar wahala tace " Aba , innata bata motsi, kazo ka taimake ni Aba innata ta Sankare bata motsi

Ya ja wani uban tsaki yace " toh sai mai ? Dan Bata motsi ? Da tsufanta à kanta ta je ta jajubowa kanta masifa ba ? To motsin mai kike SO da tayi ? Ai daman karshen masu irin cutarta kenan, sai an wulakanta sannan à shige cikin kasa ba KO yar tsokar da walakiri zai daka, wannan ai bakin ciki ne, ina zaune lafiya da iyalina ki Zo ki tayar min da fitina, to dan ubanki KO mutuwa tayi sai mai ? À kanta aka fara mutuwar ne ? Bace min da gani kije ki nemi kwarton da ya lika mata masifar yaje ya turbuneta idan kuwa ya rigayeta gangarawar kema ai mutun ce kije kiyi rami kawai ki bineta, dan kuwa ni KO kwondalata bazan bayar ayiwa wata tsohuwar banza sutura ba,

Yana gama fadar haka ya juya yayi cikin motarsa yama fasa shiga gidan nasa ya juya ya bar anguwar

nan ta zube yarab ta rintse idannuwanta ta dora hannu à samman kanta sai ga hawaye wani na korar wani

wata kamilaliyar murya taji anai mata salama ta dago da kanta ta sauke à furkar wani tsoho mai cike da kamala, da carbinsa à hannunsa ya sha farar jalabiyarsa da alama zai je wajen sallah ne

A hankali yace " yarinya lafiya ? Mai ya sameki haka kike zaune Kina kuka a nan ?

cikin karaya zuciya Nuriyah ta ce" na rasa gatana, innata ta rasu, tana gida à shinfide

Yayi kasakai cike da tausayi ya ce" Inalilahi wa'ina ilaihi raj'une, kulu nafsin za'ikatil maut, kiyi ta maimaita sunnan Allah yarinya, sannan ki daina cewa bakida gata, domin kuwa gatanki Allahnki, ki sani ya fiki sonta shi yasa ya karbeta, kiyi mata fatan samun makonci mai alkhairi, shin yarinya to ina abanki yake ne ?

Nuriyah ta kuma fashewa da kuka tace " bani da shi, hasalima banida kowa sai ita kadai, banma san ya zanyi da gawarta ba, banida kowa sai Allah, kudin wajena naira goma sha biyar ne ya rage min na aiki da nayi, banida komai sai ita, gashi bamuda kowa à duniyar nan

Zuwa wannan lokacin shi kansa wannan bawan Allah jikinsa gaba daya ya mutu, haka dai ya jure ya ce mata " tashi mu je a nemi bayin Allah su kama ayi mata sutura kiyi ta maimaita sunnan Allah, shi zai sanyaya miki rayuwarki

Haka ta Mike ta bi bayansa tana kwatanta masa har suka ISO kofar gidan inda tun kafin su ISO ya dan kikirayi mutanensa ya nemi alfarmar su Zo suyi aikin lada,

cikin ikon Allah nan da nan mutane suka fara taruwa inda har mata tsofafin anguwa suka shiga cikin gidan daidai an kawo likafani suka yi mata wanka suka shiryata suna zubar da hawayen tausayin kansu domin itafa tata ta kare, sai kowa yayi ta kansa wato dai nafsi nafsi,

Nuriyah na zaune tana ji tana gani maza suka dauki innarta aka saka à bayan irin motar nan à kori kura suka tafi da ita, daga nan Bata kuma sannin inda kanta yake ba, sai bude idannuwanta tayi ta ganta a saman gadon asibiti, hannunta jone da karin ruwa

likita ne ya turo ya shigo da wani saurayi à bayansa na biye da shi, sai à wannan lokacin ta dago da idannuwanta ta sauke kan wata tsohuwar mata mai cike da kamala wace sai à sannan ta ganta,

tunaninta ne ya katse lokacin da likita ke cewa " bata dauke da ciwon kanjamau, abinda ke damunta à jikinta rashin isashen hutu, rashin kwonciyar hankali da kuma cutar cizon sabro, wa'innan abubuwan ne suka hadu suka bada gudumunwar shinfidar da ita, aman yanzu wannan hutun da ta samu na koma da ta shiga har kwana shida ya dan rage wasu abubuwan fannin damuwar domin idan idannuwanta à bude ne kirjinta yake yawan bugawa,

katse musu magana tayi lokacin da ta gama fahimtar yanzufa ba innarta, to kodai mafarki ne tayi, domin kuwa innarta ai Bata kai wajen kwana shida da rasuwa ba, aman abin mamakin shine su kuwa wa'innan su waye su ? Mai suke nema a nan ? Cikin muryar marar lafiya tace " *Ina Innata*? Ku kuwa su wanene ku ?

À tare suka juyo suna kalonta, inda naga wannan tsohuwa ta dan matsa nesa kadan da gadon tana kalonta ba tare da ta furta komai ba,

À hankali wannan dan saurayin ya matsa kusa da gadon da take kwonce ya ce" kin farka ?

Nuriyah ta kasa magana sannan baci ya kuma daukanta à hankali,

likitan ya gama yi musu bayani ya juya ya fita,

yana fita wannan tsohuwa tace " kai Mubarack karka kuskara ka matsa kusan yarinyar nan, kaji fa ance ga abinda ya kashe kakarta, ni Sam ban yarda da wannan likitan ba da gani macuci ne ya saka mu mu kwashi masifa mu kai gidan mu, ai indai taimako ne mun taimaka mata iya gwargwadon iyawar mu dan haka kawai ka mayar da ni gida kaima ka koma bakin aikinka karta jaza maka à koreka domin kasan da aikin nan naka muka dogara gaba dayan mu

Mubarack ya danyi kasakai Yana sauraron maganar maman sa, can ya nisa yace " to baba ki cire mata wannan abin na fuskarta KO tayi nunfashi da kyau kinga dai ni

namiji ne ba muharaminta ba, aman ke macece ba komai, wly ba abinda zaki goga ai kinji abinda docter yace

ta watsa masa harara ta ce" sanu sarkin ilimi, Wanda yafi uban kowa ilimin adinni, wannan iya yin naka irin na mahaifin ka bazai saka na biye maku ku kaini ku baroni ba, dan haka umarni nake baka ka fice min mu tafin tun kafin nayi mumunan furuci à kanka Mubarack

Jin haka ya sakashi juyawa hankalinsa gaba daya À kan Nuriyah ya bi bayan mahaifiyarsa dan cika umarninta.....

♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(4)

Bayan tafiyar Mubarack da mahaifiyarsa Nuriyah ta kai wajen wata awa tana bacin wahala domin alurar baci docter ya saka mata à karin ruwan dan ta samu isashen hutun zuciyarta

À hankali ta fara bude idannuwanta da suke shanye, daman ga magana ga abin baci sai suka bada kalar idannuwan mashaya, à hankali ta kara gyara nikaf din da ban taba ganin inda ta cire shi ba, a hankali idanuwanta ke zubar da hawaye, cikin dakusashiyar murya ta furta inalilahi wa'ina ilaihi raj'une, Allah ya sa bakin wahalarki kenan innata, Allah ya jikanki da rahama, Allah ya sa can ta fiye miki nan, tabas mutuwa bata shawara bata fadin cewar tana hanya, kawai dauka take, sannan ba ruwanta da yaro KO baba, KO maraya KO mai iyaye, ba ruwanta da talaka KO mai kudi, ta lumshe idanuwanta ta bude kuma can ta ce " astaghfrullah, Allah n'a tuba ya Allah,

À hankali ta sauko daga saman bed din asibitin tana dan dingisa kafa ta bude, tana yiwa daular dakin asibitin bankwana,

Sai à wannan lokacin ta Tina fa KO naira biyar babu a hannunta KO kudin ruwa bata da shi, taso ta nufi gidansu haka kawai taji bata mararin hakan, ta juya a hankali ta dauki hanyar yan hula

Tana isa ta samu an jibge hulunan, Dan nesa kadan da shi ta tsuguna ta gaishe shi

wannan Karin fuskarsa ba fara'a domin ya fara tunanin yarinyar nan ko wata mayaudariya ce, Hakan ya Sa ya amsa mata ba yabo ba falasa

Can ya dago yana kalonta yace" baiwar Allah lafiya? Naga kin zo munyi magana kuma kika dauke kafa, injin dai lafiya?

Nuriyah ta Kara dukar da kanta cikin alamar kuka tace " kayi hakuri, rasuwa ne aka yi min, kakata ce ta rasu kuma daman ita kadai tayi min saura shi yasa na zauna har yau

Wani irin tausayinta ne ya dirar masa, hakan ya saka bai Kara furta komai ba ya hada mata tarin huluna da uban sokilin da sabulu da komai, Haka ta tatara ta koma gefe tayi bismillah ta cire safar dake hanunta, hanayenta wani irin fari ne da su sai nayi tunanin yanayin zapin safar dake hannunta dare da Rana, hankalinta ta maida sosai ta shiga wanki hulunan nan

Ba ita ta Mike ba sai karfe daya da minti ashirin ta tashi ta Jere su wajen da ake shanya masa huluna

waje ta samu ta Dan rabe tana raba ido domin bata je ta ce masa ya biyata ta gama ba,

Suna haramar Shiga masalaci ya Lura da ita, cikin tausayawa ya irga hula hamsin daidai ta wanke ya irgo 7500 ya mika mata, har rawa hannunta yake ya karba tayi ta zuba godiya ta juya ta tafi

Tunda ta shigo layinsu ake Binta da ido da kalon tausayi wasu kuwa kyankyami,

gabanta ne ya yanke ya fadi lokacin da ta hango ana zubda yar sauran katangar gidansu ita da innarta,

Dafe Kirji tayi ta kwalalo ido ta nufi wajen da gudu tana tambayar kai Malan lafiya??????

Ya salam shin ina Nuriyah zata nufa? ♀♀♀♀♀♀♀♀♀
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(5)

Tambaya take kai Malan lafiya ? Mai kakeyi haka ? Wa ya sakaka zubar da gidan nan ?

Masu aikin suka dan dakata sunai mata kalon tausayi da kuma tsoro domin Wanda ya saka su aikin ya fada musu mutuwar kakarta ya haukatata sannan cutar

kanjamau ce ta halakata dan haka yake son ya zubar da ginin nan yayi wani à wajen ita kuwa ya maida ita kauye

Tambaya take aman ba Wanda ya bata amsa,

Wani yaro da yazo ficewa ne yake ce mata" ke yar gidan tsohuwa mai neman na kanta, kinga wannan datijon mai mota ja ne ya Zo tare da masu aikin nan aka shige rushe ginnin, yace wai kin haukace tunda tsohuwa ta mutu

Da sauri ta rintse idannuwanta sai ga hawaye sharr suna bin kumatunta, ta juya tana taka kafarta da kyar ta nufi wajen masalacin anguwar inda tayi canji a kudin aikinta na yau ta nemi waje ta zauna duk inda yara zasu fice sai ta kiraye su ta mika musu tana fadin ku tayani da adu'a, Allah ya jikan tsohuwa, sannan ya jikaina ya dafa min, sai kuwa yaran su artaya da murnan su suna fadin Allah ya saka maki da alkhairi

wata murya ce ta tsinto tana fadin" sadaka maganin musiba, sadaka falala mai yawa, Allah ya bamu ikon bayar da sadaka da zuciya guda,

saurin dago da kanta tayi tayi arba da wannan datijon arziki, Wanda à tsahon rayuwarta shine mutun na biyu bayan inaRta wa'inda suka taimaki rayuwarta domin Allah

cikin yanayin farin cikin ganninsa ta kara dukawa daga zaunen da take tana gaishe shi

ansawa yake hankali kwonce Yana kara karantar nutsuwar yarinyar

can yace " ya Akayi kika gudu daga asibitin ? Abdul wahid yazo yake ce min ya koma bai sameki ba, kinsan shine Baban yarona yayi ta nemanki, shine yanzu da na fito daga masalaci na nufi gidan naku sai na tarar da mumunan labarin wai wani mai jar mota yace à rushe ginnin

Y'ata, ina son ki fada min takamaimain labarinki domin sosai nake jin tausayinki a cikin raina, shin mainene ainahin labariki ?

Nuriyah tayi Jim can tace "

À yanda innata take bani labari, kakana na wajen mahaifiyata sunansa Elhaj Abubakar mai wazobiya, ya kasance cikaken musulmi mai sauke baki à gidansa, wato idan dai taimako sai mai wazobiya, haka ne takensa

Elhaj abubakar matarsa daya wace Allah ya azurtata da haihuwar Yaya mata har hudu domin biyu tagwayu ne sai kuma biyun na baya, Aïcha, Farida, sai hasana da hussaina,

sosai Elhaj abubakar yake cikin hatsari duba da irin sana'arsa wato siyar da gwal, hakan ya saka yake taka tsantsan da rayuwar iyalansa, à koda yaushe suka tashi koda fita da wani saurayi daya ya yarda dari bisa dari shine yake tuka iyalan Elhaj Abubakar wato lawali mai kyau

lawali mai kyau dan unguwar ka taka ne dake à cikin kano, gidan su lawali mai kyau talauci har ya fito ya shaida kansa aman shi lawali akoy shi da gwali hakan ya saka baya kwana à gidansu Sam sai dai yaje gidansu abokansa ya kwana abinsa, sosai Allah ya bashi halitar kyau à jikinsa duba da yanayin tsarin halitarsa Tun daga kansa har kafarsa

sosai yan matan anguwar ke sonsa domin ya iya gayu da suturar abokansa ga kyau hakan ya sa aka yi masa lakabi da lawali mai kyau

lawali akoy biyaya ga masu kudi, ya jima Yana yiwa Elhaj abubakar yan aikace aikace à shago, harda su shara da komai, sannan KO sau daya Elhaj abubacar bai taba kama lawali da wani mugun abin ba, hakan ya saka ya kara yarda da shi harma ya biya masa ya samu takarda ta shaidar tukin mota,

Zo ka ga gwali wajen lawali domin saima ya daina yiwa gajaje magana har fadi yake ai yanzu kuma ya fi karfin ajinsu

Tafiya tayi tafiya inda Elhaj abubacar ya kara yarda da lawali dari bisa dari har ya yarje masa sannin gidansa ya bashi mukamin tuka matarsa Hajiya Halima da kuma yayansu mata

Shakuwa ta musaman ta shiga tsakanin Ousseina da lawali domin kuwa wani irin sonsa take da zuciya daya, Ouseina ta kasance kunu huce in shaka ce, ita bata san wannan kalma ba wai rigima, tunda lawali ya nuna cewar yana sonta sai kawai taji ta yarda da shi dari bisa dari

Tafiya tayi tafiya har soyayar ouseina da lawali ta fito fili inda Hajiya Halima cikin gurbataciyar hausarta ta samu mijinta take shaida masa wannan labari

Sosai Elhaj abubacar yayi murna da hakan domin kuwa shi fa ya yarda da shi ba dan kadan ba, nan da nan ya same shi yayi masa maganar kawai ya turo magabatansa ayi maganar aure

budar bakin lawali sai ya fashe da kuka Yana fadin " Aba ni maraya ne, banida uwa banida uba, dangina ban san inda suke ba, yanzu haka haya nake à dan dakina ni daya, shi yasa nake ta faduwar gaban ranar da dan nemi Aure, ya kuma fashewa da wani kukan

Elhaj abubacar ya mugun tausaya masa yace" kayi hakuri lawali, kayi hakuri, haka Allah ya so, ni zan aura maka ouseina sannan na baku gidan zama, abinda nake SO da kai shine ka rike amana lawali ka rike amana, ka sani du Wanda ya riki amana to fa Allah zai biyashi, idan kuwa kaci amana Allah ba zai barka ba

tamkar lawali ya kwonta haka yake godiya Yana washe hakura,

Yana komawa anguwarsu ya je gidan su budurwarsa Saratu inda ya kwashe karya da gaskiya yake fada mata zancen auren ya kara da fadin " my Sarah, ke kinsan ina sonki, sannan wannan Aure da zanyi auren jari ne dan nima ba samu na kaina, ina samu zan baleta ta tafi gidan ubanta muci gaba da rayuwarmu da yayanmu

Saratu tayi na'am da shawarar lawali domin à yanda take ji da kanta tana SO itama yau ace kaf cikin layinsu itace ta farkon da ta fara shiga gaban motar mijinta, dan haka ta yarjewa shawarar sa

KO wata ba'a saka ba inda elhaj abubacar ya yiwa lawali gata, ya aura masa Ouseina ya basu gida mai kyan gaske ya zuba musu kayan alatu sannan ya malaka masa mota ya bashi jari

tirkashi dagin kai sai ya karu inda kwata kwata ma ya dauke kafarsa daga anguwarsu mahaifansa daman kunya yake ace wai sune mahaifansa domin talauci ya saka har sukayi kamar sun wani masakance domin kuwa basuda hakuri, kuma Allah ya basu yaro maran Jin kai

Watanin farko daga wata daya har zuwa wata hudu Ouseina ta sha lele wajen lawali inda take zaune lafiya da mijinta da kuma mai aikinta inan sudan matar da take yiwa mahaifiyarta aiki da aka yi mata Aure sai aka hadata da ita dan ta kula da lamarinta

Sosai Inna ta karanci halayar lawali abinka da tsofafin da da basa baci Alan Aman Sai tayi shiru da bakinta domin furta wani abin à nan ba huruminta bane, ita dai tana iya yinta dan ganin Ouseina à cikin farin ciki

wata rana Ouseina na zaune da magariba kawai sai Jin dirar motoci tayi da guda ana shigowa gidanta,, ba Wanda yayi mata magana aka bude dakin dake kusa da na mijinta hannun dama aka shiga da matar

Cirko cirko suka yi suna kalon ikon Allah bayan fitar masu kawo amaryar nan, sai ga lawali ya shigo da babar rigarsa Yana washe hakori

Dan matsawa tayi cikin sanyin muryarta tana fadin " mai gida ,Aure ba ka kara ?

Lawali ya zuba mata ido Yana shirya karyar da zai mata, ya lemun kuwa sai cewa yayi" kai Ouseina da abin dariya kike, abokina ne yayi Aure shine fa na taimaka na basu dakin nan kafin Allah ya bashi ya ginawa matarsa gidan ya sakata

Sai à lokacin ta sauke ajiyar zuciya, sannan wani amai ya Zo mata inda tayi bayinta da gudu tana kwararawa Inna nayi mata sannu domin ciki ne da ita har na wata uku da yan kwanaki

Baiwar Allah Ouseina ta yarda da maganar mijinta, domin kulun tare suke kwonci sai tsakar dare ya lalaba ya fada dakin saratu su ci karansu ba babaka ya dawo dakinta ya zube mata daudar

Kwonci tashi Ba wuya wajen Allah à yan watanin nan Elhaj abubacar ya fuskanci matsaloli da yawa à harkarsa domin barayi sun dauki abinda suka dauka

Magana yake da gadara inda yace" kai nawa na biyaku ? Na fada muku idan suka kawo muku gardama gaba dayansu ku kashe min yan iska ku kwaso min kudaden nan domin na jima Ina jiran irin wannan rana, dan haka na baku yau zuwa gobe ku tabatar da kun kwaso min arzikin Elhaj abubacar kun halaka shi da iyalan sa dan na samu na kaura gidan nan nasa da iyalaina

Ido na zaro daidai lokacin da wannan mutumin ya fada motarsa ya cire hular kansa domin lawali ne, haka ya harba motarsa bakin titi Yana tunanin daga an kashe iyalan Elhaj abubacar da shi din kansa shi kenan shi ya gama zama mai kudi, da ba dan ba da har Ouseina zai kashe aman ina Yana Jin dadin kasancewa da ita ga kyau ga biyaya, ga tsarin halita, dan haka ita bazai kasheta ba (ya rabƍ)

Zaune Elhaj abubacar yake inda wayarsa ta dauki ruri, wannan Kira na tara kenan ana yi masa dan haka ya yanke shawarar dagawa yayi salama

Ba'a amsa salamarsa ba sai cewa akayi" ka taba taimakona nima zan taimAkeka, ta tabatar ka tatara iyalanka Kun bar Nigeria, domin à yau karfe uku na dare zamu Zo da zumar kasheku mu kwashe dukiyar ku da takardun kadarorinku, dan haka kanada damar tsira awa biyar ta rage maku ku
Dif aka kashe,

Wata irin zufa ce ke karyo masa à zaunen da yake inda cikin sauri ya shiga wuleliyar motarsa ya nufi gidansa, Yana zuwa ya samu iyalansa, cikin Siri ya sanar da su nan da nan suka tatara du wani abin bukata à cikin daren nan suka fada wuleliyar motarsa suka kama hanyar barin kano

Hasana sai kuka take na yar uwarta inda mahaifiyarsu take rarashinta, cikin nutsuwa tace" mama, Ouseina, kar aje mutanen nan su cin mata idan suka rasa mu

Elhaj abubacar yace " hasana, Allah Yana tare da ita, ki sani, kinga Aure take, harda ciki idan muka rabata da mijinta ai mun Shiga hakinsa, na yarda da lawali nasan bazai Bari wani abin ya samu Ouseina ba sai inda karfinsa ya kare, dan haka insha Allahu idan wannan rigimar ta lafa zamu dawo mu daukesu da mijin nata muy tafiyar mu

Hakan kuwa akayi suka tafi suna kewar yarsu da kuma garin da suka zauna

Sam bai rintsa ba Yana jiran Jin dadadan labari , wayarsa na daukan kuka ya warta ya daga ya kara
Abinda ya ji ne ya mugun daga masa hankali, wai basa nan sannan kayansu ma basa nan,

Wata dunkulaliyar ashar ce ya dana inda ya mike ya fada dakin Ouseina Yana tambayar ta gidan ubanwa ubanta ya shiga

Tamkar mutun mutuni ta zama à zaune da cikinta na wata bakwai tana kalonsa, tun daga ranar baiwar Allah ta zamo abin tausayi domin ta gane saratu fa matar lawali ce kuma iyayenta basa kasar, takan zauna taci kuka iya kuka ba mai rarashinta domin ya kori Inna ta samu wani datijo ta aura mai kanjan Mota ne Suna zamansu lafiya

Nakuda ce ta tasowa Ouseina tun wajen karfe bakwai na dare inda a ranar taci dukan lawali wai ya Kamata da kwarto ya jibgeta da tsohon cikinta har ya la'anci abin cikin cikin ya jefeshi da sunan shege cewa ba nasa bane, ciwo cinta yake baiwar Allah Tana jan gindi har ta ISO kusan kofar gidan domin dakin na kusan tsoho mai gadi ya maidata da zama,
à nan ta haihu ta haifi yarta mace goshin asubahi inda mai gadi ya buga musu Yana shaida musu

À wannan ranar ouseina taga wulakanci domin à wulakance saratu ta saka wata reza ta yanke cibin ta daukin babyn ta ce" ai fa gidan ubansa za'a kaishi in yaso ita ta kara gaba,

Haka ya Dana mata saki uku, ya hana Mata yarta yayi mata korar kare

Tun daga ranar nan ba'a kuma Jin dariyar mahaifiyata ba, ni kuwa bayan kAmaR kwana uku da haihuwata ya kaini wajen Inna ya yar mata da gargadin kar ya kuma Jin KO ganin mu à inuwarsa
Ta karashe zancen tana fasheka da kuka

Sosai shima ya zubar da hawaye yace " to aman mai yasa ake cewa innarki nada kanjamau ?

Ta ce" wata tanarana na dawo daga makarantar boko inada shekara goma sha daya à duniya na tarar da innata sai kuka take à zaune, nayi saurin zama ina tambayarta lafiya,? Sai da tayi mai isarta sannan take shaida min mijinta ne aka aiko da kayansa wai ya rasu harda magungunansa,

Mutumin da ya kawo ne da kaizai Juya yake cewa innata wai ta fara daukan maganin nan domin kuwa cutar HIV ne ya kashe mijinta,

Tun daga wannan rana sai Inna ta kawo damuwa ta sakawa ranta, Sam taki ta sake sannan du wata uku saï ta kaini anyi min gwaji an tabatar banida ita, ita kuwa A kara mata maganinta mu dawo, gashi zuwa wannan lokacin karfin innata ya kare abinda zamu ci ma ya fara gagararmu hakan ya sa na fara sana'a ina *Neman na kaina*

ur comment plz♀
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(6)

Bayan ya gama sauraronta cike da tausayin rayuwarta, da ganninta ka san yarinya ce karama aman har ta iya jajircewa wajen *Neman na kanta* dan ta ciyar da marikiyarta da kuma kanta, duda ya san matarsa sai à hankali wajen halayenta aman zai jajurce dan ya taimaki rayuwar yarinyar nan domin kuwa ya yarda da tarbiyarta , ya gyara dan zaman da yayi yace " *NURIYAH* Allah ubangiji ya sa hasken ce ke, ki sani Allah baya dorawa rai abinda Bata iya dauka ba, Allah ya baki ikon cinye wannan jarabawa ta rayuwar ki, shi wannan bawan Allah, Allah ya shirye shi ya ganar da shi, mahaifiyarki idan tana raye Allah ya bayana ta da yan uwanki, insha Allah ni zan bada gudumuwa à rayuwarki domin rayuwar y'a mace a titi ba zata kaita KO'ina ba sai halaka,, aman kuma ina mai sanar miki cewar sai kinyi hakuri, domin zaman duniya sai da hakuri

da sauri Nuriyah tace " Allah ya saka da alkhairi aba, insha Allah zan kasance mai hakuri, ta ciro sauran canjin dake hannunta ta mika masa tana cewa kaga canjin

wankin hular da nayi à yau, an bani dubu bakwai da dari biyar, na sadakas da dubu gudan sai wannan

yayi murmushi bayan ya gama sauraronta, yace "Nuriyah, ki adanna kudin ki, ni zan taimakeki ne domin Allah, aman zan shawarceki da kina iya sayen sutura dan rayuwar yau da kulun kafin ayiwa yarona albashi ya siyo maki

Nuriyah ta mayar tana godiya,

Kafin su karaso gidan Malan Isyak sai da suka bi ta kasuwa inta ta sayi hijabai dinkaku biyu da fari kal da kuma ja, ta sayi irin dogayen rigunan nan suma biyu Masu dan kwali da baka da kuma kalar ja, irin masu saukin kudin nan inda ya rage mata wajen dubu uku, cikin Jin kunya ta mika dari biyar tace à saka mata pant, aka saka mata, ta sayi sabulu wani mai girma da ya birgeta ta sayi soson wanka da yar irin kano tayi zafin nan yar karama ta zuba kayan à ciki, da sauran canjin sai ta rike dari biyar ta sayo su abarba da lemo na dubu gudan da tayi saura

tunda suka tunkaro gidan ya kunshi adu'a à bakinsa, haka itama gaban na dukan tara tara tana tsoron mai zata tarar,

Da salama à bakinsa ya shiga cikin gidansa inda wata yar budurwa baka mai kyau ta taso tana amsa salamar mahaifin nata ta mika hannu ta karbi ledar hannunsa

Sanu da zuwa malan " cewar matarsa mahaiyar mubarack dake kokarin fitowa daga falonsu itama

idannuwa ta zaro ta nuno Nuriyah dake kokarin labewa à bayansa tace " mmmmalan meye wannan kuma ? Mai yarinyar nan keyi à gidan nan ?

Malan isyak ya ce" Haba Habiba ki Bari mu zauna mana,

Cikin ikon Allah sai bata kuma cewa komai ba ta juya cikin falon ta zauna ta rafka tagumi tana tunanin wannan ai musiba ce

à hankali ya zauna Yana karbar ruwan da safiya kanwar Mubarack ke miko masa sannan yace " zauna safiya ina son magana da ku

à hankali ta zauna tana dan yatsina fuska domin warin Nuriyah sosai yake juya mata kai,

gyaran murya yayi yace " Safiya, ka kawa kuma Yaya na kawo maki, wannan yarinyar dai abin tausayi ce, gatanta Allah, marikiyarta ta rasu bata da kowa à garin nan, ina rokonku da ku tayani muyi aikin lada har Allah ya bayana iyayenta ta koma gabansu KO idan ta sami mijinta nayi mata aure ta tafi gidanta

Habiba ta ce" Aman malan idan fa yarinyar nan muguwa ce ? Idan ta Zo gidan nan ne da wata manufa haka kawai hankalin mu à kwonce ta tayar mana da hankali ? An fada ciwon kanjamau ne ya kashe kakarta, daga ita sai ita suke rayuwa to taya za'ace wani ita batada ita ?, sannan ance yarinyar nan wuni take tana yawo wai tana *Neman na kanta* , mace ? Haba malan ya zaka yarda kuma ka kawo mana ita nan ? KO dai yarka ce malan ?

Malan isyak ya girgiza kai ya ce" eh to, d'a ai na kowa ne, aman ni ina son à kama mini, inai muku shawarar nan ne dan nasan kunada hakin hakan aman fa ku sani

lale lale yarinyar nan zata zauna à gidan nan cikin aminci, domin ni na isa da gidana,

ya juya cikin kakausar murya yace " ke safiya maza tafi ki nuna mata waje ta ajiye Jakarta ki gwada mata bayi sannan da wajen sallah, kuma da wajen kwonciya à cikin dakinki

da sauri ta kuma kalon mahaifinta hankalinta à tashe, ta mike tace " muje

haka NUriyah ta bi bayanta jikinta à sanyaye

suna shiga Nuriyah tace ? Malama kinga lungun can, ki ajiye tsumakaron ki, sannan koda wasa karki taba min kayana, ga bayin can idan kinyi koda wankin ido ne ki zuba isashen ruwa dan kar à bar mana sauran virus ya shafemu, sannan wancen karamar katifar sai Kina kwana à sama, kin fahimta kar ki shiga lamarina, sannan ba abinda ya shafeki da wayana i'm i clear ?

Nuriyah ta daga mata kai tayi exactly yanda ta ce mata

Safiyah ta watsa mata harara ta ja tsaki ta fita

À hankali Nuriya ta cire hijabinta ta ajiye à gefe, ta shige bayi Da sabulunta da sosonta, à hankali ta cire kayan jikinta ta rataye ta cika bokici da ruwa ta zauna ta saman yar kujerar bayin ta shiga saba sabulun nan à jikin dunkulalen kitson kanta, haka bakin dauda ke zuba daga kanta Yana bin magudadar ruwa, ta saba sabulun à soson ta kama darzar fatar jikinta tamkar an aikota, sai da taji zata jiwa fatarta ciwo ta daina tana ajiyar zuciya, à hankali take zuba ruwa tana lumshe idanuwanta dan ba karamin Jin dadin ruwan take ba, sosai ta tsane jikinta sannan ta saka kayan nata à cikin bokicin har hijabin nata ta wankesu tas sannan ta saka pant dinta ta zumbula sabuwar rigar tata ta saka hijabin ja ta shanya kayan à nan cikin bayin sannan ta wanke bayin tas ta fito

safiya da shigowarta kenan da kwanon abincin da mahaifinta ya bata ta kawowa Nuriyah sai ta ja ta tsaya tana mamakin kamanun Nuriyah, Iya fuskarta kadai ta gani aman abin sai ya tsoratar da ita harma taji gabanta na faduwa

Shin meye kamanun nan na nuriyah ?????? ♀*♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀*

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(7)

Nuriyah ta kasance irin masu kalar fatar nan irin yan ethiopia, hasken fatarta ba har can bane aman da mai babu mai wani irin shiga ido yake da birgewa, sannan ita dai bata da jiki KO dan Bata samu isashen hutun da zata ci ta huta bane, KO haka

yanayin jikinta yake, ita dai Sam bata da jiki sai duwaiwai idan tana tafiya KO uban hijab din da take sakawa zaka gane cewar tanada Kira mai kyau, fuskar Nuriyah yar daidai ce batada irin doguwar fuska aman lebenta tamkar zanen na yar tsana wato das da shi, dogon hanci ne da ita irin na mahaifinta sai manyan idannuwa koda yaushe yanayinsu tamkar à tsorace take, idan kuwa ta farka daga baci tamkar tayi maye haka suke à mugun lumshe, girarta à zagaye take da bakin gashin gira Wanda har yayi tamkar zai dan hade ya dan baje daga gaba ya tsuke daga karshe tamkar an aske ne an gyara ita kuwa bata taba tabata ba
Tsintsiyar hanayenta tamkar zasu karye ne basuda wani cikowa aman kafarta da dan kauri domin à tsaye take das samansu, idan kuma tana tafiya ne sai kace da gangan take juya duwaiwai ita kuwa haka halitarta take tamkar na mahaifiyarta Ouseina,

Safiya ta kawar da kanta à cikin ranta tana fadin " da haka yarinyar nan keda kyau ? Haba da ni keda kyanta da ba yanda za'ayi nayi yawo da wani hijab burumburum da nikaf, ai da irin babies din nan masu ji da kansu zan zama KO sarauniya sai dan masu fada a ji dan ubansa😏,

haka dai tana kalonta kasa kasa har ta gama komai ta gyara katifar da aka bata ta kwonta da bismillah ba tare da ta cire hijab dinta ba à saman hannunta na dama har baci yayi awon gaba da ita tana sauraron safiya na ta magana ita daya da waya

garin Allah na wayewa ta farka tun karfe biyar daidai ta fada ta kuskure bakinta ta dauro alwallah ta fito ta tada sallah, tana gamawa ta zauna tana ta hailala da salatin annabi da astagfari, tana tsaka da yi har karfe bakwai da minti ashirin ya buga wayar safiya na ta ringin aman bata motsa ba

Pagammmm taji an bude dakin kafin ta Ankara ta mike har mahaifiyar su Mubarack ta shigo hannunta dauke da kopin ruwa

Kalon Nuriyah ta tsaya yi sama da kasa ta ja tsaki ta maka mata ruwan kofin nan tace " sanu yar hutu, ai kinga bazan iya asarar ruwan da na debo bane dan haka zan fada maki ayukanki à gidan nan, na farko malan tunda asuba yake fita sai goshin magariba yake shigowa, wato ina SO Yana fita au kinyi sallah KO baki yi ba ni dai ki fito ki kama wanke wanke kiyi shara idan da wanki kiyi idan babu ba damuwa aman fa bazaki yi min girki ba kar aje ki diga min jini, Kina gamawa kuma ki fice ki tafi *Neman na kanki* domin à nan ba Wanda zai Baki KO kwandala, sannan idan soyaya kike da malan ki san cewa cikin gidan nan wly yayi miki nisa, Idan kuwa d'ana ne zai aura maki bazan taba yarda ya kwaso kwarokwaro ya hadata da yarona dan haka ki canza tunani

Safiya da hayaniyar mahaifiyarta ya tasheta daga baci tace " Umah ki hada mata harda gyaran dakin baba dan walahi ni wahalarsa nake ji shi kulun sai an gyara masa daki kafin me kuma ya bata(♀Baban ?)

habiba ta ce" ai komai, tsuntsune ya fado mana daga sama gasashe, ke maza tashi tun kafin raina ya baci

Cikin sauri Nuriyah ta mike har kafafuwanta na hardewa ta nufi tsakar gidan inda tayi mamakin yawan kwanukan, abinka da wada ya saba da wahala kan kace mai har ta gama gaba daya aikin da aka sakata tana cikin shanya kayan Mubarack ya fito ya sha kayansa na wurin aiki wato bakaken kaya irin na securiti, Yana fitowa ya zuba mata ido Yana tawasali ga Allah ubangijin talikai Wanda ya halici wannan tsararar halitar mai kyan kalo, mai sosa idanniya, mai dukan zuciya, ashe shi yasa take saka nikaf da safa dan ta san idan ta tuje toh tabas zata Hada go slow à bakin titi

Juyowar da zata yi tayi arba da shi cikin sauri ta kai kasa tana gaishe shi

Ansawa yake Yana dan murmushi irin na Wanda yaji Dadin Yanda ta girmama shi,

Habiba ce ta fito daga dakin ta watsa masu harara tace " Au zaki fara karuwancin naki ? Ban yi maki kashedi Da Yarona ba ? Toh maza tunda kin gama wankin fito ki kara gaba domin safiya tayi du mai *Neman na kansa* ya fita kasuwa

Da sauri Nuriyah ta mike ta nufi daki ta saka nikaf dinta da safarta ta kafa da hanu, ta kara gyara zaman hijabinta ta juya à nitse ta fito ta nufi fita inda kunuwanta suka kuma jiyo mata mahaifiyar mubarack na kara jadada masa KO da wasa kar ta kuma ganin suna magana da Nuriyah

Haka ta taho tana takawarta à hankalin ta nufi wajen wankin hula, tana shawo kwana wani tsoho na tsaye Yana sadakar waina manya manya da wasu masu tsaronsa du sun hade fuska Suna muzurai shi kuwa Yana sadakarsa,

Ji tayi ta dan karu da mutun haka ya saka ta juyo da sauri tana fadin kiyi hakuri sannan ta duka ta tatarowa matar jakarta da ta fadi tana dagowa daya daga cikin masu tsaron tsohon nan ya nufota ya dan fincikota Yana fadin " ke mai kike SO,? Sata ce zaki yiwa mutane ?

Da sauri tsohuwar nan ta matso ta ce" kaga jikeke ka fitar min à ido na rufe, kai KO kunya baka ji ka wani fancalar da wannan yar yarinyar ? Nifa abinnan na soja ya isheni, yau za'a je ayita ta kare tunda ni na haifi ubansa da cikin nan nawa to kuwa yau zan bashi umarnin ya rabani da wa'inan masu Kiran samudawan aman à kafirce,

Tana fada mijinta Yana kalonta Yana dan murmushi, ita dai in kaji rigimarta to da bodyguard dinsu ne, Sam bata son suna biye da ita kulun tana cikin fada idan sun fito sadaka,

À hankali take dan kakabewa Nuriyah kurar jikinta sannan ta saka waina hudu manya à leda ta mika mata tana cewa karbi nan y'ata, kiyi hakuri, ki ringa zuwa kulun nan Kina karbar sadaka Kin Ji ?

Nuriyah ta karba tana fara'a tayi godiya tana tafe tana waiwayen tsohuwar nan da tsohon nan, haka kawai taji wani irin kaunarsu à Cikin zuciyarta,

haka ta karasa yauma cikin ikon Allah ta samu huluna ta kuwa zagine ta shiga wankinta hankali kwonce, tana yi tana yar fara'arta idan ta tuna fuskar wannan matar mai cike da kamala,

ba ita ta gama ba sai wajen azahar ta Mike ta kamo hanya da kudinta tana dan murmushi, aman in ta tuna innarta sai ta share hawaye, yauma sai da ta sayi siga da alewa tayi sadaka kafin ta karasa gida

Tana shiga tayi salama, Safiya ce zaune tana cin ayaba ta dora kafa daya kan daya tana dan karkada su, Bata amsa salamar ba sai cewa tayi " ke dauko min ayaba uku ki wanke min cikin tsarabar da abana ya kawo jiya, sannan ki dauki abincin ki a can ki ci sai ki hada da kwanukan can ki wanke su tas

Nuriyah ta juya tayi abinda ta sakata sannan ta dauki shinkafar da aka zuba mata duda gaya ce ba miya ta duka ta tutura abinta ta sha ruwa tana mikewa Habiba na fitowa

Habiba ta ce" toh gantalaliya kin dawo, to kawo kudin mu gani,

Nuriyah ta jimko kudin ta dan duka tana mikawa.....*♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀*

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(8)

Baby abin ba tausayi ? My besty bata tausaya min😑 to ga page din

Nuriyah ta jimko kudin ta dan duka tana mikawa Habiba

Carab ta karbe ta irga har dubu bakwai ta dago ta watsa mata harara tace " lale yarinya ashe dai yawon naki na biyanki, to aman in ba jarabar maza ba mai zasu tsinta à nan ? Kyan dai ya rude su aman à tsayen nan tamkar sanda KO karan wasa,

Ta juya ta kali Farida da har wannan lokacin ciye ciyen ne take ta hakikance wai abinda abanta ya siyo bata ma san Nuriyah ce ta saye shi ba, ta ce" Farida zaki ci kudin haram ?

Farida ta kakaro murmushi ta ce" sosai Mama, zan ci mana, ai kiba take sakawa

Habiba tayi murmushi ta raba kudin aman maimakun tayi dubu uku da dari biyar sai tayi dubu hudu da kuma dubu uku daban, ta mikawa Nuriyah dubu uku, ta mikawa Farida dubu hudun, sannan ta hade rai tace " idan kin *Nemi na kanki* ki tabatar da kulun kin kasa gida biyu kin baiwa y'ata domin ita dai kinga bata yawon *Neman na kai* dan haka sai ki dauki hakan à matsayin kudin hayar dakinta

Nuriyah ta dan duka tace " na gode, Allah ya saka da alkhairi

À hankali ta juya ta fada dakin nasu, tana shiga yauma ta tarar an warwatsa kayanta tamkar ana neman wani abun a ciki, cikin nutsuwa ta tatare kayanta ta ninke ta mayar cikin Jakarta sannan ta fada wanka hade da dauro alwallah sannan ta wanke doguwar rigarta ta shanya kuma ta saka wa'inda ta wanke à jiya domin ta boye bakar rigar ba yanzu zata saka ba

koda dare yayi bayan sallar magariba Habiba ta shigo tace " ke tashi malan na kiranki

Nuriyah ta Mike da sauri ta fito cikin nutsuwa, tana karasowa ta duka dan nesa ta ce" Aba ina yini,

Malan isyak ya amsa mata Yana dan murmushi, can yace " ina fatan kin wuni lafiya, kin huta da ranki, kin cire yawan tunani, sannan kin ci abinci ?

carab Habiba ta cire zancen tace " hm malan ai ni yau nayi mamakin yar nan, da ta kama baci sai wajen sallar la'asar ta farka, tana farkawa ta fito tace ina abincin ta, hanu baka hanu kwarya har sai da na tausaya mata domin tana gama ci tace ina lemo, nace da ita ai sai dai ruwan tulu aman na yanyanka mata ayabar nan da ka siyo ta Ci sosai da sosai, kuma ta koma daki ta ci gaba da bacinta, nayi ta dariya ina cewa Farida ai fa ta samu yar uwa wajen baci

da Malan isyak da ita Nuriyah da Farida kanta sun zubawa Habiba ido Suna kalo,

Malan ya dan sauke ajiyar zuciya ya juyo kadan yace" Eyah ai kin san gajiya, sai à hankali zata barta, sannan ai tsarabar nan ita ta sayo maku ita jiya har ina mamakin irin hankalin yarinyar

Habiba wani haushi da kunya suka turniketa haka Farida da ta tuna yanda ta Ringa gadara da ayabar da abarbar nan Sai taji wani iri,

haka Nuriyah ta dan jima à tsugune daga bisani ta Mike tayi salama ta tafi , yau ma kamar jiya ta nemi waje ta dan rakube tayi kwonciyarta

kwonci tashi nuriyah tayi sati uku à gidan Malan isyak, fanin zamanta da su sai hamdallah domin à kulun cikin ikon Allah Ayukanta na gida karuwa suke, sannan à turata neman na kanta, tana dawowa à karbe à raba masu da Farida sannan da Malan isyak ya dawo za'a kitsa abinda ba na alkhairi ba ace tayi, Inda Allah ya taimaketa bai taba kulawa da irin zancecekun tayi tayi din ba domin sarai ya san halayar matarsa, fanin sutura alhamdulilah domin à yanzu hijabanta biyar haka ma kayan jiki masha Allah domin Malan isyak ya kara mata har kala hudu, inda Farida ta karbe biyun ta Bata tsofafin nata wa'inda ta gaji da Mora,duda haka murna take domin atanfofi ne ta wanke su ta goge abinta da dutsin guga da ta roka ta adanna suturunta

yau kam kasuwa alhamdulilah, domin yau mai huluna bai fito ba sunyi tafiya, cikin faduwar gaba ta nufi wajen yan fruits da kyar ta samu suka Bata dan yanzu kowa tsoronta yake, tana fitowa ta nufi titi sai dai kash du irin gudun da tayi da tallar da tayi cinikin naira dari biyar kawai tayi, har la'asar ta shige, ta kamo hanya da yar naira darinta ta nufo gida hankalinta à tashe domin yau ta san fa Allah kawai zai kwaceta à hannun Habiba

tana shiga ta tarar tana tsakar gida ta duka tana gaisheta, sannan hannunta na rawa ta miko mata naira darin tana cewa " yau mai hular baya nan shi yasa banyi ciniki ba sai à wajen yan fruits na samu naira dari, dan Allah kiyi hakuri mama

idannuwan Habiba tamkar su fado kasa domin kuwa yau Malan ya dawo gida da wuri sanadiyar wajen gaisuwa da suka tafi da Mubarack,

du abinda ya faru à kan kunuwansu, ya sauke ajiyar zuciya à hankali yace " mahakurci mawadaci

mubarack ya dubi yanayin mahaifin nasa cikin yannayin damuwa, tabas ya san abansa yana son taimaka yarinyar nan, à gaskiya rayuwar yarinyar ne abin à tausaya mata, ya ja nunfashi ya sauke, cikin nutsuwa yace " Aban mu

Malan isyak ya kale shi da alamun ya amsa Kiran da yayi masa

yace " Aban mu ni kuwa inada shawara à lamarin rayuwar Nuriyah, wace idan ka lamunce min zamu samu mafita à yannayin rayuwar kunci da take ciki tun kafin Umanmu ta kona kanta

Malan isyak ya ce" ina sauraronka Mubarack wace shawara ce wannan ?

shin wace shawara ce Mubarack zai gabatar wa mahaifin sa ????????????
"""""""""""?????????????????
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(9)

Yayi Jim ya ce" Aba , nasan baka ra'ayin barin y'a mace *Neman na kanta*, nasan à duniya idan akoy abinda ka ki jini shine y'a mace ta ringa bin layi layi wai da sunnan tana sana'a, kace y'a mace abin à kilace ce, Aba zan fada maka gaskiyar lamari, tunda yarinyar nan ta dawo gidan nan daidai yake da tana titin, aikin gidan nan gaba daya ita ke yinsa domin KO haki Farida bata daukewa, sannan tana gamawa KO wanka ba'a barinta tayi za'a turata *Neman na kanta*, Aba dan ma yarinyar nan mai tsoron Allah ce, ai da tuni ta kauce hanya, Kuma gagarumin abinda nake tsoro shine Aba ka dauko yarinyar nan dan ka taimaki rayuwarta kar aje ka fada halaka sanadiyar hakan, domin kuwa à cikin kangin rayuwa take kuma bazaka taba Jin maganarta ba

Malan isyak ya gyada kai ya ce" to Mubarack ai baka fada min shawarar taka ba

Mubarack ya kuma nisawa Yana tsoron fasarar da Abansa zai yiwa shawarar tasa, ya ce" Aba, wajen da nake tsaron kofa, bangaran kakanin mai gidan ne, idan Allah ya taimakeni an kusan daukan ma'aikata a kara a gidan kowani bangare, da yake Hajiya mutun ce mai mutunci mai daraja talaka sai naje na nemi alfarmar à taimaka min à dauketa fanin ban ruwan fulawowi KO taya Hajiya zama dan miko min KO kaimin wancen, sai kaga idan Allah ya taimake mu an dauketa , dan kuwa idan bakada takardar shaidar ka gama secondry basa yarda su dauki mutun aiki, aman da adu'a sai kaga Hajiyar ta dauketa

Malan isyak Yana sauraronsa Yana dan gyada kai, can yace " Aman Mubarack, wannan gida naku mai hadari ? Gidan da ba'a jimawa sai an kai maku hari ? Gidan da du yawancin mutanen ciki suka dauki talaka tamkar bawa ? Gidan da idan aka kamaka da laifi baza'a saurara maka ba sai gidan yari,? Gidan da idan ka shiga ba kai ba zuwa ganin iyayenka sai wata wata ? to ya maganar Aure idan ta shige gidan nan ? À ina zata samu miji tayi Aure ? Gidan da du rashin yarda yake sakawa koda da aurenki kika je aiki suturar da zaki saka KO dan sket da Riga KO dogon wando da Riga, masu Aure kadai keda ikon rufa dan hijabi à tsokani adinni wa'inda basuda Aure kuwa sai dai dan gyale dan karami KO yar hula à kansu ? Shin idan na dauki y'ata na kai nayiwa kaina adalci, KO na nemi yardar Allah à tare da ni ?

Mubarack ya kara gyara zamansa yace " Abanmu, ni nayi maka alkawarin à gidan nan namiji baya shiga hurumin macen da ba maharamarsa ba, da ace gefen samarin gidan ne ni kaina bazan yarda ba domin akoy marasa ji, aman aba gefen su Hajiya, kakar mai gidan mu, gefen Hajiya masu shiga wajenta daidaiku ne, kuma irin yanda take nuna min kauna ne zan je na nem alfarmar ta dauki Nuriyah à bangaranta DAn nasan zata sota domin Allah kuma ta kula da lamarinta, zancen mijin Aure kuwa ni nan da idannuwana naga yan matan da Hajiya ta aurar da kanta à gabanta domin kana samun miji cikin ikon Allah zata yi maka komai ta wanke ka à kaika gidan mijinka, Aba wly gidan nan gidan mutunci ne, kuma dalilin da yasa kake ganin mata masu aiki da irin shigar nan dan saboda baza'a zubu à yarda da masu irin shigar hijabai ba, domin irin yanda yayi suna, du duniya ta sanshi, mukamin da yake rike da shi à harkar aikinsa na soja, irin cudanyan da yake da manya da irin yanda zai kaucewa muradin du wani mugu sannan ya tsaya tsayin daka dan ganin ya hana barna yake kawo masa makiya masu neman ransa da na iyalansa, Aba sai yayi wata biyar à daji shi da kansa yake fita, hakan ya sa koda yaushe mu gidan mu da tsaro, Dan Allah Aba kayi tunani à kai, hakan yafi irin yanda take yawon *Neman na kanta* Ba'a san da mai zata hadu ba, yau duniya taki dadi idan har aka lura da ita mutane sunki gaskiya suna iya yi mata wani mugun abin, Aba idan kuwa tana zaune à gidan nan kasan dole ne Umanmu ta zata turata neman na kanta, ni fa à tunanina gwara ta kasance à can din don kuwa ba Wanda zai fitar da ita daga gidan nan sai dalili, aman à nan fa Aba sai yanda Allah yayi

Malan isyak yace" à KO'inan ma Mubarack sai yanda Allah yayi, ni dai zanyi shawara , zanyi dogon tunani sannan zan roki Allah, nan da sati zan baka abinda na yanke insha Allah

Haka Mubarack ya fito yayiwa mahaifiyarsa salama wace tunda ta galawa Nuriyah hararar maganar da tayi tayi dan tsai tana tunani hankalinta a dan tashe tana ta tunanin yanda zasu kwashe da shi

À hankali ta Mike ta shiga dakin inda ta duka ta gaishe da Malan isyak ta nufi cikin dakinsu inda tana shiga ta tarar Farida tana bincika mata kayanta.....
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

Farida na ganninta ta shiga irin basarwar nan, can kuma ta ce" ke wai ina kike ajiyar sauran kudin da idan kin Zo umanmu ke rabawa ta baki ?

Nuriyah ta dan lumshe idanuwanta alamar gajiya à tatare da ita ta ce" eyah, Aunty Farida ai bana ajiye su a gida ne

Farida ta ce" eh ai daman shi karuwa yafi uban kowa sannin zafin kudi, domin KO kudin haya wayar bayansa yake ji, shi yasa aka likewa aban mu, aka likewa gidan mu, sai yawo da nikaf wai ke ta Allah, zan fadawa umana ne yau ta karbe kudin duka ta bani yar rainin hankali,

Tana gama fada ta fice buguzum buguzum inda bata lura da mahaifinta Wanda ya labe Yana sauraron gaba daya rashin mutuncin y'arsa,

À hankali ya sauke ajiyar zuciya sannan ya kudiri niyar zai dan lafe dan yaga shin da gaske Mubarack yake, gaba daya abin nan Habiba na iya aikatawa dan mutun tamkar daba dan son zuciya irin nata ?

Haka yauma ta gama du abinda ta san aikinta ne, ta tatare tayi dan kwonciyarta zuciyarta FAL da fargabar idan malan ya fita
Sam Nuriyah bata san irin rayuwar nan ba, tabas zuna cikin talauci har talauci aman fa innarta bata taba daga mata murya ba, bale har à kai ga duka, à kulun innarta na bin ta da adu'a da nasiyah, Bata taba aibata ta KO ta shigo irin ranta a jagule dan tsokanar yara sai tayi yanda tayi ta mantar da ita damuwarta, tana sakar zuci har baci yayi awon gaba da ita,

Tunda asuba ta farka kamar kulun ta shiga aikace aikacenta, kan kace meye har ta gama, tana tsaka da kwashe sharar da tayi Farida ta fito da kulin kayan dauda ta mika mata tana cewa " ke marar gata, kama nan, jiya bayan kinyi bacin naki na hutu Kawata ta tawo kayanta da nace mata ana wankau à gidan mu, dan kinga ai à jiya baki kawo min kudina ba to a yau sai ki wanke ni kuwa na saka data da kudin

Tana gama fadin haka ta juya tayi tafiyarta inda ita kuwa ta hau wankinta, nan da nan ta gama ta fada dakin Nuriyah ta dauko su nikaf dinta da saura su ta saka abinta ta fito kenan tana sanda Habiba ta kirayi sunanta, tana isowa ta wanka mata mari,

da sauri Nuriyah ta kai kasa tana dafe kuncinta,

Habiba ta ce" ke yar gidan mai kanjamau dan ubanki SO kike ki rabani da mijina ? Idan ba bakin ciki kike yi min ba nima ya sake ni na tafi yawon gantalin irin naki mu saje karuwai biyu à titi da tsufana kike fata ba dan mai zaki wani Zo Yana zaune ki miko min wata tsinaniyar naira dari ? Sannan ma gidan ubanwa kika kai kudin nan ? Fada min ?

Nuriyah jikinta dake kyarma tace " kiyi hakuri Umah, wly ban san aba Yana gidan nan ba, kuma jiya ban Sami wankin hulunan ba, aman kiyi hakuri

Habiba ta ce" haka fa saï salo irin na yan iska, kinga ki tashi kawai kiyi maza ki tafi *Neman na kanki*, kuma sauran yauma aje malan ya dawo da wuri ki kuma bani kudin à gabansa KO ki Zo min da zancen banzar baki SAMU aiki ba, idan kuma

kostoman naki na da har sun gaji da morar ganga ne sun yar da ita ai sai ki nemi wasu dan ni dai kawai kudi na sani, kin saka Farida jiya bata ji labarin saurayinta na kasar waje ba, bace min da gani karki saka ina haikar baki har na tashe ta daga baci ranta ya baci

da sauri Nuriyah ta mike tana share hawaye ta nufi hanya inda ta fice malan isyak labe bayan kyauran kofar gidan Wanda komai ya wakana à gabansa

Tafe take tana dan layi dan kuwa kanta tamkar ya tarwatse haka take ji, shi kuwa Yana dan biye da ita à hankali suna tafiya à ransa Yana aiyana tabas idan har ana irin haka maganar Mubarack zata tabata wata rana,

Yana zaune nesa Yana kalon irin yanda take wankin hulunan nan domin à yau an Sami aiki, ya ja ajiyar zuciya ya sauke,, shi dai bai ga inda ta karya ba, haka kuma bai ga inda ta sayi abinci ba, sannan iya kalo ta karbi sadaka aman tana kule à leda bata ci ba, KO ruwa à waje baiga ta sha ba, ya farakara Jin haushin Habiba à ransa, yace " tabas Mubarack yayi gajiya à haka sai dai mu kone daga ni har Habiba da Farida, domin ni na dauko nauyi à kaina, su kuwa suna shiga haki ba dare ba rana, sannan tabas wata ranar ana iya kaucewa hanya duba da irin furucin Habiba cewar ita dai kudi ta sani ba kamar da ba, domin da ran innarta ta samo bata samo ba to fa da murnarta zata shiga gidan su dan ta san ana jiranta da fara'a, à yanzu kuwa ya Dan Girgiza kai Yana kalon lokacin da take dan shanshanya su

Wasu samari ne su biyu suka Zo ficewa dayan yace "Baba, ina gaya maka wannan babyn fa mai zafi ce, kawai mu SAMU wata rana mu afka mata

Wanda aka kiraya Da Baba ya ce" kai oga kaifa baka da kyau, yanzu à nan har ka hAngo Hutu ?

Dayan yayi dariya ya ce" kai na rabaka da eh yane, karka yi mamakin Jin ka fada à kogi tanjam sannan kaji an rike maka wuta, kai Allah baba mu shirya mata dan da gani babyn nan zata rike wuta

À daidai nan malan isyak ya juyo ya barsu suka ci gaba da tsara yanda zasu cima Nuriyah

Sauri saurasauri Ya rigayeta karasowa gida inda Yana shiga ya nemi dan guri ya labe Yana jiran gannin karshen ranar nan

Tana shigowa ta karasa ta duka tana gaishe su, ba Wanda ya amsa mata Habiba ta mika hanu ta karbe kudin ta irge yau har dubu takwass, ta ce" yau KO kwondala bazan baki ba, dan kuwa harda na jiya, dan haka bace min da gani kin wani yi tsuguno kamar ta Allah

Da saurinta ta mike ta fada daki, inda malan yaji Dan Danshi danshi à fuskarsa, Yana lalubawa yaji hawaye ne, yayi saurin gogewa

Haka malan yaci gaba da labewa à kulun ta Allah Yana kalon irin yanda nuriyah ke gannin taskun rayuwa à gidan sa, wani abin tausayin ma sai irin yanda zata je har wajen gidansu inda ake tada gini tayi ta share hawaye sannan ta biyo ta wajen makabarta tayi ta adu'a har tana dan lekawa kamar tana son ganin wani, sannan ta karkato ta koma gida ta tarar da taskun Habiba da Farida, kuma masu biyar bayanta

Basu daina ba, suma suna hakon ranar da zasu kai gareta à kulun cikin taretsare Tsare suke

À yau dai Mubarack ya dawo gida da fara'ar sa, domin ya samu tsohuwa tace ya kawo kanwar tasa idan tanada nutsuwa zata dauketa à bangarenta, zuwa wannan lokacin damuwarsa aba ne kawai ina rokon Allah, Allah ya sa ya yarjewaYarjewa kudirinsa,

Zaune malan isyak yake bayan ya dawo daga masalaci salar isha'i, Yana kalon kwanon abincin da aka zuba masa aman ya kasa ci,

Mubarack yayi salama ya duka yana gaishe da shi

Bayan ya gama ansawa yayi dan jim

Malan isyak yace " daman ina nemanka, bisa shawarar da nace maka zanyi, toh na yanke shawarar.....

♀♀♀♀♀♀♀♀
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(11)

Basa comment😑

Malan isyak ya ce" daman ina nemanka, bisa shawarar da nace maka zanyi, to na yanke shawarar bayan dogon nazari, eh lale fa yarinyar nan à sama mata wajen da zata kasance cikin kwonciyar hankali, aman sai kayi min alkawaririka da dama

Mubarack yayi murmushi yace" Aba , KO wani alkawari kake SO insha Allah zan yi maka kuma da yardar Allah zan kiyaye

Malan isyak ya ce" da farko dai ka kula da lamarin yarinyar nan, duda ni zan rakata da kaina sannan da sunana za'a rubuta ta à wannan gida, aman ina SO yanda zaka kula da abinda kanwarka ke ciki itama haka,

Na biyu ina son du ranar da kake aiki ka bugo min waya mu gaisa da ita,

Mubarack na SO ace ka SO yarinyar nan na aura maka ita, sai dai kash yanzu duniya ta canza, ba kai nake ji ba, aa, ita yarinyar kar tauye hakin yayi yawa, aman insha Allah da safe zan dauketa mu tafi tare

Mubarack ya ce" Aban mu, nayi alkawarin zan kula da lamarin Nuriyah mudin raina na gangar jikina

Malan isyak yayi murmushi ya ce " Allah yayi maka albarka

Garin Allah na wayewa bayan ta gama sallah ta fito da niyar fara aikace aikacen ta, tana fitowa abin mamaki sai ta ga abansu zaune da farar jalabiyarsa har kasa ya dora dan mayafin nan da limamai ke dorawa a saman kansu,

har kasa ta duka tana gaishe shi, inda cikin sakin fuska yake amsa mata,

Nuriyah, karki fara aikin nan, ki je kiyi wanka ki canza kayanki ki fito mu tafi kinga sauko ake yi fa " cewar Malan isyak Yana kalonta

Ba tare da ta tambaye shi inda zasu ba, ta mike ta je tayi yanda ya ce, ta saka doguwar abayarta baka ta dora hijab dinta fari kar ta dauko nikaf dinta ta saka silifas dinta Ta fito zuciyarta cike da tunani kala kala, na inda zasu tafi, sannan da muguwar fargabar yanda zasu kwashe da Habiba

Tana fitowa ta tarar da Habiba ma ta farka tana zaune sai iya yi take yiwa mijinta,

Habiba ta dago tana kalonta cike da mamakin wanka ne tayi da safiyar nan, ina zata je,

Bata gama tunaninta ba taji Aba na cewa " yawa bismillah mu je

Habiba ta ce" Malan ban gane ba ku je, ina zaku tafin ?

à hankali malan isyak ya juyo ya ce" zamu je na kaita *Neman na kanta* ne, kinsan gwara ta kara kaimi KO ta ringa kawo maki ? Nairori Kina rabawa Kina bawa Farida tana saka Kati dan ta ji labarin saurayinta na kasar waje

Yana gama fadar haka ya bi bayan Nuriyah da ta dade da fita ya bar Habiba tsaye cike da fargabar daman ya san abinda yake faruwa ?

Tafe suke à cikin Adaidaita sahu, inda Mubarack ya zauna à gidan gaba, malan isyak Yana gidan baya zaune da Nuriyah, a tsakaninsu za'a iya saka wani mutun din, cikin nutsuwa Aba ya ce" Nuriyah

ta dan juyo tana kalonsa

ya ce" shin kin yarda da ni ? Kin yarda bazan yarda wani abin ya cuce ki ba ?

Nuriyah ta gyada kai

ya ce " alhamdulilah, wato nuriyah na san du abinda kike ciki, ina sane da irin kangin rayuwar da kike ciki nan da sati guda na gani da idannuwana, ina mai baki hakuri, ina rokonki da ki yafe mana

da sauri Nuriyah ta ce" Aba ba komai, ni ban taba rike kowa ba Aba

malan isyak yayi murmushi ya ce" masha Allah, Nuriyah, zamu je ne na kaiki gidan da Mubarack yake aiki, nan da yan kwanaki da suka shige Mubarack ya Zo min da shawarar na..... ..... Nan ya kwashe du yanda suka yi, da yanda ya ringa bin bayanta, da yanda su baba suke magana à kanta, da komai da komai, har zuwa shawarar da ya yanke na hakan shine kwonciyar hankalinta

kwarai nuriyah tayi amana da hakan, duda bata san mai zata kuma tarar ba, aman ta sani bazata kuma fita yawon aiki ba, sannan ai shima wannan din *Neman na kanta* ne, hakan ya sa ta nunawa malan isyak amincewarta harma ta amsa da amin daidai lokacin da suka yi adu'ar Allah ya sa a dace su dauketa

tafiya ta fi ta awa abinka da go slow ga nisa,

wasu irin shukoki ne suka fara shigowa irin maina manya manyan nan sunyi runfa , wata iska mai dadin sanyi ne ta fara buso su, abin mainan nan ya dan lulube wajen sai ba'a gannin hasken ranar da ta kyanlare garin , daidai wata igiya da wani soja à tsaye ya tsaya Yana cewa to daga nan bama iya tsanlaka gidan kan giwa

à nan suka sauka suka bashi dubu biyu da dari takwas wai dan ma na gida ne

tun daga bakin wannan igiyar Nuriyah ta saki baki tana mamakin irin wannan tsaro, duda Mubarack ma'aikacin gidan ne aman du inda ya Zo sai ya tsaya an caje su ya nuna takardar da Hajiya tayi sinye ta buga tambarin kan giwa sannan su samu hucewa, sannan à tsakanin wata kofar zuwa wata akoy soja biyar kowane tsaye da bindigar sa a dane Yana jiran ta ware KO ta walare,

suna zuwa get na uku aka ce ai dole sai ta cire nikaf dinta da safarta na hanu da kafa,
ba yanda ta iya domin ita wani irin tsoron su take tunba idannuwansu ba, kowane yayi ja gashi hausar kirki ma basuda ita, hakan ya sa kafin ya rufe bakinsa har ta ja ta cicire ta mika masa, sannan suka shige

Wata bakar mota ce mai shegen kyau ta daukesu da alama idan ka ISO nan wannan motar ke dauka ta karasa da kai can cikin palas kan giwa,

A cikin motarnan ba mai gannin kofa, wato dai baka iya ganin abinda ake à kofar sai mai tukin kadai shima dan ya saka gilas ne Wanda zai haskaka masa bakin madubin motar,

Wasa wasa gurugudu Yake aman sai da suka shafe minti ashirin sannan ya ja ya tsaya inda ya ce " Aboki, kafa caba hajiya Na Yinka

Mubarack yayi murmushi Yana cewa " sai na sako akoy magana, sannan ya rufe ya tardo abansa da Nuriyah da suka yi Shatata Da baki suna kalon wannan ikon Allah,

Mubarack na karasowa kafin yayi magana malan isyak ya ce" Mubarack yanzu wannan abin idan muka hau bazai fashe mu fada ciki ba ? , sannan ina kofar shiga ? Mubarack kaina juyawa yake yanzu da mutane à ciki ? Mubarack wa'innan maduban basa tsoro su tarwatse su rufun musu ? Shin Mubarack sun san kuwa ana mutuwa ?

Da sauri Mubarack ya tare mahaifinsa ya ce" Abana daukakar kenan, da jama'a à ciki, iya nan ne mai madubin mai yawa haka dan bangaren hajiya farar kasa ce mai kyan gaske sai shukoki, mu je Abana ba abinda zai samemu insha Allah

haka suka dunguma itama sai sauri take domin matukar tsorata to a tsorace take, idanuwanta sun kasa tsayuwa sai juya kwayar cikin take cikin firgici da tsoron fa anya har yanzu suna cikin duniya ???

Suna shigowa wajen daukan yan aikin suka tarar yan mata, mata, samari, da kuma manyan mazan, kowa ya ci kwaliya ya hakimce harda nasaru sun sha kananun kaya wai sun Zo neman aikin aikatau à gidan kan giwa,

À hankali ya mika takardar aka mikawa wata mata dake hakimce, ita ce mai alhakin kulawa da daukan masu aiki, sai à wannan lokacin Nuriyah ta hango wasu matan zazune daga can sama, da wani gilas fari à tsakiya Wanda ya kare su,

Murmushi ne ya subuce mata lokacin da ta hango tsohuwa mai sadakar waina ta hanyar yan wankin hula, wani mamaki kuma ya dirar mata à lokacin da wannan matar da aka mikawa takarda ta Dago ta ce" *Nuriyah malan isyak*

Nuriyah tayi saurin mikewa tana amsawa da na'am

À tare suka juyo suna kalonta, inda wannan matar ta ce" no, bazai yiwu ba, yarinyar nan ba karatun shukoki tayi ba, ba karatun girki tayi ba, ba wani digiri KO shaidar tayi karatu gareta ba, Hajiya kiyi Hakuri aman kan giwa yayi gargadin kar mu saki mu dauki irin hakan,

Daga saman nan sai muryar wannan mata tayi salama, ta ce" ke, inada tambaya, nace wai inada tambaya, da ban haiho Karibullah ba, da zai haifo kan giwa ? To dan ubansa ni nan ni nace à daukan min yarinyar nan, ni na yarda da ita,

Wace take da hakin zabar ma'aikatan gidan ta dan juyo gaban computer ta, wace da alama mutun ne ke sauraronsu kuma yana ganin komai, ta ce" Oga kan giwa, yau ga abinda da Hajiya ta dora

Kasa kasa kake Jin kamar Yana waya, can yace" to dad, za'a daukar mata, ba shikenan rigimar ba? ,

Can ya ajiye ya ce" ki dauketa daga ita kar à kuma daukan KO wacece indai ba shaidar takardu, ita kuwa Allah ya shiryeta

Daga saman ta ce" Allah ya shiryi ubanka dai, wato na ma zare KO ? Ba komai, yarinya kuma à daukan min ita ban ce a rubuta mata takamaimai aikin da zata yi ba, ni nan zan bata aiki

Daga cikin computer ake cewa " idan idan ka kuma yiwa mamaana magana zan saba maka, haba ka barta mana

Yayi saurin kashe camera dan kar su ji abinda zai fada

Nuriyah aka ja zuwa dakin hoto,inda akayi mata na carte aka lika à kusan sunanta wace zata Bata damar shiga KO'ina à cikin gidan à matsayinta na ma'aikaciyar gidan, nan da nan aka bata wasu suturu à cikin wata jaka wace ake ja à kasa da kuma ky na dakinta Wanda yake à bangaren su Hajiya,

Tana ji tana gani tayiwa su Malan isyak salama harda hawayenta domin kwarai ta tsorata da irin wannan daula, KO Yaya zata rayu à wannan gida ?

Shin waye kan giwa ????, ya rayuwar Nuriyah zata kasance à gidan kan giwa ?????????? ♀♀♀
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(12)

A hankali take takawa tana biye da Mubarack Wanda yayi mata jagora dan ya nuna mata gefen Hajiya,

Wani get din suka kuma shiga, Wanda suna shiga wani sanyin dadi ya kuma ratsa su, à hankali Nuriyah ta lumshe idanuwanta daidai lokacin da kafafuwanta suke nutsewa cikin farar kasar balbalin gidan, abubuwan kiwo suka fara daukar hankalinta domin daga gefe du tsuntsaye ne masu kyau sannan manya manya, harda su dawisu du sai dan zagaye suke a balbalin gidansu a wadace,

Tana ta waige daidai inda suka karaso wajen shukoki na fulawowi, sai wata uwar mangwaro wace tayi babar runfa, sai yar runfa irin ta gargajiya anyita ta dan zubo gwanin ban sha'awa, ni'imar wajen kadai ta Isa ta saka bawa cikin nutsuwa,

À wannan lokacin Hajiya tsohuwa da Elhaj tsoho suna saman mamakekiyar terass dinsu wace suke zama da safe har zuwa lokacin bacin su yayi su koma ciki, sai kuma fitowar yama

À hankali suka taka yar matatakalar da sai an hayeta ake hawa filin, suna hawa Mubarack yayi salama inda itama nuriyar tayi salamar

à tare suka juyo suna ansawa inda Elhaj tsoho ya ce" Dan gidan hajiya, kanwar taka ce ba ??

Mubarack ya dan duka alamar girmamawa ya ce" eh Aba ita ce

hannu hajiya tsohuwa ta mikawa Nuriyah tana cewa kinga Zo nan y'a ta, ki je kiyi wanka ga dakin ki can ki kwonta ki huta, za'a kawo maki abinci, zuwa gobe insha Allah sai na fada maki dan abinda zakina yi kin ji ?

Nuriyah ta gyada kanta tana farin cikin kasancewarta à karkashin innuwar hajiya, domin Sam bata da kyankyanin talaka

Cikin nutsuwa ta nufi dakin da aka yi mata nuni, ta bude da ky din nan ta shiga da adu'a sannan da salama à bakinta,

Sai da gabanta ya wani fadi dalilin tsaruwar dakin, gado ne à jikin katangar sai sip, Da coiffeuse mai madubi à hade wada kana iya gannin kanka à ciki Gaba dayanka, gefe dama na gadon kur'anai ne da litatafan musulunci, gefen hagu kuwa bible ne sai kuma yar sarka irin ta christocin nan mai +,

à hankali ta taka ta karasa shiga, daman ba abinda ta dauko daga gida hakan ya sa bata da komai a nan, cikin nutsuwa ta dan zauna à kasa tana kalon dakin tana tawasali ga Allah da ya bata wannan kyauta,

ta kusan shafe minti ashirin, Kiran sallar la'asar ta fargar da ita, masalacin tamkar à kofar dakinta, cikin azama ta Mike ta fada bayin inda nan ma ta tsaya kalon tsaruwar sa, à hankali ta ce" Gaskiyar Aba da ya ce, shin sun kuwa san ana mutuwa ? Nan wai dakin yan aiki to ina da nasu ? , à hankali ta lumshe idanuwanta ta ce" ya Allah, ka sa wannan dukiyar halal ce, ya Allah kar ka bani ikon cin haram à cikina,

Wanka ta tsala da sabulun dake bayin da sabon soso, sannan ta bude sabon brosh ta kama darzar hakoranta har sai da taji su fara zafi ta Bari, ta dauro alwallah ta mayar da abayarta ta fito ta tada sallah,

Tana gama salolinta ta kama karatun alkour'ani inda kwarai nayi mamakin daman haka take da karatu à kanta ?

A ranar nan tayi ibada har ta more, rabonta da irin wannan ibadar har ta manta, sosai ta roki Allah subahanahu wata'ala kan lamuranta, haka innarta ,

Bayan sallar isha'i aka kawo mata abinci kaya guda inda ta tankwashe kafafuwanta ta kwashi abincinta hankali kwonce tayi hamdallah, tana faman tashi aka kuma bugawa, ta bada izini aka shigo

Wani farin fata ne, wato nasara ya tsaya ya ce" hi

Nuriyah ta dago ta danyi murmushi, ya matso cikin turanci ya ce" ni ke kula da ganin idan kowa ya ci abinci, sannan na fadawa kowa kayan da zai saka domin kowace rana da kayan da ake sakawa na masu aiki à gidan nan

Nuriyah ta dan fahimci inda ya dosa, domin bokon nata ba har can bace, hakan ya sa ta bishi da kalo inda ya nufi sif din nan ya ja ya bude,

Idannuwa ta waro, tana mamaki, kenan na dazu da aka bata na ranar nan ne wato talata,

Jawo wasu bakar siket da jar Riga ya mika mata, ya ce" wa'innan sune na laraba, sai takalma kafa ciki, sai kuma wannan dan kwalin shi zaki Yana, ki kula banda kazanta, sannan gashin kanki ki tabatar da kin tsefe idan à kitse yake ki wanke ki daure, ina fatan kin fahimta ?

Nuriyah ta gyada kanta tana mamakin irin tsare tsaren gidan nan, wannan KO dai gidan shugaban kasa aka kawota ???

Bata kwonce kan nata ba, tayi kwonciyarta nan saman abin sallarta, ta gyara tayi adu'a ta dukunkuna da hijabinta, carbin da ta tarar à nan à hannunta tana ja har baci yayi awon gaba da ita

kamar yanda ta saba farkawa tun karfe biyar, haka ta farka, yauma ta fada bayin tayi wanka iya yinta ta fito tayi sallah, ta ja carbinta, sannan ta Mike ta dauko kayan nan, ta daga sket din tayi tayi ta shigeta aman ina wajen duwaiwanta taki shiga ga shegen kwari,
Zama tayi ta dafe goshinta domin bata san ya zata yi ba, sket din irin na ramamun nan ne, shi kuwa bai gane yannayin jikinta ba dan à lulube take sai kawai yayi aiki da ramar kafadunta ya ciro mata

Kuma mikewa tayi tana kokowa da sket din, sai ji Tayi An shigo Da salama

Idanuwanta ta zaro zata fada bayan gadon dan ta labe jikinta tana dan sakin kara na firgitar tarar da ita à hakan da aka yi.....

Shin wanene ya shigo ????? ♀
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(13)

Hajiya Murjanatu ce, wato Hajiya tsohuwa ta shigo tare da wani saurayi fari kar tamkar dan larabawa,

Da sauri ya juya Yana kalon kofa inda Hajiyar tayi saurin nufarta tana cewa" Ya rab, Nuriyah kiyi à hankali mana karki jiwa kanki ciwo plz

Kamota tayi kunya kamar zata nitse cikin kasa tana ta sine kai

Hajiya ta duba cikin sif din ta dauko wani sket din Wanda yafi wancen girma ta mika mata tana cewa saka wannan tabas zaiyi

Nuriyah ta karba ta saka ta gyara rigarta tana dan kara jan ta dan ta kara sauka kasa sai dai ina bakin tsayinta kenan

Hajiya ta ce " tashi mu tafi na nuna maki yanda zaki jera min waina à cikin Baban roba dan na tafi kar rana tayi

Tana fadi ne tana tafiya gaba da wannan saurayi Wanda tayi Kira da Rislan

Falon hajiya suka shiga Wanda ya kawatu da irin adon mutanen da, wato dai harda su wata kwarya ta sha Zane abin sha'awa,

hajiya ta juyo ta ce" Nuriyah ki shiga ki ce su baki kayan aikin

Nuriyah ta juya ta shiga kofar da aka nuna mata, Inda Rislan ya rakata da kalo, ya juyo ya ce" waouh, Hajiya, à ina kika hadu da Yar ethiopia ? Sannan ta iya hausa ?

hajiya tayi murmushi ta ce " ba yar ethiopia bace, inajin dai ta cakulu da filani baka ganin yanayin tsarin fuskarta, ni abinda yake bani sha'awa da ita nutsuwarta, shiru shirun nan Bata yankawa kowa ba bare ace tayi

Rislan har zaiyi magana sai gata ta kuma fitowa da katon tarmous ta shiga zuba wainar da aka toya take ta kanshi, à haka har ta gama ta rurufe, Hajiya sai sannu take jero mata, can ta fito ta ce" Yawa Nuriyah, ki tabatar kin tsefe kanki kafin na dawo dan à gyara maki gashin nan naga kitson har ya bace

da sauri Rislan ya ce" na rakata wajen momy saloon tayi mata irin na auta ta gyara mata kan da kyau

Hajiya tayi murmushi tace " Dan nema, y'ata dai sai dai hangen nesa
Du Wanda ya nemi ya shiga lamarinta zan hada shi da kan giwa,

Rislan ya ce" kai wannan tsohuwar to shi Yaya kan giwan ma ai ya nemi Aure kuma ya samu Yana zaune da su dan haka kinga ba zai hanani raya sunna ba

Hajiya tayi kwafa ta kawar da kanta tana Jin haushin bodyguard din da suka shiga dayar motar dan su rakata, domin à yau Elhaj Yana busy tare da kangiwa da kuma mahaifinsa Karibullah

su Wanene family *KAN GIWA*?

KAN GIWA kiranyan da yan ta'ada suka yiwa Ibrahim Karibullah Ibrahim,

Ibrahim karibullah Ibrahim ya kasance D'à na uku sannan Wanda ya rayu kafin kannansa uku da suka biyo baya Yaya à wajen Karibullah da Sedina

Karibullah ya kasance hamshakin mai kudi, wato ya riki matsayin ministan kudi a Japon inda ya hadu da matarsa yar gidan Elhaj sulaimankhan menistan éducation na kasar indiya,
Sedina ta kasance ba'indiya shi kuwa Karibullah bafulatanin usul,
sosai Karibullah ya sha fama kafin mahaifin Sedina da mahaifiyarta su yarda su hada su aure bayan rigingimu da tashin hankali aka yanka masa sadaki ya biya ba tare da dar ba domin kuwa shi SO yake domin Allah,
bayan auren Sedina da Karibullah, ta samu ciki har sau uku Yana zubewa, à na hudun ne Allah ya bata d'à namiji Wanda aka saka masa sannan *Ibrahim* wato ya ci sannan mahaifin Karibullah,
Sedina ita kadai mahaifinta suka malaka, ta je wanka gida wani dare tana shayar da yaronta sai mahaifinta ya shiga bayi dan yayi wanka, abinka da ajali bayan ya cika bahon wankan da ruwa irin Wanda yake aiki da wutar lantarkin nan ashe ya manta bai rufe wajen jona ruwan ya zama na zafi ba, Yana saka kafarsa ta kama shi,
Cikin firgici ya saki inalilahi wa'ina ilaihi raj'une, hakan da mahaifiyar Sedina ta ji ya saka ta fada bayin da gudu dan ganin abinda ke damun mijinta, tana shiga itama ta kama shi da niyar ta warto shi sai gawarsu aka tarar

sosai Sedina ta shiga tashin hankali, inda Hajiya Murjanatu da Elhaj Ibrahim Da Elhaj karibullah suka tare gaba daya à gidan su Sedina dan tayata jimamin rashin iyayenta da tayi

Wata rana suna zaune, jujun mahaifinta ya Zo da takardun du abinda ya malaka wa'inda du sunnayenta ne à jiki, da kuma irin dukiyar da ya tara à cikin acount dinsa na banki ya kawo shaidar komai ya baiwa Sedina, Inda baiwar Allah ta tatara komai ta mikawa mijinta tana share hawaye ta ce" Banida kowa sai kai, ka haneni aikin gwomnati domin ka tsaya à lamarina, ba abinda na nema na rasa à nan gidan duniya, wannan arziki bansan ya zanyi da shi ba, kamar yanda na baka ragamar rayuwana haka na damka maka na dukiyar mu, à mayar da komai da sunnan mai sunan Aba kafin ya girma, koda na kuma haihuwar wasun na san zaka kula dan ganin kansu ya hadu

sosai Hajiya Murjanatu take zubar da hawaye tana kara rarashin Sedina

tundaga wannan rana hajiya murjanatu take kula da lamarin Sedina koda ciwon kai take tana tsaye sai taga ta warke hankalinta yake kwonci

Bayan shekaru goma sha bakwai da haihuwar Ibrahim Kan giwa Sedina ta kuma haihuwar Yaya uku, Inda ta samu Sulaimankhan, ta samu Rislan, sai yar auta wace aka saka Mata Murjannatu sannan mahaifiyar Karibullah,
À daidai wannan lokacin arzikin karibullah ya kara habaka duba da irin yanda kasuwancin yafi karbarsa sai kawai ya ajiye aikin gomnatin ya tatara iyalansa suka juyo gida Nigeria inda aka baro Ibrahim kan giwa à makarantar sojoji wace tun yanada shekara bakwai yake can

Sedina na rainon yayanta cikin ingantaciyar tarbiya, domin du irin arzikin su Bata taba yarda da sangarta su ba duda tana iya yinta dan ganin tarbiyar UmI (Murjannutu) Bata lalace ba, dan kuwa nuna mata Soyaya Suke Fiye da tunaninta,

Shekarar Ibrahim Ashirin Da biyar A makarantar sojoji ta kasar Japon, inda aka yaye su cikin ikon Allah Karibullah ya samu hanya aka kawo Ibrahim Nigeria dan ya kama aiki

Zuwan Ibrahim baifi wata ba miyagun mutane suka yi masa sunan kan GIWA, dalilin irin yanda suke shan fama da shi, à zuwansa ya rufe manya mayan masu fada à ji da suke taka doka à Nigeria sannan Banban palas kan giwa suka ginata à kano inda babu ne kawai babu,

Matan Ibrahim kan giwa biyu, da Ba'indiya mai suna *NAdiya* sai yar Ibo mai suna *Djamila*

Ibrahim ya kasance irin mazan da ake Kira kerare, wato Ibrahim à tsaye yake sandan, dogo ne har can kakarfa, aikin soja ya saka farinsa ya dan disashe aman du da haka farine mai dan duhu, jikin Ibrahim tun daga kan kirjinsa har kwabrin kafarsa wani irin sanka sanka irin na maza masu Cin karfen nan aman shi hakan bai sa ya gajarce ba sai ma kara tsayuwa da yayi
Idannuwan Ibrahim basuda irin girman nan, tsaka Tsaki Ne KO don lumshe su da yake ne sai ka rantse cikinsu babu fari wato si kwayar idannuwan nan tamkar jajaye ne aka yi masa sai bakin dake tsakiya
Kamanun Ibrahim sun sha banban da na yan uwansa dan kuwa su yan hutu ne shi kuwa Dan filin daga ne

Sosai mata suke ra'ayin kasancewa da Ibrahim koda à dare daya ne, inda Ibrahim du yanda yakeda mata biyu aman yanada bin mata dan Allah yayi masa halitar sha'awa à tare da shi sannan matansa kowace bata iya masa dan su hutu kawai suka iya, shi suka sani hakan ya sa yakeda budurwa banasaria wace kowa ya san shi da ita aman ya kasa aurenta kasancewarta ba musulma ba kuma batada ra'ayin musulunci

Ibrahim *Kan giwa* baya Daukan raini hakan kuwa KO kai wanene, mace daya ke tsaya ta Luka masa zaki yayi dan murmushi ya kada kai sai Hajiya Murja wace yake sonta tamkar ransa,

Bayan shekara guda da yan watanni Allah ya karbi ran Sedina inda wannan family ta shiga rudani da tashin hankali tunba Mujannatu da Karibullah ba dan kuwa sun jima kafin à samo kansu

Bayan rasuwarta sai hajiya murjanatu ta zagine dan ganin rayuwar yan jikokinta ta inganta cikin ikon Allah bayan rasuwar da shekara biyar karibullah yayi Aure inda ya auri wata Yar gidan amininsa mai sunna Hasana Inda jininsu ya hadu da Murjannatu take kula da yayansa cikin kauna da zuciya daya

Haka rayuwana gidan *Kan Giwa* ta kasance Yana cikin gidan aman sai ayi wata ba'a ganshi ba dan kofar boye gareshi ta caméra yake kalon kowa sai yar kakarsa da idan ya sha kwana zai tarda ita KO ita idan tayi missing dinsa zata wanke kafa ta tarda shi gefensa tayi ta mita...

Ci gaban labari
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(14)

A hankali ta kai zaune saman kujerar coiffeuse din dakin da take kwana, tana zama ta dauko tisubala ta konce daurin dan kwalin dake kanta, da kyar take tsifar kan nata domin kitson har ya bace sosai à cikin juna,

À hankali take dan shafa jelar kitson tana tuno ranar da innarta tayi mata shi Inda take cewa Inna ki daina kitsewa har tsinnin kinga fa kafin na kunce shi na kan sha fama,
Sai innarta tayi murmushi tace " Nuriyah kitson naki duka hudu ne, ni ga tsufa bana iya yi miki fiye da hakan ke kuwa kin nace da bazaki je wajen lami tayi maki ba, shi kuwa gashin nan naki masha Allah idan ban kitse har tsinin ba bakya gannin santsinsa bazai jima ba zai warware da kansa

Murmushi ne ya subuce mata à hankali ta furta "Innata

Firgigit ta zabura cike da tsoro tana kalon wayar dake mane da bango sai ruri take tana neman agaji har wata yar jar wuta na dan haskawa tana daukewa,

Tsayuwa tayi jikinta na kyarma ta kasa daga wayar dan ita bata ma san da ita à dakin ba, tun tana yi har tayi shiru da alamar ta tsinke

Ajiyar zuciya take kokarin saki Inda ta kuma daukan wata tsuwar, ai Bata san sanda ta mika hannu ta daga jikinta na Bari tayi tsai tana sauraron lokacin da aka ce"Nuriyah ki Zo na dawo

tamkar an farkar da ita daga baci ta ce" Toh Hajiya,

sai taji dif alamun an kashe, tayi tsai tana mamakin kenan da gaske ne, wata rana sabiu ya taba nuna mata wata wakar indiya da taga à ciki akoy irin wannan wayar ashe da gaske kana iya jiyo muryar mutun, ta sauke ajiyar zuciya tana mamakin Hajiya, nan da nan sai anyi Kiran mutun à waya ? Wata zuciyar ta ce mata kin manta ba unguwar yawa gidan laka kike ba, su à nan wannan ai ba wani abin bane, ta kuma sauke ajiyar zuciya tana kalon madubin dakin à fili ta furta " à gaskiya bazan jima ina irin wannan shigar ba, dan kuwa ni musulma ce, sannan ban Zo nan dan na cutar da su ba

tana wannan maganar tana dan tafiya ne cikin nutsuwa Inda ta cunkushe gashin nata dake dan bugawar warin ruwa

Tana karasowa ta duka kasa tana gaishe su

Hajiya ta amsa da fara'arta sannan cikin yaren turanci ta ce" Emy, ki kaita a gyara mata kanta, da kuma faratunan ta, ina SO ta ringa yin irin aikin gida, koda baki akayi ta basu ruwa da komai

wace akayi Kira da Emy da alamar Christa ce ta amsa da" to, sannan tayi gaba Nuriyah na biye da ita à baya

Suna juya baya Rislan ya bita da ido yanai mata kalon kurullah, à hankali ya juyo ya ce" gaskiya à bar tunanin saka min mata aiki, raina Yana iya baci

Hajiya Murjannatu ta kama baki tayi salati ta ce" gidanku, nace gidanku Rislanu, toh dan ubanka baka Isa ba, bazan baka ita din ba, dan haka ka fitar min à ido na rufe dan nema

rislan ya ce" idan ita ta zabeni ai sai ki hanna, dan kinga ina wanni lalabaki, to saï ta soni

Hajiya Murjannatu ta rike baki ta ce" to da Ubanka kake, KO dan Ubanka ka saki ka rabin min yarinya na hadaka da mai tataka ka à gidan nan ai kafi kowa sannin halayensa

Rislan ya rage murya kasa kasa ya ce" ni fa ba lalata na nema ba, maganar Aure nake, kuma shima yayan ai yanzu ya san na girma bazai min irin na da ba, waima ke da kike kalonsa da budurwa wace ba musulma ba, ba kuma ra'ayin Aure yake ransu ba aman sai ki dage à kan dan alhaki, to Nuriyah sai ta SO ni

Yana gama fadar haka ya mike yayi gaba abinsa Inda ya bar yar kakarsa cikin tashin hankali, *Kan giwa* mutun ne har mutun sai dai ta rasa ya zata yi ta raba shi da wannan yarinyar, ta rasa wata masifa yake tsinta à wajenta bayan ga mata zuka

zuka à tare da shi, ta rasa gane kansa, wannan abin na daga mata hankali, shin mai zasu cewa ubangiji na sake da amanar da suka yi, suna yi iya yinsu aman abin yaci tura, ban ban abin haushin ma matansa Sam basu damu ba, KO mai hakan ke nufi ?

A hankali ta sauke ajiyar zuciya, ta lalubo wayarta ta dannawa *Kan Giwa* kira

Sai da tayi Kira ya kai sau biyar sannan ya daga muryarsa tamkar ya tashi daga baci ya ce" Ya akayi ?

Hajiya ta share hawayenta muryarta na rawa yanda da ka ji zaka fahimci à cikin tashin hankali take ta ce" Ibrahim

Da sauri *Kan giwa*, ya ture hannun Isabel ya mike tsaye ya ce" mai ke faruwa Hajiya ?

Yana maganar ne Yana kokarin kuna computersa ya dano bangaren Hajiya Murjannatu Inda ya hangota zaune tana dan share hawaye cikin sauri ya ce" kukan mai kike ? Wa ya mutu ? Mai kike SO ? Wa ya taba ki ? □□

Hajiya murja ta ce" Ba komai, ina son karshen satin nan kaci abincin dare à gefena da kai da iyalinka

Jikin Ibrahim ya mutu murus ya ce" bakya Jin dadin jikinki ne ? Mai yake damunki ? Wani abin kike SO ?

Hajiya zuwa wannan lokacin ranta ya kara jagulewa ta Mike ta nufi daidai camerar dake haska masa su dan ta san tabas Yana kalonta ta dago kanta ta watsa harara sannan ta ce" Laifi ne dan na bukaci ranar asabar ku halarci gidana da kai da iyalinka baki daya ? Na'am ? Tana gama fadin haka dif ta kashe ta fada falonta ta nufi dakinta dan ta samu nutsuwar zuciyarta

Ajiyar zuciya ya sauke Inda ya lumshe idannuwansa Yana Jin yanda Isabel ke shafar kirjinsa, du masifarsa kawai sai ya kasa biye mata harma ya dakatar da ita ya fada bayinsa yana tunanin abinda ya dagula lisafin hajiyarsa

Nan da nan Ya kara shiga wanni yanayin damuwa du ya juye Yana ta tunanin wannan lamari

Bayan kwana biyu Da sasafe ta gama shiryawarta tana gama saka rigarta Kiran Hajiya ya shigo à wayar dakin Inda take ce mata ta duba cikin sif din nan gefen dama akoy irin dogayen riguna ta saka guda dan yau juma'ace su je tare harda elhaj

Murmushi tayi lokacin da take karbar wannan sako ta ce" to

Harda dan tsalenta da ta buda gefen kayan hausa ba na aiki ba, Inda ta shiga ruwa ido tana ta jera adu'o'i tana mamakin kayan nan, à hankali ta dauko wata doguwar bakar Riga , tana zazage Linkin da ta sha dogon farin wando da yar Riga kamar shimi suka fado daga ciki, à hankali ta furta masha Allah lokacin da tayi arba da duwatsun gaban rigar, ta kara zazaga hannayen dogaye ne sun matse daga karshen tsintsiyar hannun,

Adu'ar saka sabin kaya tayi Inda ta warware wandan ta saka shi, Allah ya taimaketa mai jayuwa ne dan haka bai Bata wahala wajen saman ba, ta dora abayarta à sama ta kara gyara zaman chouchounta dan tana gudun cirewa ta kasa daure kan, à hankali take yana dan kwalin nan tayi masa tamkar na larabawan nan ta juya tana kalon madubi à hankali ta mika hannunta tana taba fuskarta ta ce" komai na son gyara

Komai Bata shafawa fuskarta ba, kafarta kadai ta dan shafawa mai sama sama ta saka takalminta plat ta fito cikin nutsuwa

Cikin sauri sauri Ta sauko ta nufi motocin dan kuwa har sun fifito ana saka kayan dake dauke da wainar sadaka,

Har kasa ta zube tana gaishe su, à tare suka amsa Elhaj Ibrahim ya ce" ina direban ?

Muryar Rislan ta katse su lokacin da ya fito ya sha shadarsa marun Yana dan jefa ky din Yana cafewa yace" ni zan tuka mu, su kuwa bodyguard din sai suyi mota biyu daya gaba daya baya

Hajiya murjannatu ta ce" dayar ma da Yaya nake hakurinta bale har biyu, ni ba matar shugaban kasa ba, ni ba kakar shugaban kasa ba, aman ace à falona kawai na Isa na rawata ba kato à bayana, kuma kai kana kalo Elhaj bazaka hanna ba

Elhaj Ibrahim ya DAnYi kasakai ya ce" idan mun Dawo zanyi magana

Ta turo Bakinta ta ce" nifa yanzu na tsufa a daina yi min wayo,

Elhaj Ibrahim yayi murmushi Yana kalon lokacin da aka bude mata ta shiga tana mitarta,

Shima bayan ya shiga Inda Nuriyah da Rislan suke gaba ya tada ya kama hanya

A hankali rislan ya dan kali gefen Nuriyah ya ce" Nuriyah !!!!

A tare suka kalo wajensa suka tsura masa ido dan Jin mai zai ce

Nima idon na zuba masa dan jiyo muku da wace kuma ya zo😁
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(15)

Rislan ya ce" zaki zama Kawata ?

Nuriyah ta zaro ido tana kalonsa

Yayi murmushi ya kara cewa" kinsan kinada kyau ?

Daidai wannan lokacin tsoronta ya ninku, ta sada kanta kasa tana wasa da yan yatsunta à ranta tana fadin wannan wani irin mutun ne

Elhaj Ibrahim yayi murmushi ya kawar da kansa gefe Yana kalon bakin titi, Inda Hajiya Murjannatu taki kawar da kanta ta tsura ido tana karantar halayen Nuriyah

Rislan ya ce" Nuriyah

Ta kuma dukar da kanta kasa tana tunanin shi wannan wani irin mutun ne, abota da mace, macen ma kaskantaciya kamar ita

Maganar Hajiya Murjannatu ce ta katse ma Rislan tasa Inda ta dan kebe bakinta gefe ta ce" insha Allah gobe ne zamu ci diner da iyalan Kan Giwa da shi

Elhaj Ibrahim ya dan juyo ya kaleta Yana dan kara gyara zaman gilas din fuskarsa mai kara masa karfin gani ya ce" masha Allah, ya samu lokaci KO ?

Ta kawar da kanta gefe ta ce" Aban karibullah, mai yasa baka son takurawa yaron nan ne ? Kaga fa irin halin da ya saka kansa à ciki, yanzu fisabillilahi idan ya mutu à wannan rayuwar wani irin makoma zai tarar ? Aban karibullah, ka hanene ni magana, aman kayi hakuri ni na gayato shi da iyalansa

Elhaj Ibrahim yayi shiru Yana nazarin matarsa, ita dai ta manyata duda shekara goma sha biyu ya bata aman yaci ace à shekarunta ta daina yawan saka damuwa à ranta, har zaiyi magana sai ya ja bakinsa yayi shiru à hankali jikin tsufa ya kama ya fito Inda bodyguard dinsa ya mika masa sandarsa fara ya shiga dan dogarawa Yana tafiya Yana sadaka, hakama matarsa da su Rislan da Nuriyah

Sosai Rislan ke yiwa rayuwar Nuriyah katsalandan har suka gama suka juya gida, Inda daidai wannan lokacin ta fara yiwa abin dariyarsa murmushi aman bata furta komai
dan ita ganni take wannan mutumin bai santa ba da bai nemi irin hakan ba, da bai kirata da sunan aminiya kawa wai da wani matarsa

tayi murmushi lokacin da ta fito daga dakin hajiya ta hango sabin kyankyasar dawisun sun fara girma sosai saï irin karar nan suke suna bin sahun uwarsu

à hankali ta matsa ta zauna ta zuba musu ido, sai ga hawaye à ranta ta ce" wai daba ma ta san dadin iyaye to ina da mutun ? Mamana idan Kina raye Allah ya bayana min ke da yan uwanki

tana nan zaune Rislan ya tardota shima sai gani tayi ya kai zaune Yana cewa" Kawata bakida kirki, sai ki gudo nan Kina morewa ki barni ?

Firgigit tayi tana kalonsa Inda ya zaro ido ya ce" kuka ? Kukan mai kike ? Lafiya ? Mai yake miki ciwo ?

Da sauri ta Mike tsaye tana dan dingisawa dan ta jima à zaune, haka jikinta ke Bari cikin muryar kuka da gajiyawa ta ce" Kai mai gidana ne, ni ba kowa bace sai yar aikinka baiwarka, wace koda tsakar dare sai ka sakani aiki nayi maka, ka daina yaudarar kanka dan kagan ni nan *NEMAN NA KAINA* na fito, bazan yarda dalilin

muna gaisawa da dan masu gidan na rasa aikina, bazan taba lamunta nayi wasa da damar da ta rabani da yawon titi na dawo aiki à kamilance ta subuce min ba, ka gane kai ba sa'a Yina bane, tsakanina da kai ka sakani nayi maka ne, ka daina nuna min nima inada darajar da zan iya zumunci da kai

Rislan ya zaro ido ya ce" ashe bakida hankali ? Nutsuwarki ta shirme ce ? Ashe musuluncinki à baki ne ? Yau idan har baki iya banbance tsakanin talaka da mai kudi ba Wanda ya fi wani sai Wanda yafi Jin tsoron Allah à wajen shi mai dukan ba to ki koma makaranta,
shin wannan abin ne ya cika maki ido wannan kyalekyalen duniyar ? Nuriyah ? My Nuriy, kin manta wannan kasar da kike takawa ita zata matseki, karshe ki zama ita ? Injin sallah kike, sannan kin yarda da kalmar innalilahi wa'ina ilaihi raj'une, daga shi muke, wajensa zamu koma, ina son Inda hali ki yarda da zumuncina har Allah ya cikan burina na alkhairi à kanki Nuriy

gaba daya jikin Nuriya yayi wani irin sanyi Inda ta juya da gudu ta fada dakinta ta fashe da kuka

da baya baya ya fada samman tafkekiyar kujerar dake falonsa bayan ya kare kalon diramar Rislan kaninsa da wannan bakuwa da Hajiya kakarsa ta jajubo, à hankali ya furta *wacece ke ?*

Toh fa
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(16)

Ummuta plz i beg u ki suburbudo min *MUGUN BUTULCI* kiyi anfani da dumbin basirar da Allah yayi maki, cikin nutsuwa ki kara fadakar nishadantar da mu Auntyna, mu muna jiranki plz😑

Aunty *Batul* *Anfanin soyaya fa aure* mu kam à zaune muke dan karin haske à namu auren, plz ki motsa, iliminki yafi gaban nan my aunt,

Na sadaukar da wannan shafin wa *Aunty Ummun Safwan And Aunty Batul*

My masoyan usul ina mika sakon gaisuwa na da jinjina gare ku, domin Kuna cikin mutanen da nake farin cikin buda data dan na karanta sun tashi lafiya wato *MaMan Manal* nd *LEEMAT*

Karfe takwas na safiyar asabar wata jiniya tayi kara, wada à karan da tayi na ga ikon Allah, kowa ya rikice, sai shige da fita suke kowa cikin rawar jiki Yana aikinsa harma da Wanda ba nasa

Shugabar kicin ce ta shigo tare da Nuriyah à bayanta

Da sauri naga suna gaisheta da mutunci domin KO ba komai ta manyata,

Wata mai suna Bilki ce ta matso ta ce" mama, yau *KAN GIWA* zai shigo ne ? , munji karar jiniyar shaida hakan

wannan mata mai suna laraba ta ce" Eh, insha Allah yau zai shigo, sannan ba'a fadi lokacin shigowarsa ba

da sauri wani bature ya ce cikin turancin shima" Shin wani ya aikata wani laifi KO ?

Ita kanta laraba ta dan langwabar da kai ta ce" à gaskiya nima ban san shigowar da zai yi KO na menene ba, domin ba'a fadi ba, ina fatan ba Wanda ya san yayi wani munafurcin, dan kuwa wannan karin KO da wasa bazan lamunci laifin wani ya shafeni ba, kunga dai abinda ya faru da jikata ta cikina yanzu shikenan an koreta daga aikin dan ta sakawa hajiya tatasai à miya, du Wanda yayi garaje shi zai kwana ciki kar ku ce ban fada maku ba

Kasa kasa suke kus kus, kowa na tambayar dan uwansa ai dai ba abinda yayi, Nuriyah mamaki kokarin kasheta yayi, tana mamakin irin,, wannan tsauri, nan da nan itama tsoro ya kamata, duda tana nan lokacin da Hajiya ke shaidawa mijinta cewar Kan giwa zai ci abincin dare à bangarenta, aman sai da cikin ya murda, dan kuwa à jiyan nan ta daukowa hajiya ruwan sanyi bayan Bata sha ruwa mai dumi dumi ne ruwanta koda yaushe dan karin lafiya

a hankali ta sauke ajiyar zuciya ta bi Mayan laraba wace ta nuna mata babar kurar da zata jera gaba daya kayan abincin ta kai idan bakin sun Zo, hakama fannin abin sha ta dauko katuwar farar takardar da aka rubuta komai, tun daga jus da ruwa kowa da kalar Wanda yake sha, abin Mamaki à sunayen sai ta ga Harda Isabel, ita kadai take rayawa à ranta kenan à zuriyar Elhaj Ibrahim akoy Christa

Idannuwa ta zaro daidai lokacin da baturen nan mai kula da yannayin suturar da za'a saka idan KAN GIWA zai shigo Yana mika mata wani sket daidai gwuiwa sai Riga chemise da cravate, sai yar hula baka wace zaka dan dora, sai wani dan farin zani an fitar da daidai wuya kadai an rubuta serveuse a jiki

bakinta na dan rawa ta cewa wannan bature " excuse me, aman ni musulma ce, ta ya zan saka wannan abin ?

Shima kalon mamaki ya bita da shi, Inda ya ce" to dan Kina musulma sai mai, su su Bilkiss ba musulman bane suka saka wannan à jikin su KO Kina son ki nuna min ni banida adini KO aikin naki zaki yi wasa da shi dan kawai Kina musulma ?

Ido ta kara zarowa, hankalinta ya tashi, ita fa tunda take, Bata taba saka irin hakan ba, yauma kuma bazata saka ba, bayan wa'innan da take sakawa da kyar yanzu kuma à wani kawo mata wannan abin mai shige da gyafto ace shi zata saka ?

à hankali ta koma taci gaba da kara kimtsa falon Hajiya, wace ita kanta sai murna take tana ta faman shiga daki tana fitowa

Tana gama salar isha'i ta dauko wani sket din baki Wanda ya saukan mata har kasa ta saka,

Tsaki ta ja lokacin da ta ga irin yanda yake rawa à jikinta sannan harda wata tsaga ta dafe kanta ♀ cikin takaicin wannan dabi'a ta wannan gida, Jin wannan jiniyar ta dazu ta kwasa ya shaida mata fa lale zasu ISO, hakan ya saka ta da gudu ta saka rigar ta gyara cravate din kamar yanda ya koya mata, ta daura yar hular nan wace iya gaban goshinta kawai ta rufe, ta daura farin kyalen nan sannan ta saka baj din dake shaidar ita ma'aikaciyar gidan ce

Da sauri sauri gudu gudu ta karaso kofar falon Hajiya Wanda kadan ya rage fitsari ya zubo mata sakamakon wasu jibga jibgan bodyguard har hudu, biyu à hakimce à kofar sunyi kane kane, biyu suna dan zagayawa à saman filin terrasse din

Rawa kafafuwanta suka kwasa lokacin da ya nufota da kansa ya ja bage din wuyanta ya karanta, cikin wata murya ya ce" ke kinyi lati daga kafa mun kusa hana shiga

da gudu ta kwasa ganin dayan ya bude mata kofar ta shige da salama à bakinta

Idannuwan Nuriyah tamkar zasu fito su fado kasa dan kalo lokacin da tayi arba da Wanda take Kyautata zaton wannan shine *KAN GIWA*,

Da alamar shigowarsu kenan domin kowane sai kalar gaisuwarsa yake yiwa hajiya da Elhaj Ibrahim,

A hankali take kokarin zagayewa dan ta kai kanta kicin din Hajiya tun kafin ta fadi dan kalon iyalan KAN giwa, NADIYA ba'indiya ta sha doguwar rigarta mai shegen duwatsu, ta baza gashin kanta à bayanta ta sha makup da wani digo à goshinta, sai DJAmila Ibo, ta sha wata bugagiyar atanfa ta kafa daurin dan kwali à kan uban atach din da ta dora à kanta, sai Rislan ya sha kananun kayansa sun masa kyau sosai, sai Uban garin *KAN GIWA* Wanda ya saka wandansa na soja, sai farar Riga wace ta bayanar da irin yanda tarin kirjinsa da sauran jikinsa yake

Nadiya ta saka Nuriyah zaro ido daidai lokacin da ta rungume Kan GIWA ta mana masa peck à kunci sannan ta ce" i miss u

Kan giwa ya dan kawar da kansa dan ya ga yannayin hajiya, bai ce da ita komai ba, aman ya cika da mamakin ina masu zuba abinci da jus na tarban baki

Cikin faduwar gaba Nuriyah ta turo wannan kurakurar ta shigo daidai lokacin da Isabel ta shigo itama wace ta sha dan karamin sket dinta KO gwuiwarta bai rufe ba haka ma rigarta yar karama ta daure jan gashin dake malale à kanta, ta sha zako zakon faratunanta, haka gashin idanuwanta ta kara wasu zako zako, ga Kwayar Idannuwan tamkar na mage,

Tana karasowa ta dan daga hannu ta ce" hi mamy, hi papy

Direct ta karasa jikin *KAN GIWA* à gaban matansa da kaninsa da kakaninsu ta dan rankwafa ta mana masa Kiss à lebensa ta furta" Hi my hero, ta wani kashe ido daya ta dan girgiza kirji

Nuriyah da ta saki kurar nan ta dafe kanta ta furta *WAYo* cikin tsoro da mamakin wannan matar sannan tsoron juyowar da suka yi à tare suka zuba mata ido ya dirar mata à lokaci guda

Ta dora hannayenta à saman kanta ta kuma cewa *Na mutu shikenan na kade*

Kadidi na kuma cewa *TOH fa* ♀
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(17)

Hajiya murja ta ce" Nuriyah kin bige ne ? Sanu fa, plz kiyi à hankali

Da sauri Nuriyah ta tare ta shiga karanto du adu'ar da tazo bakinta sannan ta daina hada ido da kowa bare har ta rasa nutsuwarta

Ajiye takardun kalolin abincin da aka girka ta shiga yi Inda idan ta ajiye robar ruwa da kofi sai kuma ta ajiye takardar, ta ajiyewa Isabel wace take ta Binta da kalo ta juyo daidai Kan giwa, gabanta ya yanke ya fadi sakamakon dantsen hannunsa da tayi tozali da shi à ranta ta ce" lale ka amsa sunanka *Kan Giwa*,

Ta mika hannunta ta ajiye babar robar ruwa ta dauko kofin kwalba ta ajiye, sannan ta dauko takardar ta ajiye à dan gefensa Inda take dan shakar kanshin turarensa mai mugun kwontar da hankali(□)

Muryar Isabel ta katseta lokacin da ta ce" Ke, wannan sket din da ya saka ki saka shi ? Idan za'a zubawa my hero abinci ba'a taba irin wannan shigar haka ba, sai kace wada kika je wajen karatun adini ?

Djamila dake gefe ta ja tsaki ta zabgawa Isabel harara aman bata furta komai ba

Nadiya ta dan kara yin kasa kasa da muryarta ta ce" i said i miss u husband

Kan giwa ya kara waigowa Yana kalonta ya ce" really ?

Ta dan lumshe idanuwanta, tana nufin eh
Isabel na lura da abinda ke faruwa ta kara matsawa ta kara shige masa ta ce" Hero, ina magana fa

Ya juyo ya zuba mata ido, sannan ya dan kali Hajiya Murja da ta kada kai ta ce" rayuwa

à hankali ya ce" Madame ya dai, ni yau kamar ba'a wani murnar ganina, sannan ya akayi na ga yar aiki kwaya daya ? Ina suke ne masu aikin ? Kuma haka ake taryen baki har yanzu ba'ayi serving Din mu ba, an karya min dokar idan zan Zo a tabatar an gama hada min komai, sannan maganar wannan bakin abin da ta saka shi ba'a bata Wanda ya dace ta saka ba ? Ni fa bana son kazanta, dan haka yarinyar nan gaskiya bazan zauna da ita ba

tunda ya fara magana a kanta ta lumshe ido tana Jin yanda muryarsa ke amo , irin voi rok din nan ne da shi, à muryarsa babu irin alamar tausasawa cikin taushi, aman ba karamin caza kwakwalwar yan mata take ba, tana cikin adu'ar Allah ya kubutar da ita muryar Rislan ta farkar da ita Inda cikin ladabi ya ce" Eyah Yaya, laifina ne, ni na ce ta saka shi , i'm sorry ba laifinta bane

ido Ibrahim Kan Giwa ya zubawa dan Uwansa Yana nazartar maganar sa,

Muryar Hajiya Murja ta kuma fargar da shi, Inda ta ce" bama wannan ba, koda ba kai ka sakata ba, yarinya ni na zabeta, ni nayi niyar ta zauna à wajena, bafa ka Isa ka koreta ba, sannan dan kaga ni kadai ce à zaune à wajen nan har wannan baturiyar mai sifar aljanu ke shiga jikinka haka, idan nayi magana sai kace kawarka ce dan ubanka kawar taka zatana yi maka wannan lalatar à gaban matanka ? Shin Kan Giwa mai ka dauki Aure ? Sunnar fiyayen halitar ne kake wasa da ita haka ? Shin Kan Giwa kana fatan ka samu rabauta kuwa

sai kuka ya kubce mata Wanda gaba daya jikinta ke girgiza da gani tana Jin wahalar yanda ta tsinci kanta da lamarin jikan nata

idannuwa suka zaro, Isabel ta shiga tambayar whats happen , domin da hausa Hajiya murja tayi maganarta Djamila da Rislan da Kan giwa da kuma Nuriyah dake tsaye tamkar gunki ne kadai suka fahimci yarenta Inda su Isabel da Nadia suke binsu da kalo

kasa kasa *Kan Giwa* ya ce" ku tashi ku bar mu

sifsifsif kowa ya kama gabansa ciki harda Nuriyah da ta nufi kicin da sauri Rislan ya rufa mata baya

suna tafiya Ibrahim ya matso da kujerarsa daf da ta Hajiya Murja ya ja numfashi ya sauke tamkar bai son yin magana ya ce" Damuwar har ta ritsaki haka hajiyata ?, fada mini mai kike SO nayi miki ?

Hajiya murja ta juyo da ganninta daidai fuskarsa ta ce" ka nisanta kanka da Zina, Zina mugun aiki ce, Zina na gurbatar da rayuwar dan Adam, tana sakawa komanka ya ja baya sannan idan ka mutu à halin Zina zaka hadu da fushin ubangijinka, Wanda ya haliceka, du isarka kai ba kowa bane a duniya da kiyama yanda Allah yayi niyar yi da kai zaiyi da kai à lokacin da yayi niya, yau idan ka juya ka jika à cikin kabari mai zaka bada hujar godewa Allah da wannan ni'imar da yayi maka ?

Ibrahim ya lumshe idannuwansa, tabas bashida Wanda ya kai wannan tsohuwa, wannan tsohuwa ita ce mai son farin cikinsa duniya da kiyama, abinka da rainon turawa basa boye Abu magana su kan yita ne kwaro kwaro ya ce" Hajiyata, ya zanyi ne ? Na kasance mabukaci

Hajiya murja ta kawar da kanta cikin kunya, aman ganin kunyar nan ba abinda zata kara mata sai kara ci baya ta ce" Matan ka aikin mai suke, yanzu tsakaninka da Allah yaushe rabonka da shinfidar matanka

kai tsaye ya ce" basu iya gyara shinfidarsu ba (😂), basu iya tarban mijinsu ba, su dai abinda suka iya su kashe kudi, su kwonta suyi baci, suyi wanka su taka jirgi yau suna wannan kasa gobe suna wancen kasa, ni kuwa ya zanyi, da na auri Nadia Ya kasance Sam bata iya mini, hakan ya sa na auro yar Ibo dan ana fadin sun iya tarban mijinsu aman itama kanwar ja ce, ya zanyi ne hajiyata

Hajiya murja daidai wannan lokacin kam ta kai makura à Jin kunyar irin abinda yake fadi Aman ya ta iya ta kara shafawa idanuwanta toka dan burinta ya kasance cikenken namiji, ta ce" Ibrahim, dan matanka sun kasance ragwagin mata hakan zai baka damar bin wata matar KO nace wasu ? Ka kara Aure mana

Kan giwa ya zaro ido ya ce " Aure ? Wa zan aura ? Kinga dai bazan auri Isabel ba domin Sam musulunci baya cikin tsarin rayuwarta, dan na gwada sosai aman abin ya gagara

Hajiya murja ta girgiza kai tana mamakin zamani ta ce" ita kadai ce mace ? Du matan duniyar nan, idan kyan ne ka aura, idan asalin ne da arzikin ka aura yanzu ina bukatar kayi auren nutsuwa, ka SAMU nutsuwa nima KO na samu fa'ida à cikin kabariba, shin à tunaninka aikin da kake aikatawa mahaifiyarka bata samun nata kason na azaba ?

Da sauri ya kaleta fuskarsa alamar tsorata da furucinta
ta ce" kwarai kuwa, idan alkhairi kaci gaba da aikatawa khairin nan zai tarda ita du Inda take, idan shari ne zai tarda ita, dan haka ka kiyaye, Kan giwa, yau mutuwa KO yanzu KO yanzu idan ta daukeni zanso ace na barka cikin rayuwa mai kyau sannan ina adu'ar Allah ya nuna min yayanka, shekara wajen shida da Aure aman har yanzu mata sun tsuke ciki su yan gayu ? Ku gagauta komawa ga Allah tun kafin wuri ya kure

Kan giwa ya ce" yanzu dai Plz ki bar maganar nan haka, nayi maki alkawarin zan Sami mace na kara aure

Hajiya murja Tayi murmushi ta ce" Allah yayi maka albarka

Ya amsa Yana kokarin dane damuwar dake damunsa
HajiyÀ ta Mike ta dauki waya ta Dana Kiran kicin Inda ta ce" Nuriyah ki hanzarta kawo abincin aman nawa da na *KAN GIWA* kadai dan sauran sun tafi

Nuriyah ta amsa da.....
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(18)

Nuriyah ta amsa da To,

Tana ajiye wayar ta juyo jikinta na Bari ta ce" plz ka gwada min abincin da KAN GIWA ke ci

Rislan yayi dan tsai ya shiga dora mata sannan ya ce" an taba fada miki idan Kina yannayin tsoro Kina yin kyau sosai ?

Nuriyah tayi murmushi ta ce" tsokana bata kare maka Yaya Rislan

Ya matso ya ce" kaunar Nuriyah ce ke kokarin zautar da ni my Nurih

Ta kada kai ta juya tana tura yar kurarr nan dan idan ta biyewa Rislan ta san zata rasa aikinta ne cikin sauki, hakan ya sa ta nemi hanyar da zata sadata da su Hajiya

Tana karasowa ta maida hankali ta zuzuba musu kamar yanda aka koya mata sai dai bata bude ruwan KAN GIWA ba domin bata san shima Yana cikin tsarin abinda ake yi masa

Juyawa tayi da niyar tafiya, Inda ta tsinci muryarsa ya ce" ke noncence, uban wa kike SO ya bude min ruwan ?

Daman cikin tsoro take, abin sai ya karu, ta ce" kayi hakuri

Kan Giwa ya mike ya dauki goran ruwan ya kawo gareta kafin hajiya ta karaso ya bude marfin ya tsiyaya mata tun daga kanta gaba daya ya bi jikinta ga Shegen sanyin ruwan, ga sanyin AC, ga jikinta ba hijabi,

Kalon yanda jikinta ke Bari yake da irin yanda idanuwanta du suka wani firfito ya dago fuskarta ya ce" *Ke, haka kawai nake Jin na tsane ki, kuma sai nayi maganin jakar kwakwalwarki*, Yana gama fada ya saki kanta yayi hanyar fita Inda ya bar hajiya murja sai sababi take tana fada tun karfinta kan abinda ya yiwa Nuriyah

Nuriyah baiwar Allah, banda hawaye ba abinda take, Inda Hajiya ta salameta ta ce taje ta huta

tana fita Rislan ya shigo Inda yake tambayarta ina Nuriyah ta shige ?

Hajiya ta danyi kalar tausayi ta ce" ta tafi ta kwonta, dan kuwa wannan mai zuciya à bakin ya tiltile mata goran ruwa à jiki, ni tsorona kar tayi mura DAn da alama Bata saba da harkar sanyi ba

Rislan ya girgiza kansa ya ce" My Nurih, daman zuciyarta cike da fargabar haduwarta da Yaya, Allah shi kyauta dan ma Allah ya tsaya mata kuma kema kin tsaya mata ai da tuni ya koreta

hajiya ta girgiza kai ta ce" ka fahimta, yarinyar ce is verry innocent, ina jinta à raina, shi yasa nake Jin haushin abinda yayi mata

Rislan ya mike yana cewa " ina zuwa

Yana fitowa ya nufi hanyar dakin Nuriyah, aman mai sai hangota yayi cikin duhu te hada kai da gwuiwa tana dan sheshekar kuka,

A hankali ya karasa ya dan dofana ya zauna ya ce" *NURIYAH* cikin wata voice mai ban tausayi

da sauri ta dago da kanta ta sauke idanuwanta a fuskar Rislan, Bata san sanda kuka ya kubce mata, cikin gunjin kukan take fadin " *Tsoronsa nake, ya tsaneni, kar ya kashe ni, ina tsoron kamaninsa, baya fara'a, bashida tausayin talaka, baya yafiya, ni gidan su Aba nake SO, gwara naje can na fita layi layi NEMAN NA KAINA da na zauna à wannan guri mai cike da hatsari da barazana wa rayuwana*

Rislan ya rintse idannuwansa cike da tashin hankali ya ce" plz, kiyi hakuri *MY NURIH*

A hankali ya maimaita *MY NURIH*, ta ina ta zama haskensa, Yaushe ma ya santa harda zaiyi mata suna da wai HASKENSA,? Cikin kunan rai ya nufo wajen da suke zaunen cike da izgili Yana ayana zai koya masu hankali

♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(19)

Dakatawa kan giwa yayi, Inda jikinsa yayi mugun sanyi sakamakon Jin da yayi Nuriyah ta ce" Yaya Rislan, na sani aikina a gidan nan kwonciyar hankalina ne, rufin asirina ne, sannan daukakuwar darajana ne, Dan Allah ina rokon ka, ka cire maganar SO à tsakanina da kai ka daukeni tamkar kanwarka ka saka ni à hanya, dan idan yau aka kore ni à gidan nan zan koma layi à titi ne ina *Neman na kaina*

Ajiyar zuciya ya sauke Inda ya juya à hankali Yana tafiya ya nufi gidan Nadiya,

Yana shiga ya tarar da ita daga ita sai dan wandonta da yar ficikar rigarta tayi rigingine mai aikinta tana murza mata wasu mayuka a jikinta sai lumdarta ake

Mai aikin ta fara farga da shi Inda ta Mike da sauri jikinta na bari tayi hanyar dakunansu,

Mikewa Nadia tayi lokacin da kanshin turarensa ya kai hancinta, tana yin arba da shi mamaki ya rufe ta, domin koda wasa bata taba tunanin zai iya kawo kafarsa har gefenta ba, dan kuwa du wace yake bukata yakan yi kiranta ne à waya ta tarda shi sannan idan ya gama da ita ta juyo ta maido kanta da kanta ba wani rakiya

Mikewa tayi tana lumshe masa manyan idanuwanta ta fada fafadan kirjinsa Inda ta saki ajiyar zuciya

a hankali ta furta " i miss u huby

Kan GIWA ya lumshe idannuwansa a hankali ya dago da kanta yana kalon kwayar idanuwanta har ya hade bakinsa da nata, cikin nutsuwa yake kissing dinta, Inda ya dauketa yayi dakinta ya direta saman mamakeken bed dinta, bin bayanta yayi ya ci gaba da kissing dinta hannunsa na kokarin shafa yan duguidugui din na shanunta
jinsu yayi tamkar sun kara kankancewa, ya sauke ajiyar zuciya a ransa ya ce" *matsala*, yanzu da Isabel ce da sunyi tsuru tsuru tamkar su tsole masa ido

A hankali ya ja ya cire yar yololuwar rigar jikinta Wanda yayi arba da su tamkar irin an tsoma kaza a ruwan zafi da take motsewa, ya dan Lumshe idannuwansa a ransa ya ce" a haka dai kyau kamar ka saceta ka gudu aman à can ba hus

kokarin sarafata yake, Inda tayi masa lakwass tamkar mataciya bata da katabus à shinfida ita dai kawai yayi romance dinta batada jimirin sex KO kadan,

Jan blanket din dake mamale a saman gadon suke domin burinsa ya samu nutsuwa, sai ganin wani magani ya fado kasa

idannuwansa ya dan tsura sai ya ga pilule ne, wato maganin hana daukan ciki, dakatawa yayi ya sauka ya mika hanu ya dauka Yana karantawa
Tabas na hannin daukan cikin ne, jiyowa yayi ya tsura mata manyan idannuwansa da suka kara canza kala ya nuna mata da alamar Yana son karin bayani

Ta danyi fari da idanuwanta ta ce" Huby, ai kar ka damu bazan dauki ciki ba, dan na sha na yau kuma kaga allurata bata jima da nayita ba, nima bana son haihuwar nan haka kawai nono ya zube min

Kan giwa ya watsa mata harara ya ce" Uban wa ya baki izinin daukan maganin yin ciki ? Tsufa ? Zubewar nono ? Bayan Wanda ya zube miki à nan ? To umarni na baki ba shawara ba, a yau ki nema à cire maki na alurar kuma ki tabatar kin zubar da wa'innan magungunan dan kuwa ni haihuwa nake SO idan kuwa ba haka ba zaki hadu da fushina, idan kin cire ki kawo min kanki da kanki sannan ki nemi abinda zai saka ki jurewa

Yana gama fadar haka ya juya ya bar Nadia nan zaune tana tunanin yanda zata yi ,

Yana fita ya nufi gefen Djamila sarkin baci,

Yana shiga ya tarar TV nayi, kayan abincinta da ta gama ci à barbaje, tana yashe a nan tayi dayadaya, bacinta take hankali kwonce, bakinta Ham à bude dan kuwa Djamila ba dai gagar baci ba

ya jima Yana tsaye à kanta, Yana ayana abubuwa da dama, a ransa shi kadai ya ce" yanzu ba ka tasheta ba ta isheka da labarin mutanen da baka sani ba, sannan idan ka shiga tamkar ka fada ruwan ranga Salam ba komai, ya juya kansa ya gyara mata kwonciyarta ya dauko blanky ya rufa mata, ya kashe TV, ya daidaita mata AC din sannan ya juya ya kashe fitulun ya rufe mata falon ya haura gidansa

Yana shiga ya fice falonsa baba Inda ya tarar da Isabel nan tana ta tikar rawa bata tafi ba tana jiransa, da alama Tama fi shi kamuwar

A hankali yake dan kalon kugunta, nan da nan ya kawar da kansa Yana furta a'uzubillah,

Hade fuskarsa yayi daidai lokacin da ta juyo ta nufo shi tana ta kokarin kwadaitar da shi Zina,

Dakatar da ita yayi ta hanyar daka mata tsawa ya ce" ke fice min à gida

idanuwanta ta zaro ta nuna kanta ta ce" héro, ni ? Mai nayi ? Plz kayi hakuri my hero

ya zabga mata harara ya ce" kar na buda idona na ga wa'innan tsofafin kafafuwan naki à nan, dan ina mai tabatar miki da zan karya su

Da sauri ta juya ta nufi kofa mamaki kamar ya kasheta tana mamakin wai hero ne da korar abinda tamkar maye idan ya samu, ta dan daga kafada ta ce" mai yiwuwa wata ta tabo shi zai huce à kaina, yayiwa kansa bakin ciki

shima da ido ya rakata tamkar ya jawota ta dawo aman Inna, kawai kukan kakarsa yake tunawa sai ya share, da baya ya fada kujerarsa ya fitar da zazafar iska ya ce" dole nayi Aure, ina bukatar yin aure

to kayi mana♀
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

Haka rayuwana Nuriyah taci gaba da tafiya, cikin ikon Allah Tana samun nutsuwa a zamanta da Hajiya murja,

A kulun kara shakuwa suke ita da Rislan, Inda rislan ya dage wajen koya mata son sa, sai dai a kulun zilewa take dan gani take konciyar hankalinta yaci gaba da dorewa ne dan tana gujewa soyaya da Rislan

A yauma kamar kulun, tana zaune a wajen farar kasa ta balbalin hajiya murja, ta mayar da hankalinta wajen tsuntsayen nan tana kalo ita daya sai dan murmushi take, dan kuwa Tana kaunar wa'innan abin kiwo har cikin ranta,

Wata mota ce ta tsaya, mota har mota, wuleliyarta fara kar, tunda ta shigo Nuriyah ta danyi tsam, ta daina murmushin da take sannan gaba daya ta tsargu da zaman da take, dan kuwa ta san wannan motar dai ba su Hajiya bane a ciki dan suna cikin gidan Elhaj ibrahim na dan zazabi

Bata gama tunaninta ba ta ga an bude kofar motar

Kafarsa ya diro waje , cikin bakaken kaki yake, fuskarsa da bakin gilas

Waya ce à kange a kunnansa Yana amsawa Inda yake fadin " Rislan, kana ina ne ?

Ba'a Jin abinda rislan din ya fada sai shi ya ce" KO mai kake kayi gagawar zuwa wajen Hajiya, grand papy ba lafiya wai duka yana son gannin mu, su Baby ma sun taso ita da mamarta, Aba ma Yana hanya, dan haka ka Zo kawai, ka san halinsa idan bashida lafiya sai sarewa

Yana gama fadar hakan ya katse, wani Kiran ya shigo masa ya daga ya ce " baby

daga dayan bangaren an jima ana magana Inda ya dan lumshe idannuwansa ya dan jingina da jikin kofar motar Yana sauraro, can ya ce" Baby, dan kawai babu yan mata à nan sai ki je ki tile a garin su mamanki, kinga fa ga su Djamila ai kuma Nadia na son ki KO ?

Kuma magana aka yi, Inda ya dan girgiza kansa ya ce" kinga, yayan kanwar maman naki suma su biyoki mana, baby wai ni bakya missing dina ? Kinga KO kin Zo fa nine kulun nake ta kai kawo wajen hajiya da gidana, du irin aikin da nakeda sai na Zo na ganki kafin kiyi baci, baby gida fa zaki Zo, bazan iya ba, nayi iya hakurina yanzu bani maman naki

Sosai ya gaisa da matar Baban NASA Inda ya kara jadada mata da zai je ya daukosu, plz kar su bar baby

hajiya Hassana tayi murmushi ta ce" kar ka damu KAN GIWA, insha Allah zan Zo da ita

Yana kashe wayar ya dan dafe kansa Yana mamakin rigima irin ta Murja autarsu

a hankali ya juya yana tafiya Wanda ya hangi bayan Nuriyah wace tayi mutuwar zaune, ita bata Mike ba, ita bata ji dadin Zaman ba, kamar ma wace take jinta a jike dan tsoro

Girgiza kanshi yayi Yana tunanin wannan yarinya akoy girman kai, tana sane da ya Zo aman bata gaishe shi ba, ya kawar da kansa Yana mamakin yanda bata Jin tsoronsa kamar sauran jama'a, KO don ta san Hajiya tayi tuwo tayi miya à lamarinta , yayi kwafa a fili ya ce" banga yarinyar da zata kawo mini raini ba du duniya, balatana à Nigeria, kuma a kano, karya take

Yana shiga nuriyah ta Mike da sauri tana duba sket dinta, Inda murmushi ya dan subuce mata, tsabar tsorata ce tayi har tayi zufa haka, a hankali ta taka tayi dakinta, dan kuwa koda wasa bata son ta nufi wajen hajiya har wannan mai halitar kakarfan namiji ya wulakantata KO tayi abinda zai koreta ya tona mata asiri

Zuwa karfe bakwai gidan hajiya ya cika da manyan mutane yan dubiya, ciki harda su Hajiya Hassana matar karibullah da karibullah da yar auta murja wace ita kanta ta girma masha Allah aman sai zuba sangarta take

Hajiya Bata nemi nuriyah ba dan ta san tana cike da fargabar *KAN GIWA* dake gidan, dan haka tayi kiranta da waya take shaida mata tayi zamanta zatayi kiranta zuwa safe

Sosai nuriyah taji dadin hakan dan kuwa hankalinta sai ya kwonta sosai harma ta tsala wankanta bayan ta gama sallah tayi kwonciyarta baci

Da sasafe ta farka, ta tsala wankanta sai ta canza kaya dan kuwa Bata sallah, haka kawai taji tana ta'ayin tayi kunshi, hakan ya sa ta dauko ta kwaba kayan kunshinta ta zauna nan saman dan kafet dinta ta shiga kunsawa kanta, daga ita sai dogon wandon da ta saka sai farar Riga dan tanada tabacin ba Wanda zai shigo dakin nata a daidai wannan lokacin

ta gama da kafa daya ta jawo dayar kafar ta gyara ta shiga kunsawa hankalinta kwonce, sai ji tayi gagarab an turo dakin nata an shigo

Baki da hanci ta saki lokacin da wada ta shigo ta nufi wajen sif ta bude wani gefe da ba komai a ciki, ta bude katuwar Jakarta da ta jawo, ta fara ciro kayan dake ciki tana jerawa a cikin sif din

sai da ta gama ta juyo ta kali Nuriyah da tayi zololo tana kalon ikon Allah ta ce" hi, i'm *MURJA* Karibullah,

Tana gama fada ta shiga cire babar rigar da ta dora saman kananan kayanta Ta cire komai ta daura tawul ta shige bayi

Da ido ta bita da kalo, can kasan zuciyarta ta shiga tunanin KO dai Autar su Rislan bata san nan dakin yar aiki bane ? KO dai da nan ne dakinta ?

bata gama wannan tunanin ba ta kuma fitowa Inda ta fada saman gadon Nuriyah tayi daidai bayan ta kara karfin AC sai baci yayi awon gaba da ita

Nuriyah ta gama daure ledar kafarta tayi zuru tana tunanin wata sabuwar, tsoronta daya kar aje an koreta ne, aman mi zai kawo yar Elhaj Karibullah, kanwar KAN GIWA dakin yar aiki, kawai Bata san an mayar da nan dakin yan aiki ba da Bata shigo ba,

Kalon kafafuwanta take tana ta tunani, Inda aka shiga buga kofarta cikin nutsuwa

Gabanta ya ci gaba da duka ta juya ta kali kofa tana tunanin wa ke buga kofarta, ta shiga shawarar shin zata bude kofar ne KO kuwa ???? ♀

Mura♀♀,, i'm sorry readers, mura ne ya kada ni
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(21)

Na gode da ada'arku gareni, ina fata du Wanda yake halin rashin lafiya Allah ya bashi lafiya, masu lafiya Allah ya basu ikon morarta ta hanyar aikata alkhairi da bautar mai duka, da'inda kuwa suka rigayemu Allah ya haskaka kabarinsu, ya tausasa makwoncinsu ya bamu guzurin tardasu

Mata à gurin Abdulahi, Hajiya *Maimunatu* ta gabanki karya ta bayanki..... 😆, ina tayaki murnar kamala novel dinki *Ina matsalar take*, ina adu'ar Allah ya yafe maki kuran dake ciki ya baki ladan dake ciki, gaba dai gaba dai tawan, ja muje, Allah ya kara basira ❤❤😘😘😘😘

kalon kofar take tana Jin faduwar gaba daidai lokacin da bugun kofar ya karu

Firgigit Murjannatu ta farka tana dan mitsika ido, ta kalo wajen Nuriyah da tayi zuru sai kifta idannuwa take tamkar an girgiza kuliya

dirowa tayi ta mika hannu ta jawo doguwar rigarta da Bata fi cinyarta ba ta saka, ta nufi kofar

tana zuwa ta bude, ta zaro ido tayi baya da gudu aman ina kafin ta idasa shigewa ya fado dakin ya cafkota

dagata yayi ya dora à kafadarsa, Inda ta shiga wutsil wutsil da kafafuwanta tana ihun" wayo big brother dan Girman ALLAH ka sauke ni, ni wly bazan je na zaune da matanka ba, su Mamana sun tafi autrali lafin su dawo zanyi zamana da wannan, naji ina sonta, ina SO ta zama Kawata,

girgiza kansa yayi lokacin da ya direta Yana dan hararanta ya ce" baby, enaught kinji KO, bazai yiwu ki zauna a dakin mai aiki ba, bazai yiwu na ringa tsalakowa har dakin mai aiki dan na ganki ba, kinga ki fice idan bakya son zama da su Nadiyan ne mu je gidana sai kiyi zamanki har su dawo dan kinga bazaki iya zama dakin hajiya ba dan Bata daina kunna radio ba

Murja tayi kalar tausayi ta marairaice ta tsamure fuska ta ramar da murya ta ce" ina son kawa

Kan giwa ya ce" kin daina abota da ni ? Tunda momy ta rasu wanene abokinki ?

Ta kawar da kanta ta ce" ai kulun kana wajen aiki, bakada lokaci, baka kaini shopping, baka rakani saloon, baka kaini shan ice cream, baka zama na baka labari

Ya dan kauda kansa Inda da gefen ido yake dan hangen yarinyar nan tayi kamar ace mata kak ta fita da gudu, ya ce" to ba ga su Djamila ba ?

Ta girgiza kanta ta ce" bana son fita da su

ya ce " why ? Matana ne fa, idan baki fita da su ba, idan baki zauna da su ba, da wa zaki zauna ne ? Baby karki daga min hankali plz

ta shashabe fuska ta ce" momy tana cewa, u are my father, idan basa nan komai nake SO kai zaka yi min, kaine Baban yayana kuma abana, i beg u my dad, my big broth, my Freind ka barni wajenta na zauna da ita, haka kawai da grandma ta ban labarinta naji ina son ta, so plz karka hadani zama da matanka my yaya
ta karashe tana dan matso kwalar karfi da yaji

Kan giwa ya kawar da kansa a hankali ya furta oh shuiiiiit ! Baby♀,

mikewa yayi daga bakin gadon da ya zauna ya shiga karewa dakin kalo a hankali har ya sauke idannuwansa a fuskar Nuriyah dake kalon kasa tamkar ta nitse, dalilin yannayin shigarta, da kuma mugun tsoronsa, wani sashi na zuciyarta na matukar mamakin yanda aka yi har *Kan Giwa* yake irin wannan maganar mai tsayi cikin lalashi, sai yau ta yarda da maganar Bilkiss cewar irin son da yakewa kanwar nan tasa tamkar ransa

gabanta ne yayi wata mahaukaciyar faduwa daidai lokacin da ya dago habarta idanuwanta suka shiga nasa suka yi tsamo tsamo, ji tayi tamkar ta fada kogi gaba

dayanta, nunfashinta ya shiga fita da sauri da sauri, kwayar idanuwanta suka shiga shokii suna sama suna kasa, wasu yan guntayen hawaye suka zubo mata a tare, ta nemi yawun bakinta ta rasa domin sun kafe kaf

Cikin kakausar murya ya rike habarta gam ya kuma dan zaro mata ido ya ce" tabuwar lafiyar kanwata daidai da daukewar nunfashinki na kaiwa karen daji ya cinye namanki na kawo kasusuwanki na daka su da hannuna, na nunka albashinki linki uku dan ki kular min da kanwata, wato na cireki a aikin hajiya daga yau zaki kula da baby, idan kika kuskure nayi miki alkawarin karar da danginki gaba daya kafin na zagayo kanki, sai na tabatar baki bar tarihi ba a gidan duniya

Yana gama fadar haka ya cikata ya mike Inda ya bi dan ruwan dake gangarowa daga kasan wandonta, ya danyi kwafa ya fice a dakin Inda ta juyo ta tsurawa Murja ido wace take murmushi tana kokarin komawa tayi konciyarta

Wani irin kuka nuriyah ta fashe da shi Inda ta dora hannu a kai tana dan jujuyawa

Murja ta diro ta nufota tana ta tambayarta lafiya, mai ke damunta, sannan idannuwanta suka hasko mata fitsarin da ya gudu a saman tyls din dakin, murja ta zaro ido ta ce" lah, fitsari kika yi ?

Nuriyah ta bi fitsarin da kalo ta juyo ta ce" ::
ϘϘϘ NEMAN NA KAINAϘϘϘ

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(23)

Yar Gatan yayanta ND *Yar Baba* ina mugun yinku, irin Lodi lodi din nan

Yana fita daga falon ya dan daga kafa ya isa bangarensa

Yana shiga ya nufi dakin da yake tarewarsa da Isabel,

Hangota yayi kamar yanda yayi tunani tayi daydaya saman bed din nan ta saka écouteurs sai bin wakar rihana take tana irin rawarta

A hankali ya kashe fitilar dakin sannan ya karasa gareta har jikinsa na kyarma

Murja karama ta kusan minti talatin zaune dan guard din kofar dakin sun tabatar mata cewar yana ciki, hakan ya sa ta zauna ta tana jiransa ya fito ta lalaba shi dan ya barsu su tafi gidan su kawarta

Karar bude dakin hutunsa taji, hakan ya sa ta dan dago da kanta, sai dai gannin da tayi sai da tayi dan daman da bata zo ba

Saurin sada kanta tayi kasa daidai lokacin da suka yi ido hudu da big broth dinta sun fito da yarinyar da shi da bakinsa ya ce mata kawarsa ce, ta dan sha karamin wandonta da yar rigarta

Gannin Murja bai Hanna Isabel ci gaba da dan narkewa *Kan giwa* ba , inda shi kuwa wata irin kunyar kanwar tasa da dana sani suka lulube shi,

Bai taba yin tirr da wannan rayuwar ba saï a yau, kanwarsa ta kama shi a haka duda yana iya yi mata na yan duniya dan kuwa bata kamashi turmi da tabarya ba , aman wannan bama zai yiwu ba yayi mata karya ta biyu

A hankali ya cewa Isabel" ki gane, masu tsafta ke shigar jet dina, su Abana da Su hajiya, dan haka ki je kawai ki ciri ticket mayi waya

Isabel ta dan lumshe idannuwanta ta ce" please héros, karka yi min irin yanda ka saba, i beg u, idan nayi kiranka ka daga

Dan daga mata kai kawai yayi yana kokarin karasawa kusan Murja ,

A hankali ya zauna yana dan tsayar da idannuwansa kyam a fuskarta

Idannuwanta ta dago wa'inda hawaye suka gama wankewa , ta saka su kyam a cikin na yayanta Wanda tafi so du duniya,

Wani irin karfi ne ya zo mata inda ta kale shi ido cikin ido ta ce" *Yau da nice a cikin irin rayuwar Isabel shin ya zaka yi yaya!? Ina nufin idan nice nake bin maza?*
..... Bata kai karshen ayarta ba ya dauketa da mari,
Gigitancen marin da ya dauke jin ta na wucin gadi, Wanda nan da nan ya fito reras a fuskarta ya kwonta, Wanda ya kwonce mata nadin fuskarta

Cikin bacin rai ya nunata da yatsa ya ce" Ashe bakida hankali? sa'anki ne ni da zaki kali cikin kwayar idonna ki kawo min maganar banza? , shin kin ji mai bakinki yake furtawa Baby? Du dan iskan da ya taba yatsar hannunki walahi walahi sai na harbe shi, shin soyayar da nake Nuna maki ne yayi yawa har kike kokarin sangarce min ki raina ni? Kin Mance wanene ni

Murja da gaba daya jikinta ke kirma, wani irin tsoronsa da bata taba ji ba a yau ya darsun mata, sannan a yau ta yarda da maganar mutane dake cewa idan ransa ya baci baya ji baya gani, aman ina abinda yayi shi, shi yayi ta, mahaifa guda suka kwonta, ta san du abinda zai yi bazai kasheta ba, sai dai ta daku,

Da kyar ta kara dago da idannuwanta da suka yi mata nauyi ta kuma zuba masa su ta ce" ni ban isa na raina yayana Abana ba, du irin soyayar da ka Nuna min bata kai wajen da zan raina Wanda ya raine ni ba, sai dai kuma ni nan koda yayana zai dauke numfashina da bindiga sai na tsaya tsayin daka nayi magana a irin abinda na san zai cutar da shi, yayana shine exemple din rayuwana, karka manta aya ce *DU ABINDA KAYIWA YAR WANI TO ZA'A YIWA TAKA*

Tabas yaya kaima bawa ne, baka fi kowa ba a wajen Wanda ya karbi maman mu wato mai duka, sannan du dukiyar mu, du isarmu , du kyanmu, du tsaron mu , Aya

sai ta kasance a kanmu, duda yanzu baka haihu ba yayana aman kanada ni, Wace ka kilace, kake karewa,

Idannuwa ya zubawa kanwar tasa , Wanda yake cike da matukar mamakinta, sai yau ya gabe tabas ta girma, ashe girman nata har ya kai nan, a hankali ya ce" ke da ita ba daya bane, ita ba musulma bace, ita ta banzatar da kanta, dalilin kudi ba Wanda bazata kula ba

Murja ta ce" idan ita ba musulma bace ai kai musulmi ne sannan a adinin mu anyi hani da ka mayar da matar da ba taka ba ta zamto tamkar taka, sannan yaya Allah bai ce ba Wace ta banzatar da kanta KO Wace take gidan su a kamilance, shi dai yayi hani da hakan ne sannan ya fada za'ai maka, mai zai Hana ka aureta, idan har ita kake ra'ayi?

Zuwa wannan lokacin ya gama ficewa a nutsuwarsa hakan ya sa ya nunawa Murja karama hanyar ciki sannan ya Nuna mata waje ya ce" ya isa haka, kina iya shiga KO ki tafi, kaina bazai ci gaba da dauka ba

A hankali ta dan gyada kanta ta juya ta tafi inda ya koma jagab ya fada saman kujerar yana furta" Yar Allah, ka yafe min, ka shirye ni, ka nisanta ni da *ZINA*

Tana fita da kyar ta karasa dakinsu ita da NuRIYAH, ta fada saman bed din ta fashe da wani irin kuka mai tsuma zuciya,

Tana cikin wannan halin *Nuriyah* ta shigo dauke da tea , idannuwa ta zaro ta ajiye flask din ta nufi bed din da gudu tana fadi " Ya Allah, mai yake faruwa haka? Bai yarda ba KO? To idan bai yarda ba kuma sai ayi irin kukan nan hajiya? Dan Allah kiyi hakuri

Murja ta dora kanta a cinyar Nuriyah, tana ajiyar zuciya

Idannuwan Nuriyah suka sauka a fuskar Murja, ta zaro ido jikinta na kyarma ta fashe da kukan itama, sannan ta ce" innalilahi wa'ina ilaihi raj'une, ke kanwarsa Wace ake ikirarin irin son da yake miki yayi miki haka , ina da ni banza, na san du ranar da na kauce kawai kasheni zai yi

Du irin halin da murja ke ciki sai da taji kamar tayi dariya gannin irin yanda Nuriyah ta tsure kamar ita aka daka, ta lumshe idannuwanta tana sakin ajiyar zuciya sannan tana sauraron kukan Nuriya har baci yayi awon gaba da ita,

Itama Nuriyar a nan ta bingira tayi bacinta tana ta ajiyar zuciya♀

Wasa wasa yau kwana na hudu, *Kan Giwa* bai ga autarsu ba, hakan na matukar damunsa, sai dai ya ganta ta computersa, kwata kwata ta daina neman shi dan ta Ganshi ma,

Sannan marin da yayi mata sai ta cewa su hajiya ai bugewa tayi,aman hajiya hassana ta tsareta sai da ta fada mata dalili dan kuwa bata yarda cewar bugewar ne tayi ba

Sosai taji ba dadi a ranta , sannan ta gargadin yartata da su dukufa da adu'ar Allah ya yaye masa, dan kuwa du yanda kaso da shiryuwa sai ka hada da rokon Allah ya yarje maka,

A yau asabar tun karfe takwas ya farka yana dakon son gannin kanwarsa, idannuwansa ya sauke kan Djamila da ta kwana a bangarensa sai baci take, KO wanka bata yi ba bale sallah, ya dan girgiza kai ya shiga dan bubuga kafarta hade da Kiran sunanta

Wutsil ta bingiro ta Mike tana zare ido, ta ce" lafiya, du a firgice take dan kuwa tashin karfe takwas ba nata bane

Ya dan kawar da Kansa dan da yar salebar baci a gefen bakinta ya ce" ki je ki tsaftace jikinki kiyi sallah♀

Ta dan juya ta ce" ohk tohm

Tana shiga bayin ya yaye blanket din gadon ya dauko suturarsa shada kalar ash mai duhu , ta sha simple dinki anyi Riga iya gwuiwa da wando,
Haka ya zira ya dauki turare yayiwa kansa wankansa sannan ya juya ya fice

Bai zame ko'ina ba sai kofar dakin Nuriyah, yana isa ya dan dakata yana tunanin yanzu haka suna baci kar aje ya tashe su

Har ya juya kawai ya juyo ya murda abin budewar sai ganninsu yayi sun bayana *Nuriyah* a zaune a kasa, Murja a sama da kumb suna yar kokawa ala tilas sai tayi mata kitso, ita kuwa tana ihun zafi bata so

Shirun da taji Murja tayi ne ya Sakata dago da kanta dan wani fitinanen kanshi ya kaiwa hancinta ziyara, kanshin mutumen da take jimawa a sujada tana rokon Allah ya saba kiwonsu,

Gabanta ne ya mugun fadi inda ta Mike tana kirma ta ce""""""""""
*KAN GIWA**♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀*

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(24)

❤ manal dinah□ ina kaunarki kamar yadda kike kaunata. Ina son ki kamar one alive kamar two alive kamar three alive kamar four alive kamar five alive 😍😍😍😍😍 muna tare iya wuya insha allah ke ta daban ce da saura ina mungun yinki Lodi lodi din nan

Mikewa Nuriyah tayi tana kirma ta ce" *KaKAN GIWA* ne

Kan Giwa ya dan kaleta yayi Saurin kawar da kansa domin yar doguwar riga ce Wace da kyar ta dan fice gwuiwar ta, domin suna gama sallah suka yi wanka kuma sai suka shiga kitso, sosai rigar tayi mata kyau sannan har dan dagewa ta kara daga baya dalilin mazaunanta da suke da tudu da fadi

Ganin yanayinta ya sa murja wurga mata baban hijabi dan a zaman da take da Nuriyah da kyar ta saba da ita kanta macen ma bale a gaban namiji

Karba tayi ta saka ta dan zauna tana kikifta ido

Sai a sannan Kan Giwa ya dan sauke ajiyar zuciya, ya nufi kanwarsa gadan gadan Wace ta dan hade rai tana kalon kasa

Yana isa ya dan zauna a gefenta , a hankali ya kamo hannunta yana dan murzawa ya ce" fushi kike yiwa yayanki?

Murja ta dan girgiza kai batai magana bâ, sannan ita kanta sai ta ji ta kasa sakewa da shi, du a tsorace take tana gudun ya kara mata wani marin,

Juyo da furkarta yayi, inda a hankali ya dan taba wajen da ya mareta , abinka da farin mutun bai baje ba gaba daya, ya danyi duhu kadan, a hankali ya furta" i'm sorry dear, nayi laifi na daki autata,bazan kuma bâ

Murja ta dago idannuwanta da suka cika da hawaye tana bude baki kawai sai ta barke da kuka tun karfinta

Sai da ya barta tayi ta huce har tana sauke ajiyar zuciya inda ya kafe Nuriyah da kalo Wanda shi Kansa bai san yayi hakan ba,

Can ya ce" yanzu dai ai na baki hakuri KO? Mai kike nayi miki da zaki huce?

Murja ta tsagaita kukanta ta ce" ka dena abinda na tarda a gidanka yayana, ka aureta idan bazaka iya rabuwa da ita bâ

Bai san lokacin da bakinsa ya ce" bazan iya aurenta bâ, dan ina bukatar macen da zata baiwa yayana tarbiya , sannan ina son kasancewa da ita dan ita kawai take iya daukan lalurata, matana basa iya gamsar da ni!

A tare suka dago ido suka zuba masa , Wanda ya ankarar da shi da wa'inda yake maganar, bâ shiri ya mike tsaye a hankali ya ce " oh shuiiiit! , baby ki bar maganar nan plz

Murja ta dan murza idannuwanta ta ce " i'm sorry yayana, bazan iya barin maganar nan bâ fa, i'm 22 old, shekaruna sun isa suyi magana a kan lamarin yayana,

Ta danyi Jim ta ce" to ka kara aure, ka nemi wata matar ka kara

Kan Giwa ya lumshe idannuwansa ya ce" na kare zuwa wajen mace KO yar gidan waye da zumar na zo neman aurenta, nayi na farko, nayi na biyu, ban karu da hakan bâ, zan duba KO a wajen aikin mu ne na samu daidai ni, domin na kare da auren yarinya ta kawo min raini, duba da Nadiya shekara biyu na bata, djamila kuwa har hudu, kinga kawai zan ga sa'ata na aura may be ita zata iya da ni

Murja ta danyi murmushi ta ce" Allah ya dafa mana yayana

Ya dago da kansa ya kali Nuriyah still bata daina kalonsu da mamaki ba ya ce" ke kalon fa? Kin wani tsareni da ido?

Da Sauri ta sada kanta kasa tana kifta ido a ranta tana cewa wani abin sai yayan boko, to in bâ boko ta ratsaka ba taya zakayi irin maganar nan da yayanka? Tap

Muryarshi ta katseta lokacin da ya ce" ki tashi mu tafi na kaiki ganin kayan kawar taki

Murja tayi dan tsale ta ce" yeah , Nuriyah tashi maza mu shirya mu tafi

Kan Giwa ya danyi kwafa ya ce" minti ashirin na baki baby , bara na gaishe da tsofafin nan

Yana fita cikin gudu gudu Sauri Sauri suka shiga kintsawa inda Murja ta dage sai da ta shafawa Nuriyah hoda ta saka mata Jan baki kalar lebe mai haske, ta caje mata gira dan ta ki amincewa ta zana mata, kashin idonta ta saka mata maskara dan kuwa abin hodar ya sa yayi farifari,

Sosai tayi kyau na ban mamaki daidai ta saka abayar da Murja ta ciro a yau baka ce har kasa Wace itama tana Sakata kawai sai ta bi lafiyar mazaunanta tayi slim a jikinta

Murja ta kare mata kalo ta ce" Nuriyah, bâ daga kayan bane yake saka jikinki yin kyau haka, yannayin halitarki ce, Allah ya tsara maki abinki yayi miki kyautar kayanki, Allah ya baki mijin da zai iya kulawa da ke ya daukaka wannan halita

Nuriyah ta danyi murmushi a ranta ta amsa da amin ya Allah,

Suka fito bayan sun saka takalma ita Murja mai tsayi ita kuwa mai dan tsayi kowace sai baza kanshi take

Suna shiga falon Hajiya Hassana ta dan dakata murzawa Hajiya murja kafafuwanta da take tana dan kalon Nuriyah, Haka kawai yarinyar sai ta ringa irin tafiyar yar uwarta, KO dan itama tanada mazaunai ne kamar na yar uwarta ,

Dan sauke ajiyar zuciya tayi lokacin da suke gaishe da jama'ar falon

Hajiya hassana ta dan nisa ta ce" Babyna ga abincinku fa, ku tafi ku ci

Murja ta ce" momyna, bana jin yunwa ni dai, shin ina big broth ne? Yace shi zai kaimu gidan su freind muyi mata barka

Hajiya murja ta ce" lale yar gâta, da nice na isa ma, kuma ya yarda harda y'ata?

Murja ta ce" sosai, suka nufi kofa dan tarda shi

Suna isa suka tarar da mazan ma'aikatan du sun tsatsaya kowane a nitse harda Mubarack,
Shi kuwa *KAN GIWA* a tsaye ya bude wata mota fara kar ya dage mabudin sama, kafarsa daya a ciki daya a waje da bakin glass, sannan da waya a kunnensa yana maganar cewa zai fita aman bada yan rakiya bâ

A hankali yake kalon yanda yarinyar nan le tafiya, sai juya duwawu take dan ta ja ra'ayin maza KO? Ya Dan girgiza kai yana ayana du yan matan yanzu sun lalace

Wani haushinta ne ya kara kama shi lokacin da take kalon masu tsaron kofar Hajiya tana dan murmushi da alama da saurayinta a ciki

Ya ja tsaki bayan sun zauna yayiwa motar ky ya jata a guje ya bar harabar gidan

Ta wata hanya taga sun bilo, Kenan wancen kofar bâ ita kadai bace a gidan da kofarsa ta siri, nan da nan sai gasu a bakin titi

Wajen shan ice cream ya fara zuwa da su, inda suka zauna suna sha suna ta hirarsu shi da kanwarsa inda Nuriyah ta lura da du in suka yi ido hudu saï ya zabga mata harara sannan sai dai in bata kale shi bâ, to tabas idannuwansu zasu sarku da juna

Du a takure take, fama take su juya gida

A haka suka shiga danyin hotuna, inda murja ta dora kanta a saman kafadarsa suka yi selfi, sosai sukai ta hotuna

Sun tashi zasu tafi murja ta jawo wata yar budurwa ta ce" Dan Allah yar uwa daukan mû hoto

Yarinyar ta karba, inda murja ta jawo hannun Nuriyah Wace bata tsamaci haka bâ,ta Sakata a gefen hannun damar Kan Giwa ita kuwa a na hagu ,

Cikin wani irin tsoro ta wara daradaran idannuwanta a kirjinsa daidai shi kuwa ya kalota shima, yarinyar nan ta kashe musu hoto har hudu inda ta matso tana cewa " waouh aman wannan sabon aure ne, wly sunyi mugun kyau

Ta mikawa Murja wayar inda ta karba tana yi mata godiya

Shiru kake ji cikin motar bâ mai magana, kamar ance ta daga kanta idannuwanta suka nitse cikin na Kan Giwa Wanda ya zabga mata harara ya ce" *KO mata sun kare a duniya banga mace a nan bâ* dan haka kima daina wani kalona dan wannan inconsciente din yarinyar ta furta kazaman kalamunta a kan hoto!

Da Sauri murja ta dago tana kalonsa ta dan kalo Nuriyah ta furta ya salam, sannan ta kali yayanta ta ce.....
♀♀♀ NEMAN NA KAINA♀♀♀

Marubuciya: *SAJIDA*

□□□TAURARI WRITERS ASSOCI

(25)

Ganin irin yanda ya hade ransa ya saka ta sada kanta kasA ta dan kamo hannun Nuriyah tana dan murzawa alamar lalaba

Haka suka je gidan su kawar Murja inda yayi zamansa a mota taki shiga falon tarbar baki

Sosai tayi murnar ganinsu ta kirayi wannan su gaisa ta kirayi wancen su gaisa,
Cikin hakanan har yayanta ya nacewa Nuriyah, shi ya ga budurwa, sai turanci yake zuba mata Wanda yafi karfin tunaninta domin turancin nata ba ruwa ruwa bane

Haka suka gama a dan hanzarce dan kuwa da oga suke tafe suka fito inda Aliyu yayan kawar Murja ya rakosu yana tambayar number wayar Nuriyah

Dan murmushi tayi cikin sanyinta ta ce" banida waya

Ya dan zaro ido da alamar mamaki ya dan daga murya ya ce" sister, wai batada waya? Plz KO dai banyi mata bane? Bana cikin tsarin mazan da kike so beauty? Plz ki soni mana , duda nasan gidanku kun gaji kudi aman i swear zan cika maki mafarkinki

Nuriyah ta dan juyo tana kalon wajen murja idannuwanta tamkar su fado domin ita fa tsoronsa ma take, ita *WA*? Harda yayan masu fada a ji zasu ce suna son ta? A hankali tayi masa dan murmushi ta dan daga masa hannu danma kar ya wani bi su wajen motar ya jaza mata wata matsalar

Har sun bude zasu shiga ya daga murya ya ce" *I love u Nuriyah, zanzo gidan na yaki soyayarki*

Da Sauri ta fada motar tana haki inda Murja tayi yar dariya taci gaba da dadana tablettes dinta

Wani mahaukacin gudu ya sharara inda nan da nan sai gasu a palas *KAN GIWA*,

suna karasowa ta bude ta fice da Sauri,
Murja ta kama ta bude tare da KAN GIWA , har ta fara tafiya KAN GIWA yayi kiranta

Ta dawo ta ce" na'am big brother

Ya dan kawar da kansa gudun karma ta saka wani abin a ranta ya ce" ita yarinyar nan kowama saurayinta ne? Kowa ma kulawa take?

Murza ta kali inda ya nuna inda ta tabatar da Nuriyah yake, abin ya daure mata kai, ta juyo ta ce" big broth su wanene samarin sis Nuriyah ?

Ya kauda kai ya ce" Murja kin raina ni da yawa, taya zanyi maki tambaya kiyi min kema? Ni ina damuwa ne da irin yanda kika shaku da ita har wani kiranta kije da ur sister, karta koya miki harkar maza bâ wai na tambayeki ki tambayeni ba,

Murja ta dan nutsu ta ce" i'm sorry yaya na, Nuriyah batada samari, wani freind dina bashhh muna vidéo call ya ce ai shi yana sonta zai zo Nigeria dalilinta, aman Na-san bazata kumashi ba domin shi ba musulmi bane, saï m yayan kawarnan tawa Aliyu shi keda super market na wajen gidan zoo din nan sannan baban docter ne na fanin fata, shima bata wani bashi amanar cewa zata kula shi ba, saï.....

Da Sauri ya ce" ke ya isa haka, idan tana so du duniya su ce suna son ta, ni dai kanwata karta shiga irin hakan

Murja ta dan daga kai ta ce" insha Allah,

Ya juya yana tafiya inda Murja ta rakashi da kalon mamaki

Yana shiga falonsa ya rintse idannuwansa ya a fili ya furta" *Bazaki haukatani da salonki ba, na yarda kin hadu aman ba ke kadai ce autar mata ba, sannan abinda marasa nauyi basu yi ba na tabata kema bazaki iya ba, nafi karfinki* du cikin turanci yake wannan bayanin inda idannuwansa ke lumshe

Nadia dake tsaye cikin yaren indiyanci ta ce" huby, Allah ya sa nice ke saka ka sambatu haka?

Da Sauri ya bude idannuwansa ya sauke a kanta , ya dan hade fuska ya ce" tun yaushe kike nan? Mai kika zo nema ne? Mai kike so? Kinada bulatana ne?

Muryar mahaifinsa ya tsinto daga bayansa inda ya ce" a falon nan dakuna tara ne, tun daga sama har kasa dakunan da kowane daule da bayi da ciki da falo a wadace iya wadata, aure kayi wato raya suna ka kawo y'ayan mutane gidanka, dan haka na hana irin wannan rayuwar

Ka zabi yan aikin da zasu taya matanka kimtsa gidan ku, sannan zan Fadawa Mamana(Murja) ta dawo nan dan ina son ta sami tarbiya da dabi'u masu kyau dan tafiya zamu yi a sake duba cerclage din hajiya Hassana daga nan mu biyo ta taho da su elhaj mahaifinta da kanninta zasu zo da kansu ganin makwoncin y'arsu, sannan da su Hajiya zamu tafi dan Abama sai an duba lafiyarsa contrôle dan haka na yanke wannan hukuncin, mamana tace ita sai ta huta zata waiwayi karatunta du ba damuwa dan kuwa daman karatun mace ne

Rislan zai zauna wajen su hajiya dan kar a bar wajen ba kowa, so Son please kar naji abinda ba shi ba, a Jet dinka zamu tafi sai ka sama mana matuka kwararu kamar biyu mû je da su sannan mai kula da cinmu da shanmu ka sama mana musulma tayi shigar mutunci

Yana gama fada ya sa kai da manyan kayansa ya nufi wajen mahaifiyarsa

KAN GIWA ya juyo ya dafe kai ya ce" nonononono Dad , bana son takura Dad♀

Tôh fa, shin ya za'a karke? Enfaite c'est le début du commencement♀

Ya Allah shin Mubarack haka zaka bar wannan baiwar Allah ? Muje zuwa.....
YAYA HAYAT
(admin
Hayat hausa novels
Hausa novels and fashion
Cool novel, makeup and kitchen1
AND
Cool novel, makeup and kitchen2)

WHATSAPP NO:
+2347039625239

♀♀♀♀♀♀

NEMAN NA KAINA

♀♀♀♀♀♀

Marubuciya :. *SAJIDA*

26

Ita dai sum sum sum ta fice a falon ta bara masa wajen ta koma wancen bangaren nata dan fara hada kayanta dan ta dauki daki tuntuni kuma bata so kinibabiyar matarsa wai ita a dole wata ce ta zo ta daukar mata dakin da ta zaba domin ya fi kowane kayatuwa a bangaren

Kan Giwa kuwa kansa ya kuma girgizawa yana tarababi da tunanin rayuwa tare da matayen nan a bangarensa, uwa uba Baby da ba son zama take tare da su ba, duda tana tare da kawarta ko meye dintama wa ya sani, aman gaba daya wannan tsarin bai masa ba gaskiya

Da wannan ya tashi ya koma dakinsa ya samu ya cenza tufafinsa daga na zaman guda zuwa kakinsa ta soja sannan ya fito yana takunsa na garaje kamar yadda ya saba ya nufi bangaren hajia

A lokacin da ya shiga kusan dukan ahalin gidan sun halara a falon sunna hira sunna kyakyata daria, sai dai shigowarsa da salamar dake bakinsa cikin amon muryarsa mai ruwa da rock ya sakaa du wani wanda bai isa ya daga furucinsa yana kusa ba

yin gum da bakinsa, harma suka dan fara silalewa ya rage sai manya manyan da suka isa da shi aa zaune

Fuskarsa a hade ya dubi kaka ya ce" Hajia, ki yiwa abana magana kina ji fa dukansu zai maida min bangarena bayan bana sin hakan"

Hajia Murja ta tabe baki ta ce" Ni na ga ikon Allah, Mai gida wai waye ya maka auren dole ne bamu da labari ?"

Yana kallonta ya ce" auren dole kuma?"

Ta ce" Eh mana, dole na nemi karin haske dan a duhu nake, wani irin tsari ne wannan zaka yi bangare daban cen daban na iyalinka naka daban? Suma matayen naka walahi basu san ciwon kansu ba da suka yarda da wannan banzan tsarin, yaushema mijinki yana cen wata duniyar wace kafin ki tarda shi har bangarensa tafia ce mai tsayin gaske ke kina naki bangaren? Da wannan wace ribar zaman auren zaki ci? Na tabata babu wani abu na son birge miji da zasu ringa kokartawa sunna yi domin ba wani lamarin zuwa turaka suka sani ba"

Kan Giwa da ya hade rai sosai ya samu kansa da kallon Hajia Murja ya ce" menene kuma shiryawa zuwa Ita dai sum sum sum ta fice a falon ta bara masa wajen ta koma wancen bangaren nata dan fara hada kayanta dan ta dauki daki tuntuni kuma bata so kinibabiyar matarsa wai ita a dole wata ce ta zo ta daukar mata dakin da ta zaba domin ya fi kowane kayatuwa a bangaren

Kan Giwa kuwa kansa ya kuma girgizawa yana tarababi da tunanin rayuwa tare da matayen nan a bangarensa, uwa uba Baby da ba son zama take tare da su ba, duda tana tare da kawarta ko meye dintama wa ya sani, aman gaba daya wannan tsarin bai masa ba gaskiya

Da wannan ya tashi ya koma dakinsa ya samu ya cenza tufafinsa daga na zaman guda zuwa kakinsa ta soja sannan ya fito yana takunsa na garaje kamar yadda ya saba ya nufi bangaren hajia

A lokacin da ya shiga kusan dukan ahalin gidan sun halara a falon sunna hira sunna kyakyata daria, sai dai shigowarsa da salamar dake bakinsa cikin amon muryarsa mai ruwa da rock ya sakaa du wani wanda bai isa ya daga furucinsa yana kusa ba yin gum da bakinsa, harma suka dan fara silalewa ya rage sai manya manyan da suka isa da shi aa zaune

Fuskarsa a hade ya dubi kaka ya ce" Hajia, ki yiwa abana magana kina ji fa dukansu zai maida min bangarena bayan bana sin hakan"

Hajia Murja ta tabe baki ta ce" Ni na ga ikon Allah, Mai gida wai waye ya maka auren dole ne bamu da labari ?"

Yana kallonta ya ce" auren dole kuma?"

Ta ce" Eh mana, dole na nemi karin haske dan a duhu nake, wani irin tsari ne wannan zaka yi bangare daban cen daban na iyalinka naka daban? Suma matayen naka walahi basu san ciwon kansu ba da suka yarda da wannan banzan tsarin, yaushema mijinki yana cen wata duniyar wace kafin ki tarda shi har bangarensa tafia ce mai tsayin gaske ke kina naki bangaren? Da wannan wace ribar zaman auren zaki ci? Na tabata babu wani abu na son birge miji da zasu ringa kokartawa sunna yi domin ba wani lamarin zuwa turaka suka sani ba"

Kan Giwa da ya hade rai sosai ya samu kansa da kallon Hajia Murja ya ce " ban fahimci hausar ki ba hajia"

Hajia ta dube shi da duba irin na gaske kafin ta girgiza kanta ta ce" Kan Giwa, me kuka fahimci ma'anar aure kai da iyakinka?, Me suke yi dan neman ladan aure? Su basa kwadayin irin tarin ni'imomin da aure ke dauke da shi? Matar aure idan ta dauki tsintsiya ta share dakinta dan farantawa mai gidanta watau ta gyara gidanta ka san irin ladan da gareta kuwa?, Matar aure ko me ta yi a cikin gidanta ninkaken na idan bata da aure ne, sallarta, kai ta zauna ta yi hirar duniya da mijinta cikin raha da dukar sa kai da sauke amon muryama alkhairinta ne ita da kanta ba sai an fada mata ba, a cikin nan wanne matayenka suke yi ne? Ko su a nasu kalar al'adun ba haka?"

Kafadunsa ya daga yana ta daukan maganar tata wace ga dukan alamu sunna shigarsa hakan ya sa mama ta ce" Hajiata, su kuwa suke da al'adun yiwa miji biyaya, igbo an fada masu tarairayar miji ? Mutanen da tamkar su kwonta a kasa idan zasu ba mazajensu abu? Mutanen da har mazajenmu ke bamu tsoron cewa zafa su dauko mana yar igbo ga iya girki da ladabi tamkar bata san zafin kanta ba, haka kuma indiyawa, ba'indiye yadda ya ba kalmar miji mahinmanci ina mai tabatar maki Hajia sai kin yi mamaki idan kika gani, macen indiyawa tana iya hakuri da komai ta bika, haka kuma rayuwar aure da macen indiyawa rayuwa ce mai matukar daraja, ban san me yasa Nadiarka take haka ba, haka ban san me yasa Djamilarka take haka ba, my son ko dai kaine baka basu damar gabatar da rayuwar aurensu irin na kowace mace? Shin kaine ka hore su da rashin sannin ciwon kansu? Kai kake kin kwadaita masu tarin falalar rayuwar aure a musulunci? Kaine baka basu mahinmancin da ya wuce idan kana da bukatarsu a turakarka?"

Ido yake binsu da shi, shi ba jahili bane yana da karatu sosai haka kuma ya san litatafan adini sosai, sai rayuwa irin tasa ta business man da aiki irin nasa na rigar sojoji ya saka baya tunanin idan har yana da lokacin da zai ba mace har haka, shi idan ba lokacin da zai sauke wahalar mararsa ba gani yake bashi da wani abin tsayawa batawa kai lokaci dan kallon Mace tana shirmenta da gwalinta, su matayen nasa ai akoy kwaliya da zuba kanshi, su kawai matsalarau dai inda take rashin iya hakurin sex dinma, bai san me yasa ba

Sa ido sukaiwa junna alama domin zamansa har wannan lokacin yana sauraronsu na nufin ya ba maganar mahinmanci ko kuma yana son fahimtar maganar hakan ya sa maman fadin" Shi yasa ita rayuwa ake so idan namiji ya auri mace ya bata damar kara neman ilimi, na adini idan da hali har na boko idan ba gamawa ta yi ba, ka ga wadinnan zasu taimaka mata sosai ta yadda zaku gina rayuwarku mai ma'ana da junnanku"

Dan murmushi ya yi yana girgiza kansa ya ce" Hajaju da mama kennan, bara na dan je na dawo"

Daga haka ya mike ya fice ba tare da ya kuma karra wani lokacin a wajensu ba

Kai Hajia Murja ta girgiza ta ce" Hasana, kina tunanin yaron nan zai san rayuwa mai daraja irin ta zama da mace a matsayin abokiyar rayuwa ba wani abin daban ba? Gaba daya lamarin Kan Giwa na bani Tsoro, sai nake gannin tuni giyar mulki da kudi sun gama yi masa ilar da ba zai mori lokacinsa ba har sai lokaci ya kure masa"

Mama ta sauke ajiyar ajiyar zucia, ita da kanta rikitar yaron mijin nata na bata tsoro, watau shi a rayuwarsa mutun ne mai tabararen baki, abinda yake tunani shi

yake fadi kansa tsaye, abinda yake cikin zuciyarsa shi yake amayarwa, sai dai kuma gigitarsa na nuni da shi da kansa ba zai iya ba kansa damar moriyar abubuwa masu mahinmancin dake tare da shi ba, a sanyaye ta ce" Zai gane, ina adu'ar Allah ya hada shi da soyaya, domin har yanzu a lamarin Elhaj ban ga soyaya ba, idan har Allah ya sa ya hadu da soyaya koma me yake dawainiya da shi zai zubar ya dawo ne, domin idan kudi da mulki sunna da karfin rikita dan Adam, Soyaya tana da karfin mayar da shi mutun irin kowa, koda kuwa kurman namiji ne shi"

Da wannan suka ci gaba da tataunawa har aka sanar masu cewar su gama su fito baban filin da jirgin nasa yake domin Pilote din da zai jasu har ya karaso da takardar basu damar tashi su sauka a kasar da ake duba kafar Hajia Murja

Yan rakiyarsu da dama
Ciki harda mutanen kicin masu girman matsayi a gidan, inda kowa ka ganni yannayinsa cikin zulumi da tsoro yake na barinsu da za'a yi daga su sai su a gidan watau daga su sai mai saka masu nutsatsen nutsuwa mai sunna nutsuwa koda basu shirya ba

Hajia Murja dake rike da hannun Baby gefensu kuma Nuriyah ce tana sada kanta dan irin kallon da abokannan aikinta na kicin ke biye da ita na sakata a hali na tsarguwa da kai, gaba daya sai ta bi ta tsargu da kanta ta kasa nutsuwa waje daya sai kakawar da kanta take yi

A nutse hajia ta ce" Takwara, ki kula kin ji ko? Kin ga yana matukar tsoron zuciyarki, zan iya ce maki gwarama ni na yi kuka da ki yi, ki matsa masa sosai ta yadda zai fara sannin mahinmancin rayuwa, ina so ya iya zama da iyalansa, ya koyi raha da su, takwara ki yi hakuri na san bakya son zama da su aman idan har kika jure kika kai zuciyarki nesa zaki yi taimako ne wa mutumen dake yi maki so daya tak da ba algus, ke kin san yayanki na iya tunkarar komai dan gannin kin samu ci gaban rayuwa da farin ciki, shin zaki iya yin hakan kuwa?"

Babar Muryar da ta sanar da karasowar Kan Giwa ne ya saka dukan mutanen daidaituwa a bakin hanyar kowa ya kama kansa bayan baima idasa tahowa ba an dai fadi cewar ya shigo get na farko ne kuma sai ya biya ya dauko Elhaj da baba kafin su karaso aman a haka du aka nutsu ana jiran karasowarsa

Hajia Murja ta kai dubanta wajen Chef ta kicin ta ce" Mariam, kamar yadda kika san ana kiyaye lokutan cin abincinsa, ana dafa masa abinda ba mai a ciki dan yannayin aikinsa, Mariam ki kula idan kuka dafa masa abu da mai ya bata maku bana kusa bale na hanna dan Allah kin ji? Kuma a karra kiyaye tsaftar bangarensa da na matayensa kafin su daidaita lamuransu, idan kuka yi sanya yana iya zubar da kowa ya zuba sababi kun san halinsa sarai gashi ni din bana kusa bale na tsawatar"

Da biyaya take amsawa, duda zuciyarta ita kanta a darare take da tsoron barinsu da za'a yi daga su sai uban gidan nasu, duda ya kasance mai yawan tafia aman basa tunanin zai yita bayan ba kowa duba da Baby na gari, hakan yake saka su a cikin hali na zulumi

Karasowar motar da suke ciko ne ta katse tunanin kara daukan lamarin Kan giwa serius da Nuriyah ke yi, sosai ta shiga wani rudanin itama da tashin hankali duda Hajia na fadin ga Baby tana iya hanna shi aikata wani abin, aman ba zata manta babyn kanta ya taba keta mata marin da ya kusan sati bai baje a fuskarta ba, gaba daya sai tsoro ya karra shigarta nasa a lokacin da ta dago da dubanta ta sauke a kansa ya bude ya fito ya zagaya ya bude bangaren kakansa da mahaifinsa ya fara fitowa kafin ya taimakawa mahaifinsa ya fitar da shi cikin motar cike da kula

Magana Kan Giwa yake yi kasa kasa wace hakan ya saka mahaifinsa dagowa ya maka masa harara, wada ta saka ya dan daga hannunsa yana nuna alamun ya sara masa

Hannun ta bi da kallo da fafadan kirjinsa , gaba daya kamar wanda yake box, watau fadan nan na kakafar mazan turawa da sauransu , abin dai ba'a yi a nan wajenmu y'ayan africa sai cen wazajen,
A hankali ta janye dubanta gannin sun juyo sunna tahowa bayan ta yiwa irin tafiyarsa kallo daya tak ta sada kanta irin na yan uwanta ta nutsu, domin itama ba kowa bace a wajen nan alfarmar baby take co wace ta tabata sangarta ce irin ta shagwababu duda Baby na nuna mata soyaya ta zumunci aman tana guje ranar da zata daina yayinta ko ta koma kasar wajen da ta fito sunnanta ya dawo matsayin yar aikin da yake da, ta tabata hakan zai haifar mata da matsala idan har ta ari yannayi na yar masu gida ta yafawa kanta

Hajia Murja ce a nutse ta ce" Nuriyah?"

Nuriyah ta dago kanta , haka ya sa sukai ido hudu da mama dake ta kallonta tana ta jin wani iri a kan yarinyar, duda muguwar gajiyar dake tare da ita na tafiyar jirgin da ta yi yau ta shigo dan tana so ta raka hajia gannin likita da kanta gashi kuma a yau zasu wuce dusa mijin nata ya ce ta bari ya tarda ita cen au wuce ta ga za'a wahalar da hajiar ita ta taho, hakan bai hanna mata kin zuwa ta zauna ba , tama fi sha'awar bin yarinyar da kallo,
Sanyin halinta,
Yannayin kallonta
Irin tafiyarta na kayar mata da gaba
Sai dai tasu an ce masu ta rasu
Tasu an ce masu bayan rasuwartamaa wuta ce ta ci namanta
Tasu ko kabarinta basu taba gani ba
Ta rasu da abinda yake cikinta aka ce masu
Aman me yasa kamanin, abubuwan suke kusa da junna duda Allah kan halici bayinsa da kusan kamaceceniyar kamani da dabi'u?

A sanyaye hajia Murja ta ce" Ki kiyaye dukan abinda zai hadasa fada da wani har Allah ya dawo da ji lafia kin ji?, Na san ke ba mai fitina bace, wa'inda ke tare da ke ne auka cika fitina, so ki kiyaye lamarin KAN Giwa har Allah ya dawo da mu kin ji?"

Kai ta gyada tana kokarin maida kwalar da ta ciko idannuwanta muryarsa ta saka ta kasa rikewa ta bar abinta gudu a saman fuskarta a lokacin da ya ce"

□□□□□□□□ *NEMAN NA KAINA* □□□□□□□□□

Karashensa sabon salo

Na

SAJIDA

Muryarsa ta saka ta kasa rike kwalar dan ji ta yi kamar zai mareta tsabar ta saka tsoronsa ko mace shayinsa a ranta sakamakon irin yadda ake karra tsoratata da lamarinsa a lokacin da ya dan sake wara idannuwansa a kan mutanen wajen yana fadin" Me kuma kuke jira? Kowa ya kama gabansa!"
Dama da haushi haushin an saka shi kwana biyu da matansa a bangare daya wa'inda tunda suka dawo bangaren nasa zai iya cewa banda takura babu abinda ya tsina a wajensu, yanzun idoma ya kawo ya zuba masu dan ya ga irin nasu haukan, matan nan babu wace zata zo ta neme shi sai shine mai abu a hannu ko?, Uwa uba a yanzun da ya karaso ya baro Mahaifinsa na kokarin taimakawa kakansa fitowa a motar ya karaso wajen nan ne dan ya gazkata tunaninsa cewa basu zo wajen yiwa kakanninsa bankwana ba

Lebensa ya dan cije na kasa yana kallon yadda Mamansu ke bankwana da auta tana nuna mata maza ta tafi yayansu na tsaye , sannan ta juyo ta kamo hannun Nuriyah dake barin jiki suma suka bi layin yan barin wajen domin ga dukkan alamu ta tsorata sosai kamar wace aka kama sunnanta daban da sauran aka wanka mata mari

Da mamaki Hajia Murjanatu ke kallonsa irin yadda du ya korar mata mutanenta, sai kuma ta yi murmushi tana girgiza kanta a sanyaye ta ce" Dan Albarka, ta yiwu mu jima a tafiyar nan, ta yiwu kuma ba zamu jima ba zamu dawo, dan Allah dudai yadda hali ya kama ka riken yan amana da zuciya daya ka ji? Ka kular min da su, ina fatan muna zuwa likita yace ai da ta wayama yana iya rubutan magani mu dawo na tatali yan bayin Allahna bama kamar takwarata da kawarta sunne abin tausayi ka ji?"

Bakinsa ya dan tabe bai ce mata komai ba , watau kin yin maganar ne ya yi hakan ya sa ta shaka itama, dan ai Kan giwa ba mutun mai shiru shiru bane, yanada maganarsa daidai gwargwado

Har zata sake masa magana da hargagin da ya dace da shi mahaifinsa da tsoho mai ran karfe suka karaso sunna tafiya a hankali, ba dan komai ba sai dan jikin tsufa da ya dace a tatala a bi a hankali

Juyawa ya yi ya kama hannun tsohon ya nufi wajen jirgin da shi kasa kasa sosai yana fadin" Wai kai du inda ta yi sai ka bita baka tausaya min ne ka zauna kusa da ni mana ka barta yawo ne fa take so, baka ganninta tsaye kan kafafuwanta masha Allah!"

Murmushi ne ya fadada a saman fuskar tsohon da yi ya riko da adininsa ka'in da na'in hakan ya sa yake cikin hayacinsa sannan yake da kwari fiye da dubunnan masu shekaru irin nasa
A hankali ya sake rike shi da kyau yana dora kaffafuwansa har suka idasa hayewa suka shige ya kaishi wajen zamansa ya zaunar da shi ya daura masa belt ya daidaita sanyin saman kansa ya masa komai sannan Tsohon ya ce" Dama ina da rai ka hadu da irin tawa, dama tun ina raye na ganka a gaban macen da ta amsa sunnanta mace ? Macen dake gyara adinin mijinta, take gyara halayansa, take wasan kura da zuciyarsa, take tausayinsa fiye da kowa a duniya take tatalar arzikinsa? Ka san irin matan nan irin dadin zamman da sukeda kuwa? Takwara su fa yi masu biyaya yana zame mana wajibi ne, irin abu ne da idan baka yi ba zaka kasance a takure ne, dukantama nawa take da zan barta ta je gannin likita ita kadai? A wajena jaririyata

ce koda ita ta haife duniya, nutsuwata ce, farin cikina ce, ka ga wannan matar da ubanka ya sanyo a kanta ina iya komawa filin yaki koda kuwa bani da karfin yakin"

Shima wajen ya zubawa ido Abansa ya kawota ya zaunar da ita saman kujerarta itama a nutse kusa da mijinta ya gyara mata komai

Idannuwansa ya sauke saman hannunta da ta saka cikin na tsohon mijinta kasa kasa ta ce" Kakan Kan giwa, ina fatan kana cikin koshin lafiya?"

Murmushi ya maida mata ya ce" Kakar Kan giwa tunda kin karaso komai ya daidaita In sha Allah"

Da mamaki yake karra kallonsu irin yadda du suka ba junna kulawa ta hanyar jifan junna da lalausan kalamai masu daraja sannan suka sake maida kansu kan d'ansu dake karra jadada kar su kunna AC su bar na cikin jirginma ya isa du sunna amsa shi, gefe daya kuma sarakuwarsu mai datakon alkhairi tana nata basu kulawar daidai misali

Murmushi ya yi yana kawar da mamakinsu da kulun baya barin zuciyarsa
To shi fisabililahi bai taba haduwa da rayuwa irin wannan ba
Shi dai matan nan saima da ya zabi wa'inda ko a TV akan yawan nuno su a matsayin wa'inda suka fi kowa iya soyaya, Ba'indiya ko a labarin samari da yan mata sukan so su samu kwatamkwacin indiyawa a yadda ake hasko mana su, mai kyau ce, siririya ce, ga gashi, ga manyan idannuwa, ga kyakyawan kugu, bai san me yasa cen din yake haka ba sam....., Sai kuma a zo kan bayarabiyarsa, ko a cikin yarabawan ita din wace take da daraja ce, ba zai manta da aka zo miko masa ita a matsayin mace ba gaba daya ta ruguje ta kai kwonce sai da aka ringa mata yayafi kafin ta mike, a ranar ya gama samun nutsuwar tunaninsa cewa ya gama dace, sai dai kashhh, ba'a je ko'ina ba ya ga haza, ya ga rubutu a rubuce, hakan ke bashi mamaki, shin kowama haka yake rayuwa da matan ne? Matan gaba dayansu haka suke ne? Yanzun da wannan kakansa ya rayu har yake ikirarin a yadda yake tankwasar nan zai je filin yaki saboda kakarsa? To shi yana gannin a bariki kadai yake yin daidaya ya amshi kaya daidai misali, a barikin kanta abin sama sama ne domin idan ya ce zai karra takan firgicewa ne karrara ta nuna mutuwa zata yi ya bata dama ta shiga ruwan zafi

Riko hannunsa da aka yi ya saka shi sado kansa yana kallonta

Fuskarta ta sake sanyayawa sosai a nutse ta ce" Rislan ya ce zai dawo cikin satin nan, idan Allah ya dawo da shi ka sake rarashinsa kan maganar karatun nan ,ya yi hakuri ya koma domin ba'a fushi ka ji dan albarka?"

Kallonta yake da fuskarta dake nuni da dukkan alamu na rarashi da take masa da dadin baki dan ya rarashi yaron da ya riga ya girma ya kai mizalin da yake tunanin shi fa yama isa aure?

Dan musmushin da sam bai gamsheta ba ya sakar mata hakan ya sa ta kalli mijinta dan ya tofa wani abu a maganar,
Sai dai shima bai ce komai ba, domin gaskiya ya fara tunanin dole sai ya bar Rislan da Kharibullah din dan su ganewa junna tsakaninsu dan haka nema ya kawar da kansa gefe yana fata kar Rislan ya yi shirme irin na yarinta ya yi tunanin ai Kharibullah din yayansa ne ya dan kwatanta gardama, dan bai san abinda zai faru ba

Baki ta dan turo ta sake duban Kan giwa ta kuma fadin " Ka kula da kanka, Dukan abinda zaka aikata ka ringa duba da matanka, da kanwarka da rayuwarka kanta

wadda nan gaba burina na budi ido na ga yan dagwai dagwai sunna ja min gyale sunna min ihu a kunnena, wannan zai sa na mutu da nutsuwa a zuciyata MUHAMADU"

Murmushi ya sakar mata still da wani salo na neman fitina yana kin yi mata magana bayan ya san ta tsani hakan ya ja hannunsa da nufin tafiyarsa
 sake rike hannun ta yi raf tana sake kallonsa da tatare girarta

Fuskarsa ya juyar ya sake juyowa ya ce" Ki sakeni mana madame wai hala a cen zaki shekare ne? To bari ki ji da kika saka mijinki a gaba zaku tafi tare idan niyarku jimawa ki yi ki tataro ki dawo, domin ni dai ba zan iya da yawan maganar mutanen gidan nan ba in ba haka ba na hada su dukansu na kaisu bariki a horasu gaskiya daidai laifinka daidai horonka"

Ido mai sunnansa ya zarro , wato takwaransa sai kuma ya saka dariya irin ta nutsuwar nan yana girgiza kansa ya saka hannunsa ya raba hannayen yana fadin" Jeka abinka in sha Allahu ko mun dawo zan mayar da abata gefe ta ci gaba da ibadarta dan na kula hayaniyar gidanka na sake hada mata ciwon kai, matanka su fito su fuskanci ragamar gidan Kan giwa, fatana Allah ya sadamu da alkhairi"

Murmushi ya yi ya juya ya karasa wajen mahaifinsa ya karra sada kansa sosai mahaifin nasa na yi masa adu'o'in tsari har ya gama cikin dakewa ya ce" Abinda zan sake jadada maka a kai shine, ka kiyaye harkar zinna babana, domin ita din bashi ce, Allah ya shirya min kai ya tsare"

A samaan lebensa ya amsa da amen sannan ya sake zuwa wajen Mamansu dake daura belt itama, murmushi ya mata sosai yana sada kansa a ladafce kamar yadda ta siyawa kanta mutunci a wajensu sakamakon zama da ciki daya da take yi da su a matsayinta na matar mahaifinsu ya yi mata fatan alkhairi, inda ta bishi da adu'a hankalinta kwonce ba wata damuwar ta bar yar autarta a nan, asalima ta sani ne soyayar da yake yiwa auta ta musaman ce, yar kanwarsa ce, autarsa ce, ririta abinsa yake yi son ransa dan a kan auta yana iya rufe ido ya ja masu ba daidai ba

Bai sauka ba sai da ya karasa wajen matuka jirgin su biyu dake zaune sunna dan taba hira dan sun gama duba komai a tsare yake shi suke jira ya fita su daga
Murmushi ya masu bayan sun yi musabaha a nutse ya ce" GENERALS Allah ya sauke ku lafiya"

Da wannan suka yi salama da junnansu ya fice ya yi nesa sosai yana tsaye hannayensa duka biyu cikin aljihunsa yana kallon yadda suka yi tafiya saman doguwar hanyar da ya yi ta bayan gidan nasa wajen jirgin da yake tafiya kafin ya cira har ya cira ya tafi sannan ya sauke ajiyar zuciya yana sake bin jirgin da kallo har ya bacewa ganninsa

Juyowa ya yi a nutse yana tafia
Shi tafiyarsa yake yi dan ya karasa bangarensa domin fita yake son yi duba da yamma ta sanyo kai yana da wajen da zai je, su kuma ma'aikatansa na faman dudukawa dan su gaishe da shi da sauransu, sam bai wani damu da hakan ba dan hankalinsa ba a kansu yake ba, shi baima taba lura da tarin tsoronsa da suke ji ba a rayuwa, yana rayuwarsa ne yadda ya dace ta zo masa, yana aiki yana kuma kasuwanci, yana mu'amala da mutane masu yawa da suke kasansa da kuma da yawa da suke daidai da shi, haka kuma da wa'inda suke sama da shi
A mu'amalarsa da wa'inda suke sama da shi kuma babu maganar tsoronsu ko yi masu biyaya dan dole, ana girmama junna a ilimance, shi ba mai zama bane ko daya, baya zama a gidan na lokaci mai tsayi, idan ya yi tafiyarsa sai ya dawo, idan ya dawo

yana fita nema, mutanen dake tare da shi suka fi daukaka lamarinsa ta yadda idan ya zo wucewa akan duka har kasa a gaishe shi ko a yi gagawar nutsuwa da dukkan abinda ake yi dan a bashi girma

Hannun kofar bangarensa ya kama ya murda ya shige kansa tsaye yana dan dage hannunsa da cusawa cikin gashin kansa

Turus ya yi yana kallon tsaitsayen da aka yi tsakanin su hudu, tsayuwar da ta nuna matakin kowa a gidan, kama daga su da suke da shi da kanwarsa mai shi, sai kuma yar aiki zai kireta ko abar kaunar kakarsa dake gefe tana tsaye kamar wace ta aikata wani laifi domin tsayuwar tata wata iri ce kuma a gefe take sosai

Nadiya ce ta fara dubansa da rantsatsen turancinta ta ce" Ur excelency Murja ta ce Grandma tace a nan zata zauna, wai kuma sai tace harda wannan yarinyar....bayan muna da masu aiki sun wadacemu bama son karri?"

Da mamaki ya zuba masu ido yana yaba nasu sallon rainin wayon, watau basu san cewa ya yi mamakin rashin ganninsu a wajen yiwa kakanninsa salama da mahaifinsa ba harma ya kulace su kuma shine Nadiya zata kama sunnan kaka gatsau haka dan rashin kunya? Kai da ba dan sunnan tata kakar a cikin hinduma tsofafin sunnaye bane da idan wuka za'a dora masa a wuya a yanzu ba zai tuna yaya sunnan yake bama bale har ya kama kai tsaye da ya kwatanta, aman zai binciko ko dan ya kama ya sani sarai sai ta yi kamar zata kifa dan sunna girmama nasu sosai

Su kuwa matansa su dukansu biyun fatansu ya amince cewar Nuriyah ta koma bangarenta , watau dakinta ta yi rayuwarta har wace ta daure mata ta dawo, domin su a kankin kansu daga ita Nadiar har Djamilar basu taba jin wani abu a kan mu'amalarsa da matan da yake yi jefi jefi irin Tsoron zaman yarinyar a bangarensu ba, haka kawai aiki irin na shedan ke son rikita su a kan maganarta bayan su din sun gama gane cewa mijinsu dole sai ya samu karri sama da su shi yasa suka watsar da mu'amalarsa da izabel a kwondon shara suka gwamace kishiyar waje fiye da ta gida dan ko ba komai sun fita daraja su kam kuma du iskancinta bata isa ta zama mata a wajen only one Kan giwarsu ba, su biyu ne suka ci zaben daga su kuma ba karri

Tun daga kasa har sama ya bi jikin nadiya da kallo , cikin shiga take na wando sakake sosai har kasa budade ne sosai wanda iya kugunta ya rike, sai rigarsa wace iya mamanta ta rufe hakan ya sa cibiyarta da shafafen cikinta ke waje harda dan kunnen dake cikin cibiyar nata a bayane wanda ya dan zirro kadan har kusan wandon dake jikinta

A hankali ya sake maida dubansa kan Djameelarth itama yana kallon shigarta, ita kuma tana sanye ne da sket da riga na atampa, wa'inda suka amshi jikinta ta nada wani katon dauri a saman kanta wanda baban mamakinsa da kuma abinda yake son ganewa zanni nawa ne ya mata daurin nan, sai ya maida kan Baby dake tsaye watau Murja karama auta ita kuma ta yane kanta da dan kwali tana rike da tsatsonta tana jira ta ji me zai ce, domin ita dai a gabanta ai kaka ta ce su zauna a nan kau? Idan kuwa ya kori Nuriyah saboda wadinnan ababen zata bita ne su zauna domin ita ba zata bar yar mutane ita daya a cen ba, sai kuma ya juyo wajen da Nuriyarr ke tsayen itama kanta a kasa har kamar ta dan karra matsawa ta rakube a dalilin shigowar tasa

Tun daga kasa har sama itama ya bita da kallo a lokacin da ya samu kansa da sake bin cinyoyinda dake cikin doguwar riga da kallo yana mamakin wannan yarinya ko me yasa take anfani da cikon nan irin na kanti da ake siyarwa? Mata kam wani sa'in

yakan rasa me yake damun wasunsu, to wanann gabjejen abin ai sai ya hannaka zama da kyau, ita zata iya daukan wannan abin ne? Hmmm yarintahhh zalla
Sai kuma ya tabe bakinsa da ya sauke kan hijab din dake kanta madaidaici ya juya ya nufi dakinsa ba tare da yace ku ci kanku ba

A tare suka raka shi da ido daga su nadiar har Murjanatu baki da hanci bude, domin a tunaninsu su dukansu ai ihu ya dace ya dan masu ko yayane ya kuma fada masu su fita a idannuwansa ya rufe baya son shirme, sai kawai ya tafi ya barsu bayan fada ne ake shirin yi?

Djamilar ta taba hannunta tana kallonta ta ce

□□□□□□□□ *NEMAN NA KAINA* □□□□□□□□□

Karashensa sabon salo

Na

SAJIDA

Djamilar ta taba hannunta tana kallon Murjanatu ta ce" u see, ke baki san komai ba, ke yarinya ce karama, baki iya komai ba, kin ga bamu da matsala da ke, ke kanwar wanda ya auremu ce, idan kyakyawar mu'amala ba zata shiga tsakaninmu da ke ba bama so ki zamto abokiyar hamayarmu domin komai na iya faruwa ciki.....mun gama shawara da ni da Nadia cewar mu biyun mun isa, bamu hanna masa kula wasu a waje ba dan yana da damar hakan, aman wannan yarinyar da ban san a ina aka samo bahaushiya mai hausa da kuma kamaninta ba ba zata zauna mana a bangare ba koda na second daya ne, ta tafi kawai, wai acema du fadin palace din nan sai a nan zaku zauna?"

Murjanatu ta hadiye jin haushin da ta kumsa na yayanta gannin bai yiwaa wadinnan mutanen magana ba da mamaki tana kallonta ta ce" Kina nufin, kun gama yankewa kanku hukunci ne a zamantakewarku da shi cewa yana iya bin wasu bayanku a matsayin da ma muharamansa ba?"

Kai ta gyada cike da bata tabacin hakan take

Murjanatu ta tafa hannu tana fadin" lalle yau na sake yarda cewa an tafka asara mai girman gaske ta lokaci da dukiya wajen ajiye abinda ba shi ba, ba zan ce da ku komai ba a kan décision dinku domin da hakoranku na ganku, abinda zan fada shine in sha Allah ba dai ya ci gaba da abinda kuka zabar masa ba , Allah kuma zai bashi

mai sonsa mai kishinsa wace zata guji ya mutu ya fada wuta sanadiyar aikata alfasha bi izinillah, ku kuma zaku girba kuma daidai da shukarku, zama kuwa daram a bangaren nan sai na ga wace zata hanna!"

Juyawa ta yi ta damki hannun Nuriyah dake kallonta da mamaki tana tunanin da itama ta iya fada har haka

Ido Nuriyar ta zarro gannin ta jata ta nufi wajen dakunnan tana bankadawa tana lekawa sai ta janyo ta rufo ga dukkan alamu tana son bambance nasu da wa'inda ba mutun a ciki ne

Daga inda suke sai ya zamto kururuwarsu ce ke tashi, ita ibo dama ba zata yi fadan gigayar jiki ba ana zaman lafiya, bale a je kan ba indiya da bata tashi da wannan wasan ba sam, sai suke ta kyruruwa irin daidai wace suka fi kwarewa a kai sunna biye da su da kokarin dakatar da su bama kamar idan Nuriyah ta juya yadda ababen bayanta ke rawa kamar tana luluka masu ashar ne da su da gangan

Sake budewa ya yi ya fito da shiga irin ta riga da wando dogo, ita rigar mai dogon hannu ce a balla boturan cen jiki na hannayen ne yake dan kokarin balawa aman ya kasa

Wajen da Murjanatu ta nufa zasu shige dakin da ta gama yarda cewa nanne wanda suke iya zama ya nufa yana fadin" Auta bala min"

Da sauri Nuriyah ta koma gefen daya hakan ya sa mazaunen sosai suka juya a cikin doguwar rigar irin juyawa mai ma'anar nan wace ta saka idannuwansa suka kai wajen ba tare da ya aikesu ko ya san zasu iya kallon nan din ba

Dan kasakai ya yi cike da mamakin to dama abin cikon ana siyar da mai ruwa ruwa wanda zai ringa abu kamar na gaske? Kai yarinyar nan du inda taa fito ta yi rashin ji sosai

Murjanatu ta kama hannun rigar tasa ta bala masa boturan nan da kyau bayan ta juyar da shi yadda ake masa, sannan ya sake juyawa yana kallon yan matan matayensaa dake tsaye cirko cirko su dinma shi din suke kallo ya bata dayan hannun shima yana dan gyaran murya kadan dan sake sakin muryarsa sakamakon ruwa mai sanyi sosai da ya sha

Tana gama bala masa ta janye hannun Nuriyah suka shige cikin dakin ta maro kofar da karfi sannan ta saki hannun Nuriyah

Ido ya zubawa kofar dan harga Allah marowar kamar ta kwala masa dutse a kansa ya ji kafin ya dan rintse idannuwan nasa ya juya ya fice a falon gaba daya

Nan fa suka dora nasu meeting din na cewa lalle lalle wannan abu ba zai yiwu ba, su din matansa ne sunna da daraja fiye da wannan sangartaciyar kanwar tasa
Su mamakinsuma da ta mako masa kofa aman dan rashin adalci bai ce mata komai ba
Duda sun kula kamar yana da wajen zuwa mai mahinmancin da ya sa bai tsaya kula su gaba dayansu ba, aman kuma yana da wani hali irin na yankan tsagwaron wulakanci dake iya raya masa cewar ya yi watsi da shirmensu, shi yasa suka kasu suka rabu suka tsaya a kaan matsayar lalle lalle zasu yi jiran dawowarsa idan ya gama dukkan abinda zai yi su sake gabatar da muradinsu na a fitar masu da yaren nan a bangare, ko ba komai yana da dabi'ar dane mace a falo fa, shin yaya zai yi idan hakan ta raya masa ga su Murja a gefe? A yadda yakr kakau da tarbiyar

yarinyar yadda yake hannata aikata komai sun tabata ba zai so ta ganshi a yannayi irin wannan ba....da wannan suka rufe suka tashi suka koma kowace ta shiga lamarin gabanta na abinda zai karrata, ba tare da sun kula da harkar girkin abincin da zai dawo ya tarar ba, sun dai san idan lokacin hawa table din ya yi za'a hau koda ba'a so ne, idan yana ra'ayi zai ci, inma baya yi zai bari, su din kansu basu riga sun daidaita zama irin na haka da shi ba,, sai yanzun dai koma meye za'a yi

A sanyaye Murjanatu ta karasa kusa da kujerar da Nuriyah ke zaune tana maida numfashi ta zauna itama ta sauke dubanta kasa zuciyarta cike da daci, tana jin daci har cen kasan ranta , tana tunanin shin da ace mahaifiyarsu na raye zata kyale kan giwa aikata irin haka kuwa? Zata bari matansa su saka shi a hali irin wannan kuwa? Shin yaya zata yi ta samo mafita wa yayanta? Yaya zata yi ta gyara lamarin yayanta?

"Na shiga ukunna, ta yiwu kafin Hajia ta dawo ya koreni, Innalilahi wa inna ilaihi raj'une me yasa matansa basa so na zauna ne? Ni kam Sis da kin barni na koma cen din sai na labe har Hajia ta dawo sai na fitowata hakan zai sa a manta da ni kwata kwata ba wanda zai kore ni, auta idan na fita daga nan ina kuma zan dosa.....?"
Maganar take yi a harhade tana dan jimke cinyoyinta dake nuni da abin daga zuciyarta yake, subutar baki ne ta yi tana fada mata tsoronta firgicinta da kuma muradinta na kasancewa a nan din , watau a cikin gidan hakan na nuni da tana tsoron komawa nata iyayen
Wannan sai ya dan bata mamaki, ita dai ta san wanda ya kawota gidan nan ya ce ne ita din yar uwarsa ce watau Sabiu daya daga cikin ma'aikatan gidan wanda ya yi sanadiyar kasancewarta a gidan

A sanyaye ta ce" Nuriyah?"

A dan firgice ta dubeta, sai kuma ta ankara da abubuwan da ta fada din
Da sauri ta mike ta shiga yayumar abinda aka shinfida saman gadon tana fadin" Bara na tsaftace kayan nan dan ba zamu kwonta saman su ba ko?"

Murjanatu bata ce da ita komai ba tana dai kallonta har ta shige bayin ta karasa bangaren da washing machine take ta hada komai ta saka ta kunna sannan ta ci gaba da tsaftace bayin duda ba wani dati ta yi ba sai kura dake nuni na ba'a anfani da ita

Sai da ta gama tsaf sannan ta sake fitowa ta kuma tarar da Murjanatu zaune an kusa yin kiran sallar magariba

Murjanatu ta sake gyara zamanta ta ce" Zo ki zauna"

Nuriyah sai ta samu kanta da tsayawa tana kikifta ido tana kallon Murjanatu, ita dai ta dan girmi Murjanatun aman a yadda ta yi maganat a dan dake sai ta ji shayinta na neman kamata, jinnin dake yawo a jikin yarinyar irin na yayarta ke sakata rikicewa lokuta da dama ta dauko hali irin na riginar yayanta

A hankali ta zauna tana fuskantarta ta ce" Baki ga lokacin sallah na gabatowa ba gashi bamu kawo suturunmu nan din ba?"

Murjanatu ta ce" Kin manta na tashi da kwana daya da bako kika tashi da shi? Ko ke a kwana daya yake dauke maki?"

Yawu ta hadiye tana lumshe manyan idannuwanta tana tunanin yadda zasu kwashe

Murjanatu ta dan muzguta a hankali ta ce" Ki bani labarinku mana.....?"

Gabanta sai da ya kwonci kwonci ya fadi, hankalinta ya nemi tashi
Labarin nata ta ringa maimaitawa a samab lebenta tamkar wace take son ta sake gane me yaren yake nufi ba

A hankali Murjanatu ta kama hannayenta tana kallonta ta ce" Tunda na zo gidan nan nake son fahimtar da wace takarda kika shigo a matsayin mai aiki? Sai da grandma ke fadan cewa lalalalaalalala baki karanci karatun girki ba, ita dai yaron nan Sabi'u ta yarda da tarbiyarsa ya nemi ya kawo yar aiki ta kuma amince, sai na ringa tunanin to yaya aka yi haka? Nuriyah tl me, ki dan bani labarinki mana idan ban takuraki ba?"

Nuriyah ta lumshe idannuwanta hawaye na neman kwace mata, a hankali ta ringa shanyewa, sai dai abin na neman fin karfinta, da sauri ta sake sada kanta tana ambaton sunnayen Allah a kasan zuciyarta kafin ta fuskanci Murjanatu cike da rauni ta ce" Da ace zan samu, da zan samu da kin bar maganar son sannin ko ni wacece, domin ina tsoron sannin hakanan ya haifar maki da tsanata fiye da kima dan ina mai tabatar maki cewa zaki kyamaceni fiye da tunaninki"

Da mamaki Murjanatu ke kallonta har bata san lokacin da ta furta cewa" Subahannalah, kisan kai kika yi ko shirka da har kike fadin irin haka?"

Da sauri Nuriyah ke girgiza kanta, sai kuma ta sada kanta saman cinyarta tana mai shashekar kukan da ya kwace mata

Jikin Murjanatu ne ya yi sanyi a hankali ta shiga shafa bayanta tana fadin" its ok Nuriyahrtahhhh, dainan kukan haka na bari na bar tambayarki labarinki kin ji?"

Da sauri Nuriyah ta dago tana sake yin shashekar kuka ta ce" Ba zan daina ba Murjanatu, zan fada maki domin kema kin kasance mai min adalci a rayuwa, bakya kyamatata kamar yadda hajiya ta amshe ni take kuma kamanta adalcin rayuwa a gareni bayan bata san takamaiman wacece ni ba, Kin ga ni ba jinnin Sabi'u bace, shima yana daya daga cikin mutanen da suka taimakeni suka yi min adalci a rayuea suka bani damar rayuwa tamkar kowa ta hanyar nuna min rashin karatuna ba zai zamto ila a rayuwata ba tunda har inada hardar alkur'ani daidai gwargwado kuma ina da hadisai zan ci gaba da neman ilimi a nutse aman tunda ina da zuciyar nema na nema dan na rayu.....Auta a rayuwata ni ban rayu da kankara hakori a abin hannun kowa ba, ban rayu da jiran sai an bani ba, marikiyata uwata kuma kakata wace ta min adalci a rayuwa ta rikeni har ta koma ga ubangijinta wace ta fadan cewa Mahaifina shine mutumen dake korata tamkar kare baya so na rabe shin nan ta koyan nema, ta fada min cewa duniya tun kafin ya zo yanzu, watau tun a da idan kana son wulakanci to fa ka dogara da abin hannun mutun .....ta kare fada min cewa ko iyayen da suka haifeka suka kawoka duniya daidaikunne zasu ci gaba da yiwa yannayinka uzuri da zarar ka yi girman da kake iya cinye kwano daya, ta fadan cewa sana'a ba laifi bane, da sata gwara sana'a da zubar da mutunci gwara sana'a, ta ce min Nuriyah ki tashi ki *NEMI NA KANKI* dan duniya ta dawo ko zaman lafiya baka samu da mutane sai kana dan lasa masu, ba wai maganar rashin kauna bace ko wani abin, lamarin ne ya zo a haka koda ba'a sonka ba za'a kasheka ba, kuma ana iya mu'amala da kai, aman ko a gidanku mai shi shine baba koda kuwa shine auta....., Auta ina ta ce da ni riba komai kankantarta itace alkhairina, sannan na nema dan ciyar da cikina ba dan na tara na yi matashin kai ba.....bara ki ji labarina a iya abinda na sani gaskiyar wacece ni.....SUNANA *NURIYAH* mahaifina kam takamaiman wanene din ban fahimta ba tukunnan, na taso a hannun Inna

Baraka....." A nan Ta kwashe dukan labarinta ta sanarwa Murjanatu, wace ta yi wani irin kasakai take kallonta cike da mamaki da al'ajabi har ta dire aya

Kukan da ta fashe da shi ya saka Murjanatu mikewa da sauri ta rungumeta a jikinta tana rintse idannuwanta itama muryarta na rawa ta ce" Ki yi hakuri Nuriyah, kowani bawa na fuskantar jarabawar rayuwa, aman lamarin Lawali da inna tace shine mahaifinki na bani mamaki, shin da gaske haka ne? In haka ne ganganci ne ko rashin jin Tsoron Allah ya yi tasiri a duniyar Lawali har ya aikata haka? Subahannalah Astagfrullah wa atubu ilaikah , ya salam....."

Kanta ta dago tana kallon Murjanatu da mamaki ta ce" Baki ji ba? Marikiyata cutar HIV ce fa ta kasheta, Murjanatu wannan dalilin ya sa idan aka ji ake guduna"

Tausayinta ya sake cikata, a hankali ta sake rungumeta a jikinta kafin ta saketa ta zauna tana fuskantarta ta ce" Cutar HIV ko ke kike dauke da ita Nuriyah an samu ci gaban da za'a zauna da ke a rayu da ke cikin mu'amala tsaftataciya, ke bara na kare maki ki yi aure ki hayayafa har sia wa'adinki ya cika zaki bar duniya, wa'inda suka jahilci abim ne suke ci gaba da jahiltarsa, ba zasu taba daina jahiltarsa ba .....now stop crying, na matsa maki har na tuna maki rayuwarki ko? Allah ya jikan Mama idan kuma tana raye Allah ya bayana mana ita, Allah ya bayana mana ahalinta, idan kuwa babu rabon ganninsu Allah ya sada mu a aljanah, aman ba zan kuma barinki ki yi kukan kadaici ba ko na rashin gata, Allah ne gatanki....mune ahalinki, ko aure kika samu in sha Allahu mune danginki ba zaki yi maraici ba!"

Abin ya yi mata zuwan ba zata hakan ya sa take YIWA Murjanatu kallo mai girman gaske har zuwa lokacin da wayar dakin ta dauki kuka

Murjanatun ce ta mike tana fadin" Nadia da Djamilarth take ko wa sunna sak gayanan aman su ibo sun karkata shi walahi idan balaki suke nema zasu samu da ni suke maganar!"

Tana dagawa da niyar a kwasa ta daga sai dai muryar da ta ji da umarnin da ya bada ya kashe ya sakata hadiyar yawu ta cewa Nuriyaj tana zuwa

Ita dai da ido ta bita tana tunanin Allah ya sa kar a yi wata rigima a kanta a gidan, Allah ya sa su ganewa junna a samu sasanci ta koma cen ita ta fi sakewama

Tunda ta tunkaro Falon sai da ta ji ta sare sanadiyar wayar da ta tsinkayo yana yi da Rislan

Tana karasa zama a saman cafet kamar yadda matansa suke yana dire maganar da fadin" Rislam ? Gobe in sha Allah karfe goma na sameka a gidan nan!" Kittt ya kashe yana fadin " Baku isa ku hadani da ciwon kai ba y'ayan gidan nan !"

A lokacin ya sauke dubansa kansu baki dayansu
Da daidaya yake kare masu kallo kafin ya yi gyaran murya , ya ce" Kika xe me dangane da zamansu a gidan nan?"

□□□□□□□□ *NEMAN NA KAINA* □□□□□□□□□

Karashensa sabon salo

Na

SAJIDA

Page.
29

Kana kallonsa ka ga wanda ya shirya a mutu ya ce" Mema kika ce dangane da zaman yarinyar nan a nan?"

Yawu ta fara hadiya dan ta kula da ita za'a fara kai lomar, hakan ya sa ta shagwagwabe tana neman fashewa da kuka

A dake ya ce" Murjanatu, kina ji? Ina so ki hadiye kukan nan har ki gama min maganar da ta dace , wace hankalina zai dauka, na rashin kunya da cece ku ce da kika yi da yayunki bayan mamanki dai ai tarbiya take baki, idan ta ji yaya zaku kwashe? Fada min wace kika dage kika kirta rashin kunya a kanta me yasa?"

Sai da ta sake hadiye yawun bakinta sai kawai ta saki kukan tana rike kirjinta hankalinta tashe ta ce" Marainiya ce, marainiyar Allah da annabi, gatanta Allah, shikenan dan Allah ya kawota cikinmu sai a wulakantatata? Na ce mata kai din babana ne, kuma zaka kasance babanta, zaka bada aurenta zaka tsaya mata, shikenan sai suce ba zata zauna ba? Me yasa ba zata zauna ba? Me ta masu ne? Na ga dai da dakunna kuma bata da matsala bata shiga harkar kowa? Bamdama rayuwa da kirki ya yi karanci yayanmu kai din ai uban marayu ne ko?"

Da hausa ta yi maganar har ta dire, hakan ya sa ita Nadiya bata gane komai ba sai Djamilart ce ta yi gagawar fadin" Ke Kan giwa ba uban marayu ba, ba uban wannan katotuwa ba, yana iya cinyeta da....."

Da karfi yana fido idannuwa jin zata kwala abinda ya tabata sai ya yi Jiri a gaban kanwarsa yar jaririyar kanwarsa da bata san komai ba sai ta ci ta yi barci ta yi rigima ta yi sallah tana neman tafka aika aika ta hanyar cewa shi shi shi kan giwa yana iya cinye wancen abar fisabililahi wannan ai zubar da girmansa ne da darajarsa za'a yi ya ce" ke ke ke ni uban marayune mana, kuma ni babanta ne, ke tashi jeki koma daki za'a kawo maku kayanki, aman kar na kuma gannin hayaniya tsakaninki da su yayunki ne fa"

Ita dake kuka sai kuma ta zarce da dariya harda dan tafawa ta yi gaba bayan ta sake gode masa tana murna, dama ta san yayanta fa ba zai zuba mataa kasa a ido ba walahi ta yi tafiyarta

Da matsanancin mamaki yana kallon Djamilar ya ce" Karasa maganarki ina iya me kika ce?"

Djamilart ta sauke ajiyar zuciya na bacin rai ta ce" Yanzun shine ka nuna mata bamu da mahinmanci? Shine ka nuna mata ka fi sonta a kanmu? Wannan yarinya idan muguwa ce tana iya sakawa ka ci fa....."

"Innalilahi " ya fada kasa kasa yana sake fuskantarta da kokarin hanna kafarsa da ta fi kusa da ita habreta , ba dan komai ba sai dan son da yake ya YIWA kansa waazi cewar bata da hausa ya dace a mata uzuri idan tana wasu magangannun rashin hausa ai matsala ne

A dake yana hararta ya ce" Ke tsaya wai na ci me?"

Sai da ta kalleshi da kyau sannan ta ankara harararta yake yi fa?, Dan haka sai ta ringa dan kame kame kafin ta ce" Ita wancen din nake cewa ka....."

" Muhamadu rasulullahi sallalahu alaihi wa salam, Djamilah idan kika karasa wannan sabon sai na karya miki wuya da harshe na huta da ke , in ban nadeki ba ki ce min ni ba dan babana bane!"

Shiru ta yi kamar an yi ruwa an dauke tana kikifta ido tana kallonsa

Gaban goshinsa ya dafe cike da takaicinsu ya maida yaren turanci ya ce" Yanzun tsakaninku da Allah dama abinda kuke tunani a kaina kennan shi yasa kuka tsaya dan rashin kunya kuka ringa min ihu a kai dazu? Kunna da hankali kuwa? Yarinyar nan gaba dayanta bata tafasa ba bale ta kone, nawa take? Da wuya idan ta fi baby fa? Shine kuke min wannan abin? Kuma kun kasa bale wancar abar? Yanzun dama abinda ya saka kuka min hayaniya kennan a wannan yarinyar mene abin duban da har zaku min wannan wulakancin? Ko na maku wani abu ne? Kai a mema kuka dauke ni ? Ga dan duniya ko?"

Nadiya ta dube shi da mamaki tana fadin" Husband, ba haka muke nufi ba fa, ka san dole mu ji tsoro ka sani sarai yaya aka yi aurenmu, yanzu haka idan aka ji ka min kishiya ai na ji kunya, bale a ji biyu?"

Da takaici ya ce" in na yi niyar aure hanna ni zaku yi ne? Bama wannan ba mema ya kawo daga sun zo ku yi wannan tunanin a kansu?" Ya karashe a kausashe yana sake hararsu

Djamilah ta ce" Kai baka ga kyan yarinyar tamkar aljannah ba?"

Nadia ta dora da fadin" Baka ga bombom dinta ba yadda suke ko a cikin riga?"

Da ido ya kakafe su da mamaki ya ce" Cikon kuke yiwa hauka? Ina ruwana da kyanta ne?"

Summa da mamakin da wawanci Nadia ta ce" Wani irin ciko? Wannan abin fa duka nata ne! Ai ni ina tausayawa tsufan yarinyar dan abin ya mata yawa sosai walahi!"

Shiru ya yi ya zubawa Nadia ido, gaba daya shedan ya dauki tunaninsa ya kaishi wani wajen daban da ba zai so yan saka ido su san me ya tunana a wannan lokacin ba, har sai da ya ringa jin hayaniyarsu sama sama ga ciwon kai da ya kumso domin a cen dinma hayaniyar ce suka sha ta mamaki ya dawo ya dora da su, dan shi a yi a karra yi ba isarsa take yi ba, hayaniya kuwa da bakinsa shima ya iya bale a gwadawa soja kayaniya ne? Ai sai yi kawai abin ba'a cewa komai

Ajiyar zuciya ya sauke yana fuskantarsu ya ce" Ku saurara, ya zama wajibi ku gyara muamalarku, zamantakewarku da komai , domin kanwata na tare da mu ba zan so ta dauki dabiunku ba, zan so ta yi koyi da na kirki idan kunna da su, sai magana ta gaba Nadia da Djamilarth me ya hanna ku zuwa yiwa dangina bankwana ? Sannan

ke Nadia dazu na ji kin kama sunnan Murjanatu kai tsaye bayan ni take kakata ke sarakuwarki ce? Ba dan karrama? ?"

Inda indar da suka fara ya saka shi gane son rai da tsabar jin dadi ya saka su aikata haka, dan haka ya mike yana mike tsayinsa ya yi mika sosai gana godiya ga Allah sannan ya nufi dakinsa yana tafia irin ta ingarman namiji ga lamura sun nuna kansu sosai da sosai

Da ido suka bi shi jiki a sanyaye Djamilar ta ce" Mun shiga uku, bai mana ihu ba, gwara ya dawo ya mana da ya mana shiru, na tabata zai rama ne, kar mu je garinmu ya gaida Baba a tsaye in shiga ukunna"

Nadia ta sake talabe habarta tana fadin" Ke da sauki, kar nima mu je ya ki neman albarka a kafafuwan nawa dangin, ina zan shiga da raina, tashi ki je yau ai kwananki ne"

Da mamaki Djamilar ta kalleta ta ce" Kwanana kuma? Inace jiya nice aka ce kwanana ko?"

Nadia ta ce" Eh yo ai bibiyu zamu ringa yi"

Djamilar ta ce" Ke muguwa ce, ba inda zani, a yau da muka saka shi magana shine zaki tura ni ya sauke min komai ko? Kema jeki mana ai kin san hanya aman ni kam ba zan iya daukan abin cen ba!"

Da wannan ta barta zaune a wajen tana kallon dakin da ta shige

Ajiyar zuciya ta sauke tana tunanin rayuwarta tun daga bakin nunawar da ta yi cewa zata gudu da shi da irin abubuwan da suka faru
Gata dai a nan din bata rasa ci ko sha ba, sai dai gaba daya mutumen da take aure ta yi nisa da shi dan wasu lamura da suke faruwa, a gaskiya a rayuwa ta fi so ko meye a tsaya iya romance, shi kuma sai aka yi shi wani irin mutun mai tafe da rashin yarda da wannan kuduri nata ba, ko yaya aka kai ga taba junna sai ya yi yake samun nutsuwa, shi yasa bata yi wani tashin hankali ba da zai karra aure a tunaninta cen matarsa zata ringa amshe wancen lamarin ita kuma iya romance ya isheta, dayan tashin hankalinma a kan haihuwar ne, tunda ya kama maganin hanna haihuwa a dakinta yake bibiyar lamarinta, ita kuma tun daga ranar take taka tsantsan da dukkan wani ruwa mai iya komawa dan mutun a cikinta, idan ta kalli shafafen cikin nan nata tana iya rantsewa zuciyarta ce zata buga idan ya zama kato, kai ita fa sam bata son haihuwa to a kan me ba zai yarda da haka ba? Wadinnan abubuwan na matukar wahalar da ita.....

A bangaren su Nuriyah kuwa kusan karfe takwas har sun gama komai sun kwonta, danma Murjanatu na faman vidio call da mamanta wace sai da Nuriyah ta yi barci maman nata ta yi kiranta hakan ya sa basu gaisa da Nuriyar ba, aman kuma ta sha hirarta domin atafau take bata labarin ga y'ar uwa ta samu mace maman nata zata zamto mamansu

Ita kam murmushi take ta binta da shi kafin su dora da wata hirar, ta ringa jadada mata kame kai, rike mutuncin kai, sannan ta sake jadada mata ta yiwa yayanta biyaya da matansa ta yi hakuri kar ta bata masa rai ya karyata a banza a wofi, ta bari ta tardota rasss ba a karye ba.....da wannan suka dan cika dare sunna hira kafin tai mata salama da adu'ar kwonciya barci tamkar baby karama ta kwonta tana murmushi da godiyar Allah tana sake farin ciki da tunanin cewa ko mahaifiyarta na

raye iya haka dinne zata iya samu, matar na binsu da zuciya daya, idan ta ji ana cewa matan uba mugwaye ne sai ta ce ba duka ba, akoy masu zuciya daya, masu yi maka son da suke yiwa babanka, ai ita a ganninta idan matar uba ta ki son y'ayansa to ahine bata so, su dai sun dace sai godiyar Allah

_____

Washe gari kamar yadda ta kware wajen sauko a cen bangaren hajia, hakan ya kasance a bangaren nanma
Ta fito ne da shigarta ta mutunci, zani da riga ne a jikinta sai hijab dogo wanda ta nade shi ta shiga dan aikace aikacen gyaran falon domin kicin din a rufe take ruf dan ba'a fara girki a nan ba Kan giwa yace baya son kai kawo, daga cen ake yi a lodo a kawo

Tana gama shirya falon ta koma tana tambayar Murjanatu wajen da ake kilace turaren wutar bangaren
A lokacin Murjanatu ta mike ta ce ta je ta yi wanka itama domin sosai lokaci ya ja har karfe goma ke neman yi dan ta jima tana kyalkyale wajen nan, du wani lungu da sako sai da ta gamsu da tsaftarsa, ba wai dan ba'a gyara wajen bane, kawai ita dince idan ta tashi gyara gyaran take yi mai sunna gyara

Wankan ta shige Murjanatu ta fice dan saka turaran wutar domin itama dakin nasu da suka kwana ta gyara ta goge tasss dan a dan zamanta da Nuriyar itama ta sake koyar sauko dan gyare gyare , ta san mahinmancin hakan yanzu sosai

NURIYAH na gama kimtsawa bayan ta saka sket da riga na atampa ta zumbula katon hijab dinta sannan ta fito , ba dan komai ba sai dan ta ga idan akoy aikin da zata yi a gidan, domin ita bata cire kanta a matsayin da take ba, idan ta samu damar mutuntawa da suke yi mata ba yanna nufin zata manta cewa ita din yar aiki take a gidan har ta nemi wuce gona da iri ba

Tana fitowa ta ja ta yi turus gabanta na dukan uku uku sakamakon mutanen dake falon a irin lokacin

Kara bude kofar ya saka shi waigowa shima ya sauke dubansa a kanta, kyakyawar fuskarta mai dauke da dukkan niimar dake sake dawo da tunaninsa kanta ya zubawa ido, harmaa ya kai wajen da ya nemi shagala da neman manta a gaban wanda yake har sai da Kan giwa dake jiran amsarsa ya dan dago idannuwansa ya sauke a kansa, lokaci daya kuma ya dan juya dan gannin abinda yake kallon
Dubanta shima ya yi na dan sekwani yana yatsina gaban goshinsa cike da jin wani yannayi mai kama da haushi haushin yarinyar bayan babu abinda ta masa ya dan maida dubansa bakin hanyar fitowa daga dakin Nadia yana yiwa Rislan dan gyaran murya

Da sauri Rislan ya juyo yana sada kansa , cike da inda inda ya ce" Ka yi hakuri yayanmu, in sha Allah zan koma jami'ar na karasa, dama fa shi professer din ne yace wai askina kamar na yan dako, a gabam kowa ni kuma raina ya bace na ga ai wulakanta halitar da Allah ya yi ne, shine na so daina zuwa university din kwata kwata"

Sake kure shi ya yi da ido, a kasan zuciyarsa duka magangannun na Rislan yana da amsoshinsu ciki harda'kan balaki, Rislan babu halitar da ta rainani sama da kai' sai dai a bayane gaba daya yau da ya tashi kamar kurma haka ya tashi, da kangin kansa baya son yiwa kansa magana bale ya yiwa wani, dan haka sai ya gyada kai a ransa

yana sake ayana' Wai halitar da Allah ya halita, gashin ya masa gamo ne tamkar wanda zai dauki wani kayan tallah, shi askin ya fi masa kama da na samarin nan dake siyar da kifi, ya wani saka abu a gashi ya yi bakin kirin ya tsayar da shi wai shi ga dan suwaga!'

Baki ya sake tabewa yana fadin" Ka je ka koma gobe in sha Allah, kar na kuma jin wata maganar fada tsakaninka da malamai ko dukanka suka yi dan sun isa ne ka gane? "

Kansa ya gyada yana sake sada kansa sosai

A hankali take son komawa dakin sai dai bata kai ga aikata hakan ba muryar Nadia cikin turancinta na kasa da kasa ta ce" Ke, ke, dawo min nan, ke kuka saka min turaran wuta a bangarena bayan ina da asthma?"

Da sauri ta tsaya dan bata san me tace ba aman a irin yadda ta nufota ta gane koma meye da ita ake kuma itace ta yi laifi

Murjanatu dake karasa daidaita table ce ta juyo da sauri tana kallon wajen, hakama yayansu ya dago yana waigawa yanaa kallonsu

□□□□□□□□ *NEMAN NA KAINA* □□□□□□□□□

Karashensa sabon salo

Na

SAJIDA

Idan mijinki baya jimawa a wajen aiki ki samo wadinnan hadi ki hada ki bashi bayan sallar magariba sai ki sakani a adu'a nima Allah ya karra min lafiya da arziki mai anfani😂 *MADARA MAI DAN DUMI, KANANFARI KWAYA BAKWAI KI WATSA A CIKI, GARIN CITA KI ZUBA CIKALI DAYA, KI KAWO NAMIJIN GORO DAYA KI GURZA A CIKI, SAI KI KAWO ZUMA ITAMA COKALO DAYA KI ZUBA A CIKI* sai ki motsa masa sosai ki bashi ya shanya ☺☺☺☺.....sai ki shirya karba dan kin gayata ne hajiata□□□□

Cike da bacin rai Nadia ta ci gaba da fadin" Dama kin biyo mu nan ne dan ki ga bayana?"

Da mamaki Rislan ke kallon Wani abin kuma, me hakan yake nufi ne? Yake ta ayanawa a kasan zuciyarsa

Shi kuwa Kan giwa a yadda yake din nan abinda ya fi zubawa ido yannayin tsoron da yarinyar ta shiga wanda ya saka take ta murzar hannayenta tana kuma girgiza kanta tana son yin magana aman kuma gaba daya Nadia ta ki bata dama

Da sauri ta ajiye tissu din hannunta da take karra gyara wajen cin abincin yayan nata ta nufo wajen tana fadin" Aunty Nadia ba ita bace ta saka turaren ba fa, nice, ni kuma tun dazu na saka ai inaga baima yi hayaki ba sai kamshin dake tashi dan dan hayakin du ya tafi ai"

Da manyan idannuwanta ta ce" Kina nufin ki ce karya zan maki ne Kanwa?"

Murjanatu ta tabe bakinta tana riko hannun Nuriyah ta janyota tana fadin" Ba itace ta saka ba, na ga baki fito bane ya sa na saka duba da dakin na bukatar turaren"

Da ido ta raka su da kallo, duda yarinyar yau jikinta sanye da zumbulelen hijab, aman abinda Allah ya hore maka wadatace ko da hijab ana gani, gaba daya sai take jin Bata da nutsuwa da yarinyar nan, irin yadda take juyi kuwa abin ba'a cewa komai, su sun san wa suke aure dole hankalinsu ya nemi tashi a kan hakan

Idannuwansa ya dauke a kansu gannin Murja ta nufo falon da su ya sauke saman fuskar Rislan
Gani ya yi Rislan na yin kallo irin na wuce misali wa yan matan, sai ya tabe baki yana kawar da dubansa gaba daya a kan abubuwan dake faruwar

Zai iya cewa bai taba jin murya mai sanyin na yarinyar ba a kusa kusa da shi gaskiya, domin shi din mutun ne mai kaza kaza hakan ya sa yawancin wa'inda ke tare da shi suke mu'amalantarsa da kaza kaza din, ciki kuwa harda iyalinsa, hakan ya sa ya sauke dubansa a kanta a lokacin da Murja ta dukkar da ita dan nesa kadan dan ta gaishe shi muryarta a sanyaye ainun da tsoron da ya cika mata ciki ta shiga gaishe shin

Shirun da ya dauki wajen ba amsa ne ya saka mutanen dake wajen bayan su sake dubansa, sai dai gannin Kan Giwa na yi mata irin kallon nan nasa na son karantar abu ko mutun ya sa Da sauri Murja ta ce" Nuriyah dan daga muryarki kadan bai jiki ba fa"

Nuriyah idannuwanta na cika da kwallah ta dubeta muryarta na rawa ta ce" Auta haka nake magana ba da gangan na yi ba"

Tausayinta ne ya kamata, domin kwarai gaskiya ta fada ita din mai sanyin magana ce sosai da sosai, da yawancin lokuta har akan ce mata kissa ce irin ta mata masu classs, sai dai idan ka zauna da ita zaka gane haka muryarta take da sanyi, saima ta karra sanyayawa idan tana hali na rudanin zuciya ko tsoro

Ita dinma jikinta a sanyayen ta dubi Kan Giwa da siga irin nata da take tunkararsa koda ransa a bace ne ta ce" Yayanah, da mura ne ta tashi yau sosai ka yi hakuri dan Allah"

Kamar an kwaci fuskarsa haka ya maida dubansa kan Murjanatu
Ya yi mata kallo na yan sekwani kafin ya dauke idannuwan nasa a hankali ya mike daga zaunen da yake ya juya barin da Nadia ke tsaye tana cika tana batsewa da yaren turanci ya umarceta kan ta dauko masa abincinsa ta kawo masa dakinsa

sannan ya wuce ya yi tafiyarsa dakin nasa dan ranar hutawa yake yi na zai fita ba sai ko gobe

Sai da ta je ta hada komai tana ta tunanin kar ta saka abinda zai bata masa rai ko kwatankwacin hakan domin su ba su suke saka masa abinci ba hakan ya sa basu san me da me yake so ba da adadin abincin da yake iya ci ba

Tana tura yar kurar da ake dora abincin ta karaso kusa da su kasa kasa sosai ta ce" Kanaina haka kuka zabarwa kanku? Kun taba gannin KAN GIWA ya ci abinci a daki? Sanadiyar wannan yarinyar yau har ya kaurace wajen cin abincinsa na shekara da shekaru? Ku sake tunani kan lamarinku gaskiya"

Da ido suka rakata babu wanda ya ce da ita ufan har ta shige babar kofar dakin Kan Giwa

Kasa kasa sosai RISLAN ya ce" Me yake faruwa ne Baby?"

Auta ta sauke ajiyar Zuciya tana dage kafadunta ta ce" Ni kaina ban san meye damuwar matan nan ba, dan tun jiya suke abubuwa tamkar zararu , a tunaninsu Nuriyah ta zo wajen nan ne dan ta zama barazana a cikinsu, a ganninsu tana iya zamtowa daya daga cikinsu shi yada gaba daya suka haukace suke neman haukata zaman lafiyar kowa, domin kowace cikinsu abin fada take nema"

Da mamaki shinfide saman fuskarsa ya kalli NURIYAH dake ta murzar hannu dan du a takure take ya kalli Murjanatu ya dauki yaren turenci ya ce" Me kike nufi, kina nufin tsabar basu da hankali sunna tunanin Yayanmu zai iya yim soyaya da Nuriyah?"

Itama da wani mamakin da ya shinfidu a saman fuskarta tana kallonsa ta ce" Ban gane sunna tunanin zai iya yi ba yaya? Kamar kana gannin bata kai matsayin ba?"

Zamansa ya gyara yana ajiye wayarsa da kyau ya ce" Baby kin fa san sarai me nake nufi, NURIYAH fa idanma ta fiki bai fi ta baki shekara biyu ba, kin kuma san waye yayanmu, a tsarin macen da yake iya duba babu ta kasa da shekara talatin, bama wannan ba ni kar ku min haka bana so, duda ta dakatar da ni ta nuna min cewa ni din na fi karfin soyaya da ita lokaci na bata, na bata dama ta sake hutashe da tunaninta, na mata tanadin lokacinmu, na tabata idan na zaburo zata dubeni , gaskiya idan matan nan nasa zasu takura mata ne ta koma cen har su Hajia su dawo"

Zata iya cewa kwata kwata ita lamarin dan uwan nata bai wani shigeta ba, dan hakane ta ki tofawa a kan hakan, ko dan yayan kawarta ya nuna yana son Nuriyar ne? Ita gaskiya gaba daya gani take yi Yah Rislan yaro ne sosai a kan lamarin Nuriyah, ko me yasa ? Oho.....a sanyaye ta sake rike hannun Nuriyah tana kallonta ta ce" Ni bama wannan ba duka, gaba daya bama wannan ba Brother, Wannan tsoro da baya baya da Nuriyah ke yi a gabansu baki dayansu na damuna, dan Allah me yasa zaki ringa jin tsoronsu ne? Mutane ne kamarki, bale a yanzu da suka sako ki a gaba burinsu su saka ki gaza daukan rigimarsu, me zai hanna ki yi gwa da gwa da su ne?"

Da mamaki itama Nuriyar take kallonta a nutse ta ce" Auta, na yi gwa da gwa da su wa kike magana?"

Murjanatu ta ce" Da ita Nadiar da Djamilar"

Nuriyah ta yi murmushi tana sauke ajiyar zuciya ta ce" Ni a wa?"

Daga Rislan har ita kallonta suke kafin Rislan cike da shaukin yarinyar ya ce" Ke a mutun dan Adam mai daraja"

Nuriyah ta kalleshi a karo na farko ido cikin ido tun fitowarta domin tun dazun tana ta murza hannayenta ne dan ta samu jikinta ya daina rawar gannin Kan GIWA da matarsa a wajen , tana ta son koyawa kanta yadda zata rayu da su ba tare da ta wahaltu sosai ba, domin wajen nan dai nasu ne, ya zama dole haduwa da ita da su a kowani irin lokaci

Murmushi ta yi tana janye idannuwaan a cikin nasa a nutse ta ce" Tabas dan Adam yana da daraja, shine halita mafi daraja a cikin halitu, haka kuma a cikin y'ayan Adam akoy sarakai, akoy iyayen gida kuma akoy y'ayan gida, kamar ma'aikata ce, zaka yiwa wanda yake gaba da kai biyaya koda kuwa ka girme shi a shekaru ne, bale aiki irin nawa
Ban taba aikin aikatau ba sai a wannan karron, ban san yaya wasu gidajen suke ba aman nakan ji daidaiku a wajen saide saidenmu ana kwatanta irin rashin adalcin wasu iyayen gidan, Auta da yaya RISLAN da an zo gidan nan zan iya cewa hankalina ya kwonta sosai na kuma samu nutsuwar da har nake ji a yanzu idan na fita zan yi ta gararamba a kan titi ne ina bin waje waje, shi yasa nake so ku taya ni, dan Allah ku tayani yiwa iyayen gidana biyaya, kar ku ringa saka min abu a kaina duda ba mahaukaciya nake ba aman zuciya bata da kashi yau da gobe kuma sai Allah, idan ku kun aikata irin haka kun tsira ni na san sai dai a tsireni domin haka din rashin da'a ne, rashin kunya ne, rashin godiyar Allah ne, a gaskiya ina alfahari da tsoronsu da nake ji dan ko ba komai tsoron nan nasu da nake zai sa na kiyaye dokokinsu in sha Allah " ta karashe tana ta sauke ajiyar zuciya dan harga Allah abinda take da muradi su yi mata kennan, ba su ringa daidaita kansu kai tsaye da ita a kowani lokaci ba, kai ita da za'a ware mata aikinta a wannan bangarenma kamar yadda take da shi a dayan bangaren da ta godewa Allah, da kuma matansa ko a leke ba zasu kuma ganninta ba dan idan ta buya sai an nemeta

Da wannan suka je suka karya suma sannan suka fice gaba dayansu suka nufi cen bayan gidan Rislan na ta jajen gobe gobe zai tafi shi kam ko kwana biyu ba za'a bashi ba, yar uwar nata tsokanarsa irin na mutun da mabiyi, Nuriyah kuwa na dan murmusawa idan halin hakan ya kama

A cikin dakin KAN GIWA

Tunda ta fara magana da irin kalaman dakew fita daga bakinta ya cire dubansa irin na kureta da idannuwan nan ya kawar gefe guda ya kurawa lalausan kafet mai gashisshika ido yana kallo bai ce mata ufan ba har sai da ta dire bayaninta sannan ya sake juyowa a karro na biyu yana kallon hannayen nata da take maganaa da su zuwa bakinta dake furucinsa

Dan murmushi mai ciwo ya yi sosai yana kallonta ya ce" Tabas na san aure ba iya sex ya tsaya ba, domin nakan ji magidanci na shaukin maganar cewa yau ko me madame ta dafa? Nakan ji magidanci yana cewa ya ajiye madame a saloon, ko da ya zo lokaci zuwa lokaci sai na ga waya ta yi haske wai ace madame ce..... ni da kaina ina son na ga dayan abin nan da na rasa gane menene shi na sanshi.....sai dai abin takaicin Sex dinma da ake min kallon shi na sani a duniya bani da shi yadda nake so?"

Nadia ta kure shi da kallon tsoron irin kalamansa na yau, domin da da ne zai wartota ne ya danneta a saman gadon ya amshi abinda yake so
A raunane ta ce" Baby (), yanzun du irin kokarin da nake yi a saman bed bai kai godiya ba? Kana ganni ina iya bata lokaci mai tsayi ina romancng din dukkan wani lungu da sako na jikinka, bai isa ya saka ka samu nutsuwa da ni ba?"

Jin kansa na neman sarawa ya mike ya nufi bayi yana fadin" Kina iya tafiya"

Da kallo ta raka shi har ya shige cikin bayin sannan ta sauke ajiyar zuciya tana zarro ido da kallon abincin da ta zuba masa bai ci ba gashi har karfe goma sha biyu na neman yi na rana bayan Kan Giwa ba dai yiwa abinci uzuri ba
Marfinsa ta saka ta rufe ta juya ta fice a dakin
Abu daya tal ta sani tare da mijinta shine idan ransa ya baci baya so kowa ya zauna masa a tare da shi, shi yasa ba zata takura masa ba, ita ta kwana gidan sauki, da ta masa maganar me yasa rayuwarsa sai da sex zai rayu da iya gaskiyarta take, ace rayuwa Namiji sai ya sasakeka? Shi ba zai iya hakura da Romance ba? Romance ai shine soyayar, aman sai ta rasa daj me yake son sai ya yi, har fada yake yi yau kwanansa uku rabonsa da mace, ko ina Izabel dinma ta yi?

A bangarensa kuwa a bayin ruwan sanyi ya samu ya runga wanke fuskarsa da shi
Tamkar wanda wani abu ya ciyo shi mai mugun daci ya saka hannunsa da karfi ya daki gilasss din dake jikin bangon haka kuma tashi daya zuciyarsa na tafarfasa

Idannuwansa ya rintse, domin gilass din ya fashe ne harma ya shigar masa bayan hannu hana ya sa jinni ya fara dan bata wajen a hankali a hankali

Hauhawa kirjinsa yake yi da wani dacin , sosai ya gama hawa sama a tsaka tsakiyar tashin hankalin da yake ji tun daga cikin zuciyarsa .....wannan shine gaba kura baya sayaki! .....ZINA bashi, matansa sakarkaru, idan azumin ya dauka yana shan ruwan yake tashi da feeling!, Ya subahannalah! Ya kai hannayensa ya dafe kansa yana jimkewa
Bai taba jin daci irin na yau ba
Bai kuma taba yarda cewa eh idanma akoy son zuciyarsa na bin matayen banza to fa akoy sakaci na iyalinsa
Bai kuma sake yarda cewar rainin hankali ne ya masu yawa ba har sai da ya auna su sauran matan dake iyawa da shi ai suma mutane ne ba injinna ba

Da dacin rai ya fito ya fice ya nufi bangaren da kayan motsa jikinsa suke ya rufe ya shiga motsa jikinsa, ga yinwa na dan tsikararsa da sauransu

A wannan ranar a nan ya wuni cirrr, idan lokacin sallah ya yi ne yake ficewa ya je masalaci ya salata ya dawo, a cikinsa kuwa banda madarar dake cikin frij din da ya ringa sha kadan kadan baya taba komai, yana ta auna lamarin rayuwarsa ne
Shi dai ya san a harkar jikinsa akoy wa'inda suka dame shi suka shanye a nacin abin nan, ya kuma san babu abinda ke rikita kwonciyar hankalin namiji irin ya kasamce a irin bukatuwar nan ya kumarasa.....to wai yana da tambayama a wajen mutanen dake dukan kirji su budi bakunnansu su ce " *DAN ME ZA'A TAKURA DA MAGANAR SEX BAYAN SOYAYA BA A NAN TAKE BA, ANA KUMA IYA RAYUWA DA SOYAYA A ZUCIYA BA TARE DA AN YI SEX BA*!" Neman amsarsa shine a fayace masa dala dala maganar nan dan ya gane mahaukaci ya yita ko mai hankali????????? A fada masa ta yadda zai rayu da mace igiya na zame masa karfe a wando ba zai taba ba sai dai ya kalla dan shi so ai so ne babu tabe tabe?

□□□□□□□□ *NEMAN NA KAINA* □□□□□□□□□

Karashensa sabon salo

Na

SAJIDA

Page.
31

Yana dawowa daga sallar isha'i ya wuce direct cikin gidan ya zarce dakinsa domin a lokacin su Nuriya na kicin ita da Murjanatu sunna girkin da suka saka kansu wanda Nuriyah ke cikin nishadin gannin sunna girki da kansu, dambun nama suke yiwa Rislan da ya nuna yana so mai yawa da zai yi guzurinsa dan komawa makaranta

Yana shiha dakinsa wanka ya shige ya yi sosai sannan ya fito daure da tawul dinsa ya nufi wajen da ya bar wayoyinsa
Kiran da ya tarar sai da ya saka shi dan zarro ido ya mayar da wayar nan ya ajiyeta bai maidawa kowa kiran ba , ciki kuwa harda Hajia Murjanatu domin yau din nan harda ita ya wuni jin haushi a zuciyarsa dan du ita ta karra saka masa kyamatar zinna a zuciyarsa haka kawai ita da mijinta da d'anta !

Da wuri ya samu waje ya kwonta, abincin nan da aka kawo masa yana nan wajensa , sannan dakin bai samu arzikin tsintsiya ba, shi du ba ta hakan ba yake hannunsa ya yi kaba sosai ya fara kumbura haka kuma jikinsa yanna jin da zafi zafi dan haka ya kwonta ya rufa rufff ya shiga neman barci

A bangaren sai da suka gama komai suka juye a abin tsanewa suka rufe rufff dan kar wani abu ya fada sannan suka rufe kicin din suka shige dakinsu da nasu abincin, falon sai kanshin soyayan dambun naman yake basu saka turaren wuta ba, dan gudun fitinanun matan nan da tunda safe basu kuma gannin kowace a falon ba, su a tunaninsuma ko sun fita ne, sai dai ai basu wuce su ba basu ji karar fitarsu ba, kawai kowace na dakinta tana fama da wayar asara, babu wace ta nemi wajen da mijinta yake, hasalima a wunnin ranar idan sun daga waya dan kiran cikin gidan dan su yi oder irin abincin da suke iya ci ne kawai a kuma kawo masu har bangarensu

Cike da nishadi da farin ciki yan matan suka gama cin abincinsu bayan sun gama yin wanka da sallah da komai, sannan Murjanatu ta turawa mamanta vidio call a daidai lokacin da summa suka gama cin nasu abincin sunna dan taba hirar yama don tserayar awanin dake tsakani ya saka bambancin lokacin tsakanin kasashen

Idannuwanta ta zubawa fuskar Nuriyah a lokacin da take yar dariya dan Hajia na mata tsokana kamar jikarta ta jinninta

Ajiyar zuciya ta sauke ta maida dubanta kan mijinta da shima ya kurawa yannayinta ido

Idannuwan nata ta sake cirewa a kansa ta maida kan Nuriyah, watau yarinyar harda gura gura gareta a harshenta irin na gidansu sai dai a gidan nasu yar uwarta bata gura gura, itace mai gura gura da mahaifinsu da mahaifiyarsu

Tabatan da Hajia ta yi da kula tana fadin" Maman takwara lafiya?" Ya sakata sauke ajiyar zuciyar da sai da kowa ya kalleta

A hankali Murja auta ta ce" Mamanah baki da lafiya ne?"

Dan murmushi ta yi wanda kumatunta suka lotsa tana shafa gaban goshinta ta ce" Lafiyata kalau autana, ina yayanku ne? Ina fata ya ci abinci kuma kun kula da baku dauki magana ba ko?"

Murjanatu ta gyada kanta duda bata da masaniya a kan maganar cin abincinsa, sai dai a tunaninta ai mata ne tare da shi har biyu wa'inda take tunanin Saboda su yanzun yama tsaneta ne, domin tun jiya zuwa yau wani iri take ganninsa ita dai kuma du laifinsu ne , dan haka ta bada amsa da eh

Mama ta yi murmushi a sanyaye ta ce" Nuriyah ?"

Nuriyah dake bayan Murjanatu ta duko da girmamawa da Murmushi ta amsa tana kallon Maman,
Mama ta lumshe idannuwanta zuciyarta na dokawa a sanyaye ta ce" Allah ya maki albarka"

Sai da NURIYAH ta ji wani irin abu na tsirga mata jikinta gaba daya, muryarta a sanyaye ainun ta dago sosai tana kallon fuskar matar ta ce" Amen ya Allah Mamah"

Mama ta sake lumshe idannuwanta ta mike da sauri ta yi ciki hakan ya sa Hajia rakata da kallon mamaki da tunanin abinda yake damunta, inda Aba ya mike ya bi bayanta dan yannayinta ya saka shi a cikin tunanin ba lafiya ba

Yana shiga ya ganta tsaye gaban madubi ta sada kanta ta rungume hannayenta biyu a kirjinta , hakan ya sa ya karasa yana kallonta a nutse ya furta" Maman Auta me yake damunki ne haka?"

Juyowa ta yi a hankali tana sauke dubanta a saman fuskarsa, raurau din da ta yi ne ta kasa rike hawayen da ya cika mata idannuwanta har suka samu damar biyowa gurbin idannuwanta a hankali sunna zarya a saman kumatunta
Hankalinsa ne ya fara tashi yana dubanta ya ce" Yar uwarki ko? Aman me ya saka ta fado maki a rai kai tsaye haka bayan kikan jima koma nace tunda kika dauki shawarar Mama cewa kuka ba shine magani ba ki yi ta yin adu'a kina fadawa ubangiji sannan ki ringa yawaita sadaka in sha Allahu ko me ya faru da ita zaki ji shine yau kuma zaki yi halin?"

Hannayenta ta hade ta shiga murzawa tana fadin" Ba zaka gane ba Aban Babana (Kan Giwa), ni da kaina na rasa gane cakulewar tunanina a kan lamarin yarinyar cen, ka ga dai bata kama da yar uwata sam, aman kuma wasu irin abubuwa ke karra fuzgata a kanta, da zarar na ji muryarta kuwa hankalina sai ya nemi gushewa, shin me ya faru da y'ar uwata ne? Tana raye ne ko bata raye? Ina Lawali ya koma ina ya kaimin ita? Cikin da muka barta da shi yana ina? Abanmu ya rigai ya kamu da ciwon da sai dai a lalaba kawai sakamakon tunaninta, ya Rab....." Ta idasa tana rufe

bakinta da hannayenta bibiyu tana fashewa da kuka hadi da zama a bakin kujerar tana hanna kanta yin kukan tun karfi domin Hajia na yawan yi mata nasiha a kan hakan

Sake salama Hajia ta yi tana tsaye har sai da Aba ya ji ya juyo hankakinsa du a tashe ya amsa ya kamota suka idasa shiga dakin ya zaunar da ita saman kujera tana kallonsa shi da Mama a tausashe ta ce" Wannan karron sau uku kennan ina hankalce da dukkan nutsuwarki na barin gangar jikinki da zarar kin ga Nuriyah, me yake faruwa ne?"

Mama ta sauke ajiyar zuciya tana fadin" Mama ni da kaina ban sani ba, abin na fin karfina ne sosai, bayan ban ga mahadi ba.....aman wasu lamura kadan kadan dake fitowa a tare da yarinyar kam saka zuciyata dokawa da karfi, misali irin dagowar da ta yi dazu , y'ar uwata na yin haka idan abu ya taba mata zuciya, tafiyar yarinyar na karra dulmiyani a yannayi na tunani, muryarta ta yi sanyi sosai a kan tamu sai dai gura gurarta dake dan sake sakani a nazari, Mama a ina kuka samo yarinyar ne?"

Mama ta sauke ajiyar zuciya ta ce" Kina ji Ouseina, abinda nake so da ke shine ki saka hakuri da nutsuwa a cikin zuciyarki, ki dauka cewa idan tana raye zata bayana idanma ta rasu ne tabas zamu sani, kin ga daga ranar da kika fada min kema haifafiyar garina ce har kika fadan labarinki nake kwana ina tashi da abin a zuciyata, fada maki ne bana yi aman nima ina cikin masu neman yar uwarki, kin ga Nuriyah dai ban san iyayenta ba, aman yayanta ne ya kawo min ita, da zarar mun koma zan kirawo shi mu yi magana sai hankalinki ya kwonta in sha Allah "

Da wannan suka rarasheta, Hajia ta karra da nasiha sosai har ta dan samu nutsuwa a zuciyarta har ta iya sakewa ta ci gaba da yan shagulgulanta , aman cen kasan zuciyarta gaba daya hoton yarinyar ne a dankare a ciki ta rasa gane kan naci irin na idannuwanta a kan abu

---

"Auta.....Auta.....Auta? Ki tashi mana haka wai ni ki rakani na dauko a juye masa a rufe masa shi mana" ta sake fada tana dan dadaba Murjanatu dake ta juyi tana alamun ta kiya domin barcinta ya yi nisa sosai ba zata iya tashi ba

Sake dadabata ta yi zata sake cewa ta tashi Murjar ta buda idannuwanta da kyar tana fadin" Gaskiya Nuriyah ba zan je ba.... fisabililahi ke bakya gajiya da aiki ne ? Ni ba zan je ba"
Ta idasa tana turo baki hadi da sake juyawa ta ja bargo ta rufe kanta ruf dan gani take farmaki ne kawai Nuriyar ke son kawo mata tana zaman zamanta

Yar dariya ta yi a sanyaye ta sauko kafafuwanta tana mika da rigar barcin dake jikinta doguwa wace ta kai har kasa, sai dai mai santsin nan ce sosai domin gaba daya a jikinta take kuma bata da nauyi ko daya sannan siraren hannaye ne da ita, sai hula irin mai hudojin nan bak'a a jikin gashinta wanda ta kasa saka gashin gaba dayansa cikin hular dole sai saman gashin ta dora hular shi kuwa ta tufke shi ta barshi a bayanta hakanan

Hankali kwonce ta nufi hanyar fita, dan ta riga ta san dabi'ar mutanen gidan, sun kasance tamkar horon nasaru basa wuce lokacin kwonciyarsu , haka kuma idan ba lokacin su fito ya yi ba basa fitowa, shi yasa kai tsaye ta fitowarta ta yi hanyar kicin

A daidai zata yi kwanar kicin din da lalube ta laluba ta dadana abubuwan kunna fitilun falon tama dan yamutsa fuskarta domin gaba daya iskar falon sai ta ji bata jin dadinta a hancinta

Ita da zata wuce ta dauko dambun naman sai ta zagaya ta dauko kaskon da Murjanatu ta saka turaren wuta tunda sasafe ta yi kicin din da shi ta saka abin budewa ta bude da Bismillah ta shige da ayatul kursiyu da take yi a bakinta kasa kasa tana tafe tana dan lumshe idannuwanta da murmushin da bai barta ba wanda ta kwanta da shi tun albarkar da maman Murjanatu ta saka mata haka kawai take jin abin a cencen kasan zuciyarta

Wajen gawayin da kayan turaren wutar ta je ta ajiye kaskon ta shiga bubude kwalaben tana sinsinawa hadi da lumshe idannuwanta tana jin yadda kanshin ke ratsawa har zuwa cikin zuciyarta tana sake shinshinawa

Cike da rausayar da ba da gangan take yi ba da farin ciki ta kunna gawayin nan biyu ta dan ja baya tana kallon kwalaben turaren wutar ta ce"

I'm sorry □□□□□□ ku mu bashi amsa mu ji???????□□□□□□□□□

□□□□□□□□ *NEMAN NA KAINA* □□□□□□□□□

Karashensa sabon salo

Na

SAJIDA

Cike da rausayar da ba da gangan take yi ba da farin ciki ta dan ja baya tana kallon kwalaben turaren wutar ta ce " Nama rasa wane ya fi dadi, bara a yi tsakani tsakani , tsakanin gizo da kogi in ba gizon ba gigogi kantana da awa da adam....nana nana, nana gwadamini gidan gaskiya wai ke ni ba gashinan ba....." Ta idasa da murmushi ta dauki kwalbar tana budewa ta dibo dan daidai misali ba da barna ba ta zuba tana sake fadin" bara kicin din ya fara yin kanshin sai na kai falon....., Koda yake bara na kai falon ya dauki kanshin sai na maido kicin d....."

Dif ta yi shiru sakamakon muryar da ta ce da ita" Wacece ke?"

Jikinta ne ya dauki bari a tsayen da take, zuciyarta kuwa ta aniya neman fitowa daga cikin bakinta ta fado kasa,

Hankalinta ya dugunzuma ya tashi, kwakwaluwarta ta nemi hadewa ta sakata doke doke irin na wace bata da hankali

A tsayen da yake bibiyu yake ganninta, tun bayan kwonciyarsa a dakinsa ya kasa barcin domin jikinsa sake daukan zafi yake yi, haka kuma hannunsa sai ya idasa zundumewa tamkar ba nasa ba, wannan dalilin ya sa ya mike da kyar ya shiga neman wayoyinsa aman gaba daya ya rikice domin du a rikicen yake

Fitowar da ya yi da nufin ya je ya yi anfani da wayar falon ya kirayi Rislan ne dan shi ya zo masa da likita sai dai bai karasa wajen wayar ba ya zauna a falon yana rike da hannun nasa a hankali yana shafawa dan ya ji wajen da ya fi sukansan nan dan ya tabata Kwalbar nan ce a ciki ya tsigeta ko zai takaita masa sukar
Yana wannan halin ya ringa jin maganar mutun a kansa, bai ganta ba dan duhu har sai da ta kunna fitilun nan ta kuma juyo ita kadai sai hira take tana murmushi ta dauki abin turaren wuta ta nufi kicin din gidan
Wannan dalili ya saka shi kamewa a zaune da mamaki, domin wannan budurwar bai santa ba, bai san ko wacece ba, nan da nan ya shiga tunanin ko dai aljanna ce? Domin tsarin halitar yarinyar zai iya cewa a kurkusa idannuwansa basu hango masa irinta ba sam, irin yadda samanta ke dore a saman kugunta subahannalah tabas aljannah ce, ga kalar gashin kanta uwa uba yadda ta sake take sha'aninta a gidansa tamkar wace gidan nata ne

Da kyar ya ciciba dan ya karasa ya ga ko mecece ita, da wannan ya idasa kicin din ya tsaya yana gannin yadda ta ringa magana da murmushi ita daya har zuwa yar wakar tsakani tsakanin da ta yi dan daukan turaren wutar

Kwalar da ta cicika idannuwanta fuskarta ta dauki yannayin tsoron da ya saba ganninta da ita ba yannayi na farin ciki da sakewa da walwala ba ta juyo tashi daya ta sauke idannuwanta a saman fuskarsa kafin ta idasa sakin shagwababen bakinta , tabararen bakinta ta fashe da kuka tana sada kanta bakinta na rawa ta ce" IIIIna kwana , iina yini, dama dambun naman Yah Rislan ne na zo dan na juye a flas sai kuma, sai kuma nace tunda barci kuke bara na saka turaren wuta dan kar ku tashi dakin na kannin kayan yaji..... Innalilahi wa inna ilaihi raj'une....." Ta idasa tana karasa sakin kukanta dan ita da kanta dake bada bayanin baya mata dadi a kunnenta yadda ya dace, kawai fadinsa take yi zuuuuuuu kamar wace ke sheka karya

A hankali, muryarsa na nuni da baya jin dadin jikinsa ya saka hannunsa ya talabe dayan ya sake fuskantarta ba alamun tsoronta a tare da shi duda kokonta na cewa aljannah ce dake cikin zuciyarsa ya ce" I sd who are you?"

Ido ta shiga kikiftawa tana kallonsa hakan ya saka shi girgiza kansa da dan daga murya kadan Wanda ya hadasa masa tari ya ce" na ce wacece ke?!" Sai kuma tari ya kama shi a hankali ya hade bayansa da jikin garun kicin din yana lumshe idannuwansa

A tsorace take bin yannayinsa da kallo, du irin rikicewar da take ciki ba zai hanna mata gane wannan bawan Allahn na cikin wani hali na rashin lafiya ba, dan haka take dan matsowa duda ta san kasada ce aikata hakan har ta idasa matsowa kusa da shi sosai a hankali take kallonsa har ya kare tarin yana sake lulumshe idannuwansa

Da sauri ta juya ta dauki kofi ta kunna ruwa ta darwaye sannan ta zubo ruwan pampon ta dawo wajen da ya durkushe yana dan bubuga kirjinsa dan tarin ya kwonta masa

Gaba daya ta samu kanta da dora hannayenta ta samu da kyar ta dago kansa da ya sada ta kawo kofin ta saka masa a bakinsa tana talabe da fuskarsa ta ce" Sha , idan ka sha ruwan zai bari kuma.ka daina sada kanka tarin ba zai tsaya ba, sannu "

Idannuwansa ke lumshe ya hade da bayan hannunta yana shan ruwan a hankali a hankali har ya ji sosai ruwan ya dira masa harma ya ji ya daina tarin sosai sannan ta cire ruwan ta ajiye a kusa da su tana sake hura masa fuska tamkar wani yaro karami, domin ita du ta rikice taimaka masa take yi , idan ka mata tambaya a lokacin tsabar rikicewa da wahala ra shaida maka da wa take tare

A hankali a hankali yake sauke ajiyar zuciya yana jin gaban goshinsa na sara masa

Muryarsa cen ciki ya kamo hannun nata a gefen fuskarsa ya ce" Call Rislan fr m pllz"

Fuskarsa ta kurawa ido tama son fasarce yarensa a cikin zuciyarta
Hannun nasa da ya yi kaba ta zubawa ido wanda hakan sai da ya sa tsigar jikinta tashi gaba daya
Da sauri ta janye hannunta ta mike ta yi falon jikinta na fawa ta karasa wajen wayar ta saka nmber bangaren Rislan din ta yi kira domin gaba daya na kowani bangare kake shanyewa idan kana ma'aikacin gidan

Ta jima tana ringin kafin ya daga muryarsa a shake da alamun barci yake yi shi dinma

Muryarta a sanyaye ta shaida masa cewar ya zo bangaren Kan giwa bashi da lafiya

Sai da gabansa ya fadi, da sauri ya wartsake yana wara idannuwansa ya saki wayar ya nufi hanyar wucewa da wani irin sauri kwata kwatama bai tsaya ya dauki komai ba

Itama tana nan tsayen jikinta bai daina bari ba tana sake leka hanyar da yake jingine idannuwansa lumshe har Aka shiga buga bangaren nasu

Da sauri ta je ta bude tana kaucewa Rislam ya shigo kai tsaye zai fara magana idannuwaansa suka sauka a kanta

Da sauri ya cire dubansa yana waige waigen falon dan son gannin mutanen bangaren da yayansu, sai dai ita daya ya gani a lokacin da ta juya ta nufi hanyar kicin din tana nuna masa tana kuma fadin" Yana cen Yah Rislan mu je ka gani"

Wani irin mamaki, da tunani ne ya darsu a cikin zuciyarsa a lokacin da ya ga suturar jikinta ya kuma tabata cewar itace kadai ke tare da yayansa, me ya sa daga ita sai shi a irin wannan lokacin? Me take yi da wannan shiga a haka bayan Nuriyar da ya sani ba zata iya fitowa a haka gaban wanin da ba muharaminta ba? Shima yana cikin wa'inda suka yi maganar a barta ta saka suturar da take so dan aiki a gidan nan

Yana tsakanda maganar zuci cak tunaninsa ya tsaya sakamakon damkar damtsen hannunsa da ta yi gannin ya ja ya tsaya a birkicen da take ta sake nuna masa hawaye na bin kumatunta ta ce" yana cen din fa, ka je dan Allah"

Sai a lokacin ya iya gane ko me yake tafe da Nuriya, tabas tana cikin hali na rikicewa wanda da yawan mutane idan suka rikice sukan rasa abin yi ne, saima daga baya ake iya fada masu ga abinda ya faru

Kamar wadda ya kunna haka ta shiga fadin" Ni ja fito ne dan na juye dambun namanka sai na shiga kunna turaren wuta sai kawai na ji maganarsa a bayana, sai da na juyo sai ya karaso sai ya....."

A hankali ya ce" NURIYAH, NURIYAH "

Ta yi dif tana kikifta ido a birkice

A hankali ya ce" Je ki kwonta kin ji? Tafi dakinki ki kwonta ki yi barci kin ji?"

Da sauri ta ringa gyada kanta ta juya ta yi dakin nasu gaba daya ba a cikin hayacinta ba
Sai da ta kulewa ganninsa sannan ya juya ya nufi wajen yayansa
Yana dora hannunsa a saman wuyansa ya ji zafin da ya kwasa ga kuma yadda hannunsa ya yi , dan haka da sauri ya fice ya kirawo masu tsaron lafiyarsa mutun biyu suka kama masa suka yi dakinsa da shi sannan ya saka aka je cen bangarensa aka kwaso masa baban kit dinsa na asibiti ya shiga ba yayansa talafin da ya dace cikin gagawa, domin ya gane wannan ciwuka na hannunsa da wasu kwalaben basu fita bane suka hadasa masa zafin zazabin nan mai fitar da mutun a hayacinsa

Sosai ya cire ya wanke sannan ya saka magani ya nade masa kuma ya jona masa karin ruwa mai hade da maganin zafin zazabin sannan ya zauna a gefensa ya zuba masa ido

Gaba daya a duniya bawa kan hadu da jarabawa kala daban daban, kuma kowani dan Adam tara yake bai cika goma ba, kamar yadda du jin dadin mutun ko kudinsa yakan hadu da wata tangarda ta rayuwa....to hakan ce a kan yayansu
KAN GIWA ya kasance mutun mai arziki, mai kuma mulki, sai dai gaba daya rayuwarsa a abinda ya shafi mace a hagunce ya zo masa
Shi yaro ne a kansa, aman zai iya fadin menene matsalar yayansa kuma menene maganinta
Tunda farko shi ya fara saka kansa a damuwa da ya dauka cewa idan ya yi duba da abinda ke wakana ta bakin yan bariki ne gaskiya, sai ya mike ya ce shi a duniya macenma ga daga bakin shekarun da zai iya dauka, ya je ya zabo din ya darje a tunaninsa yana neman wace zasu zauna su fahimci junna, sai ya samo sun aman kuma sai ya fara bata rawarsa da kansa ta hanyar yin sake wa tarbiyar ahalinsa, ba maganar shakuwa, ba maganar zaman aure a tatare da su, kuma shi dai ya dauki hakan a matsayin tsabagen samun waje da raini domin a cikinsu ko yare suke koda basu da alkibla daga gaban uwa da uba aka dauko su.....a yanzu bai san ta yadda zai yi ya daidaita al'amarin nan ba, abinda ya sani shine a gaskiya ran kowa zai bace a gidan nan ta yadda yayansu KAN GIWA ne bashi da lafiya aman iyalinsa na kwonce sunna shagalinsu? Wannan ba zama na aure ake yi ba, ko zaman bariki ne zara yi maka biyaya ko dan kudaden aljihunka

Zuciyarsa ke hucin bacin rai , yakan saka hannunsa ya shafe hawayen da ya Tarun masa a idannuwansa da tunanin yanzun a gobe dole zai bar gidan nan ya tafi jami'ar indiya dan ya karasa karatunsa na zama baban professeurn likita? To yaya zai bar bayansa da irin wannan rikicin? Yayansa ba zai taba dubawa ba!

A nan a zaune sai barci barawo ne ya kwashe shi wanda ya yi mai nauyin da har bai san an yi kiran sallar asubah ba

Shima kasancewar ya samu barcin sai da hasken safiya ya fara dilowa ne ya fara bude idannuwansa a hankali yana dan maida su yana lumshewa

A hankali ya kuma budewa ya sauke dubansa a kan karin ruwan da ya karre Rislan ya kashe tun kafin barci ya kwashe shi sannan ya dago hannunsa mai daure da bandeji yana kallo

Idannuwansa ya lumshe a hankali ya ciciba da niyar tashi yana dan sauke numfashi kadan daga makogwaronsa,
Wannan motsi ya tayar da Rislan da sauri daga barcin da yake a karkace a saman kujera yana kallon yayansa

Da sauri ya mike yana saukowa hadi da fadin" Sannu yaya, yi a hankali bara na kama ka"

Barin ya yi ya taimaka mada ya mike kan kafafuwansa yana sake yamutsa fuska ya rike shi da kyau suka nufi bayi sannan ya barshi ya dawo yana tunanin koma meye ya same shi madubin bayin nan da ya yi ratsa ratsa ne ya shishige masa hannu domin ga digo digon jinni nan ga kuma madubin a zuzubde ko'ina

Shima wucewa ya yi ya koma bangarensa da gagawa ya samu ya yi wanka ya yi sallah sannan ya fito ya zaga baban kicin ya saka aka loda masa hanta ruwa ruwa da jus ya turo ya dawo yana duba lokaci karfe tara ce ta yi falon na kanshin turaren wuta ya wuce ciki

Gaban madubi ya same shi tsaye yana balla agogo a hannunsa mai ciwon a hankali, shi kuma yana cikin shiga ta dogon wando na yadi baki lalausa sai riga mai dogwayen hannu fara kal sai kanshi yake zubawa na turaren da ya bulbula a jikinsa

Ta madubin ya saci kallon Rislan din da ya tabata shine ya fitar da abincin nan da ya kwana a nan sannan kasa kasa sosai ya amsa masa gaisuwar da yake yi masa

Rislan ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya ce" Yaya fita zaka yi?"

Kan Giwa ya sake kallonsa kadan cen cikin makoshi ya ce" Oummmm"

Rislan ya dan daburce dan sai ya ji ya samu wani irin shaku na maganar da ya kunso a bakinsa, sai dai ba zai iya ba idanma dukansa zai yi sai dai ya doke shi, dan haka ya rintse ido yana fadin" Yaya"

Kan Giwa ya sake dakatawa da kokarin bala boturan rigarsa na cen sama yana kallonsa da kulla , dan ya kulla akoy abinda ke damunsa

Rislan ya kikifta idannuwansa hawayen dake cikin zuciyarsa suka farra samun gurbin zuba ya hade hannayensa ya shiga fadin" Yaya, wannan rayuwar na damuna, wannan rayuwar na sakani a tunani, yaya Matayenka sunne ya dace ace a gidan nan sunne iyaye, sunne bangon du wani wanda yake cikin gidan nan domin Kaine baban yayau, kaine babanmu, kai muke kawowa kukanmu, tunda muka rasa mahaifiyarmu ka rikemu bamu nemi komai mun rasa a duniya ba daga mu har iyayenmu, Yaya sai dai wa'inda ke tare da kai da suke wasu iyayen namu sam mun kasa samun nutsuwar da ta dace da su, basu da lokacinnka bale su fuskanci rayuwarsu su daidaita abinda ke damunsu, yaya yanzu ace kai da girmanka da darajarka aman baka da lafiya har ta kaika haka? Why ba zaka daidaita masu tunaninsu ka sauko su su fuskanci rayuwa ba? Yayanmu ba haka ake rayuwar aure ba, ba haka ake zama da mace mai daraja ba, yayanmu ina kwadaita maka zama da mace mai mutunci mai daraja wace ta san ciwon kanka, yayanmu....." Tsitt ya yi sai hawayen da yake zubarwa a idannuwansa yana kallon yayansu da ya zuba masa manyan idannuwansa yana kallonsa shima

Dan murmushi ya yi hadi da juyar da kansa a hankali ya ce" Rislan ka san karfe goma sha daya zaka tashi ko?"

Rislan ya sada kansa kasa bai iya bashi amsa ba, saima kukan da yake hanna kansa yi ne da ya kwace masa wanda ya saka Mu'azam wara idannuwansa a kansa kafin ya saki murmushi mai sauti ya matso a hankali ya kama hannunsa ya zaunar da shi bakin bed yana kallonsa a hankali ya ce" Kuka kuma? Sai kace yar budurwa?"

Rislan ya ringa cije lebensa yana ta son goge hawayensa,
Kan giwa ya rike hannunsa yana kallonsa ya ce" ka yi kukanka Dan uwana, ka min kuka ka ji? Ka min kuka sosai, domin nima a jiya na yi kuka....Rislan na yi kuka cikin shiru harma na so ilata kaina, babu irin tunanin da ban yi ba, haka kuma na yarda cewa ashe zama lafiya da mace mai nagarta shine farin cikin rayuwa ba neman kudi na, ka ga ni na fi ba kudi mahinmanci sama da komai, shi yasa na je na zabo masu tsada na aura sannan.....Rislan sannan na rike Izabel a gaban kowa a idon kowa nake mu'amalantarta tamkar iyalina hankalina kwonce....."

Ya dafe gaban goshinsa ya ce" Rislan ta yiwu dan na maida zinna ado ne Allah ke kamani ta nan, ko kuma gaba dayane ban iya shinfida rayuwar iyalina bane har na fuskanci haka? Rislan mata ne sai na nemo su du takamar tawa? Kuma idan na nemo sun ba zan taba samun nutsuwar zuciya ba?, Saima na yi wani fahimta da matan nan guda biyu jiya zuwa yau da suka ga barazana ta ina iya duban watansu a matsayin raya sunna ba watsewa ba suka haukace suke neman hanyar daga min hankali ta kowace fuska, sannan ka san abin takaicin.....?"

Rislan ya girgiza kansa da sauri cike da tarin takaicin matan nan , yayansa ya dan yi shiru yana tunanin shin ya fada masa a duk goce gocensu dan nuna yana da bukatarsu da ya yi ne aka sake daukaka bacin ransa ko bai dace kanninsa ya san irin haka ba?

Ajiyar zuciya ya sauke yana fadin" Miko min abincin na ci sai mu tafi Aéroport na raka ka"

Rislan ya mike ya dauko abincin ya matso masa da shi a ransa yana ayana' babu inda zani walahi sai na hannawa matan nan zaman lafiya tunda mahaukata ne su!, Sai na koyar da su iya rike miji a matsayina na namiji, dan kuwa akoy mata a duniya su din ba sunne kadai karshen da suka rage ba da har zasu wulakanta aure haka ba!

Kwonkwasawar da ake yi ne ya saka Rislan bada damar shigowa yana budewa yayansa abincin yana saka spoon

Da sauri ta karaso da salama a bakinta fuskarta na nuni da ta ci kuka ne ko menene? Fuskar dai a kumbure domin sai dazu ne Nuriyah ke fada mata dukkan abinda ya faru cewar yayanta bashi da lafiya, shine ta haikace ta fashe da kuka da kyar Nuriyar ta lalasheta ta janyota ta rakota su gaishe shi domin ita yanzun matansa sun sa du ta tsani lamarin gidan

"Yaya me ya same ka? Me ya same ka? Yah Rislan ni ban san bashi da lafiya ba, jiya dare muka yi muna yin dambun naman nan, cikin dare ne Nuriyah tace zata zo ta kwashe komai dan ya tsane mansa , ni kuma barci ya hanna min fitowa da na san bashi da lafiya, ko da Mama ta ce ya ci abinci na ce mata eh ya ci, ashe bashi da lafiya, NURIYAH ta ce hannunsa ya kumbura ta ce jikinsa zafi, ta bashi ruwa kuma ta kirawoka Yayanahhhhhhh wayo Allahna....." Ta karashe maganar tana riko hannun yayanta da ya kurawa fuskarta ido tunda ta farra kayaniyar nan

Abinda ya iya tsinta wanda ya dawo masa da tunanin aljanar da ya gani tsakiyar dare ko mafarkin da ya yi a jiya cikin idannuwansa daidai Nuriyar ta shigo tana rabewa ta duka daga cen nesa da wannan zumbulelen hijab din nata tana mai bude muryarta mai sanyi da alamun tsoro wace ta yi masa magana da ita a jiya da farko kafin ta kula da hannunsa ta rikice ta rikeshi a lokacin da bata shiryawa hakan ba

A hankali ya lumshe idannuwansa ya sake budewa ya zuba mata ido , a saman lebensa ya bude bakinsa cen kasa kasa sosia ya furta" NORIYAHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHHH?"

😑😑😑😑😑😑😑😑😑😑

□□□□□□□□ *NEMAN NA KAINA* □□□□□□□□□

Karashensa sabon salo

Na

SAJIDA

Page.
33

I'm sorry yau kadan ne, ina matukar son gama shi kafin azuminma abin na neman min cikasssss, in dai ba so kuke mu ce fatiha an daura , bayan shekara goma sha biyar sun aurar da yarsu 😁♀️ wollah na aika

A saman lebensa ya ambaci sunnantaa lokacin da Auta ke ta maimaita sunnan a cikin bayananta, sai aka taki sa'a ita dinma ta dago a hankali ta saka Idannuwanta a cikin nasa, lokaci daya sai lokacin da ta talabo shi ta kafa masa ruwa a bakinsa tana ambatar masa ya sha ya fado masa a ransa

Da sauri suka dauke idannuwansu a kan junna a tare, wanda hakan a kan idannuwan RISLAN ya faru
Mikewa ya yi daga zaunen da yake ya juya ya dauki karamar wayarsa dan ya tabata kakus tana cen ta rikice masu rabonta da shi tun jiya da sasafe basu yi wayar sasafen bama ta gado

Kannensa ya sake kallo da suke shinfide da yannayi na damuwa da damuwarsa ya sakar masu Murmushin da bakinsa saman lebensa ya juya yana fadin" Idan kun gama ku rufo dakin ina zuwa"

Baki sake Murjanatu ke kallon kofar da ya fice ta juyo tana fadin" Yah Rislan ina yaya zai tafi kuma? Ba shine ba lafiya ba? Kalli hannunsa fa ima zai tafi ne?"

Yar dariya ya yi shima yana fadin" Ni kam hakan ya min daidai ya manta shi yace yanzu zai kaini aéroport, a hakan da ya manta ta fi gyarani ta fadi gidan sauki Walahi "

Ajiyar zuciya ta sauke tana kallon Nuriyah ta ce" Nuriy sai ki tashi dodon naki ya tafi fa"

Nuriyah ta sake dagowa tana mikewa jikinta tamkar an cire mata lakka ta juya itama tana fadin" Bara na koma na hada kayan wankinmu Auta bana son wankin naj na inji sake kashe min jiki yake yi, na fi so na darj....." Dif ta dauke wuta sakamakon goshinta da ya hade da kirjinsa a lokacin da ya dawo ya bude ya shigo

Shima idannuwansa ya sake dorawa a kanta yana binta da kallo irin tsoratar da ta yi ta yi baya tana wara manyan idannuwanta a saman kansa lokaci daya kuma ta nemi sake rikicewa irin na jiya da ta yi , watau ta daburce tana ta neman bashi hakuri da dukkan gaskiyarta

Haka kawai ya ringa ji a zuciyarsa tamkar ya riko hannunta ya bata hakuri kan doke mata goshi da ya yi, sosai ya ringa jin bakinsa zai bude ya nufeta ya rike ya ga goshinta ko ya ji mata rauni ne? Sai ya ringa ji yana so ya ce mata ta daina bashi hakuri bata yi masa komai ba
Aman sai ya kasa aikata hakan yama juya wajen Rislan yana fadin" Ka yi ka fito a kaika aéroport Likita"

Ya kuma juya wajen Murja yana fadin" Baby me ya hanna malaminki na islamiya zuwa kwana biyu?"

Auta ta ce" Yaya rasuwa aka yi masa ne, sunna zaman makoki ai Hajiama ta je ta yi gaisuwa"

Sake juyawa ya yi bai ce komai ba, da sauri Auta ta sake daga kafarta ta bi bayansa tana fadin" Yaya, dama , dama dan Allah ina so yau mu je shan ice cream"

Dan sake juyowa ya yi yana kallonta daidai Djamilart ta fito yauma cikin shiga ta atampa dakakiya mai kyan gaske ta kashe daurin nan nata tamkar gamo tana murmushi ta shiga gaishe shi da dan rage tsayinta tana hade hannayenta irin yadda suke yi din nan sannan ta bi hannunsa da kallo da kula ta ce " Hubby me ya samu hannunka ne?"

KAN GIWA ya bi hannun nasa da kallo ba tare da ya amsa gaisuwar tata ba a hade sosai ya furta mata kalmar "Nothing" sannan ya sake kallon Murjanatu yana duba agogonsa ya ce" Ku je karfe biyar na yama , ku dawo karfe shida da rabu har tafiya da dawowa, kar magariba ta maku a cen"

Cike da farin ciki take amsawa da in sha Allah sannan ya wuce ya tafi ya bar Djamilart da mamakin irin amsar da ta samu yau a wajensa ta halin ko in kula, kamar wata wace bai sani din nan ba bayan ita a sanninta bata aikata wani laifi ba,

bayan wannanma ita fitane zata yi tana da bukatar kudi dan zata je ne ta yi wasu siyaya da ta gani an zuba sababin atampopi yan kasa da kasa

Kallon Murjanatu ta yi tana fadin" Me yake damunsa ne? Me ya samu hannunsa a nade haka?"

Murjanatu ta girgiza kanta itama a hade ta furta kalmar " I don't know" ta wuce wajen su Rislan dake tsaye shi da NURIYAH

NURIYAH ta yi yar dariya tana fadin" Wai tsaya yayanah, wai shi karatun dama wahala ne da shi kake jajen ba zaka koma ba baka son tafiya? Wani mawaki ke fadin tafiya mabudin ilimi ko dan ka tafi ka yi gane gane ka ilimantu ai zaka kwadaitu da son komawa"

Murmushi ya yi yana kallon Murjanatu da ta karaso tana fadin" Sis Nuriyah, ai shi Broth ya fi so ya yi zamansa a kasarsa, kuma shi ya ce sai ya yi karatun professor, daga bana nefa ya gama aman kin ga ya kiya sai da aka hado shi da baban yaya yanzun"

Yana makala abin wayarsa ya ce" Ba zaku gane bane yan matan Hajia, idan kana nesa da yaya komai a duhu ake baka, idan kana kusa ciki kake dumu dumu gaba da baya haja ce bashasha, a wannan karronma na so na zauna ne dan na daidaita rikicin cikin gidan nan, aman yaya ya ki koda amsani a kan maganar "

Nuriyah ta yi dan Murmushi tana juyawa tare da kama hanuar dakinsu dan ta kula zasu shiga maganar cikin gidansu tana fadin " A sauka lafiya, Allah ya bada sa'ar karatu, idan ka je ka cewa wannan dan film din nan musulmin nan wannan wanda Auta ke nunan wakokinsa a wayarta ina gaishe shi"

Murjanatu ta yi daria tana cewa" Oh sharukhan?, Ai kam kin san inda yake da family dinsa daga dlgu sai an shiga kwale kwale ya tsalakaka , Idan ya tsalakaka ko wa ya tambaya gidan Khan Sharu za'a nuna maka sai dai tsaron ne ba kowa ke iya shiga anguwar ba sai da katin gayata"

Shima dariyar ya yi yana kallonta har ta shige dakinsu sannan ya fuskanci Murjanatu ya riko hannunta yana fadin" Me kika fuskanta da bakuwarki kuma kawarki?"

Murjanatu ta dan ja tana kallonsa ta ce" Yaya kana tune dai dai da yadda kuka yi kafin ka yi tafiyar nan ko? Dan Allah ka barta ta yanke ta ga abinda ya dace da rayuwarta yaya"

Sai da ya tsatsareta da idannuwansa kafin ya yi murmushi ya ce" Ina tsoron ta samu yankewar shawarar da bata taba jira ko tsamani ba Auta, domin ni zan iya ce maki na yi dana sannin gagawar maganar da na yi a kanta, da na sani da na yi jira na ga wani abin daban.....sai dai ko a haka zan iya ce maki zan iya sadaukar da zuciyar dake bugawa a kirjina saboda wanda ya cencenta ya samu bale soyaya, gaskiya zan iya bada raina wa wannan bawa dan shima zai min sama da haka!"

Gaba daya ya sakata a cikin hali na tunanin abinda maganarsa ke nufi, a hankali ta ce" Yaya ban fahimci inda maganar nan ta dosa ba fa"

Bakinsa ya tabe yana yin gaba hadi da fadin" Zaki fahimta na tafi"

Da sauri ta bi bayansa dan ta masa rakiya

Sunna fitowa suka ga wani shirmen a wajen Djamilarth dake kwasar rigima da sojan dake kula da harkar shige da ficen mutan bangaren
Rai bace ta ce" Kai wai ka gane ni kuwa? Nice amaryar KAN GIWA a kan me zaka ce ba zan fita ba? Ka bani katin fita na fada maka"

Fuskarsa a daure yana tsaye kikam dinsa ya ce" Ki yi hakuri madame umarni ne daga oga , babu inda zaki je"

Daga haka ya maida bakin gilas dinsa da ya cire dan girmamawa a gareta ya juya ya ci gaba da aikinsa ba tare da ya sake koda yi mata kallo daya ba

Rai bace ta ringa magangannu da yarenta da su ashar kala daban daban ta juya ta koma tana fadin" Bara na kireshi shi sai ya baka damar barina fita, yaishe yake hannamu fita? Ko saudiya zan je daga nan ai zai barni na tafi ne"

Da ido suka bita har ta shige kafin Rislan ya sake zubawa makeken tsakiyar gidan ido yana fadin" Walahi idan suka kasance a nutsen nan sai ki rantse sai tsuntsaye a Palace KAN GIWA"

Yar dariya ta yi kadan tana fadin" kowa yana cen yana aikinsa, basu san idan akoy mutun mai sauki bayan yayanmu ne, shi fa wasu abubuwan da suke yi baima san dalilin da ya sa suke yi ba, shi kawai bai dame shi bane ya tsaya ya bincika din , idan ka ga yana fada kuwa to fa a fannin abinci ne, baya so ko da wasa a yi masa wasa da tsaftar abincinsa da wajen cin abincin da komai da komai da ya shafi abincin, shi yasa suke tsaye kan kafafuwansu basa ji basa gani basa wasa da girkinsa ko kadan

_____

Tafiyar da suka yi nata dauki lokaci ba domin ko minti arba'in basu dauka sunna tafiyar ba suka karaso dan kauyen da yayi niyar zuwa yai din

Tunda motocin suka tsaya ya zubawa koren shukokin dake kadawa a hankali alfarmar albarkar damina sun yi shar da su sai iska mai sanyi suke badawa kadan kadan sunna rausayawa

A hankali ya sake juyo hannunsa yana duba hannun nasa mai bandejin nan ya gwada jimke shi a hankali sannan ya sake kallon madubin motar da sojan dake tsaye mai farar fata nasara wanda gashin kansa ke dan kadawa sakamakon iskar dake kadawa mai sanyi da kanshin damina

A saman lebensa ya furta" *She takes care of me after all she’s afraid of me* "..... ....Hannun nasa ya sake dubawa yana mikar da shi kadan irin yadda yakke girke sosai ya sauke dan murmushin da ya fito a saman lebensa a hankali ya sake furta" NOURIYAHHHH, who are u?.....>.....juste ina son sannin daga ina laushinki ya samu? Yaya aka yi kika iya pretending like kina da tsoro kamar wata yar lalausar fulawa mai laushi ???????????? Ko haka suke matan a kannanun shekaru irin naki ne?????????? Sai sun fara girma sai kuma su dawo kamar mahaukata ??????"

Aa fa.....rashin sa'a aka ci oga kake tare da yan eyane😂😂😂😂

□□□□□□□□ *NEMAN NA KAINA* □□□□□□□□□

Karashensa sabon salo

Na

SAJIDA

Page.
34

A wajen da suka yi ne zasu hadu da mai garin garin da kuma yan kauyen da suka kawo tallar kwaririkansu mutun har goma sha daya suka hade

Tunda ya karaso bayan bodyguard dinsa sun gama gyare gyaren wajen ya zauna ya ringa amsar hannayen jama'ar garin sunna gaisawa cike da mutuntawa du kuwa da irin duban da ya kula sunna binsa da shi wanda ya rasa fasararsa, kamar sun ga bakon halitar nan

A nutse ya fuskanci mai gari dake fadin" Alhamdulilah, Elhaji kamar yadda ka bukaci sannin a kan wani dalili mutanen kauyen nan mai albarka suke son saka albarkar dake tare da su a kasuwa , harma ka ce kowa ya zo da dalilin nasa a bayane ka gani kafin a yi maganar gasunnan da kansu da kuma dalilansu, zan iya cewa a cikin nan mutun biyar magana ce ta gado, gasu da yan uwansu wanda ya zama wajibi a raba dukiyar mamaci bayan rasuwarsa wa shakikansa, yawansu ya sa ba zai yiwu su iya yiwa kwaririkansu kwaya takwas rabiya ta daidaitu ba, gashi kawunna a rabe sosai kowa da ina yake zaune da iyalinsa bale a yi aiki tare a raba ladan aikin, sai wa'inda harkar jarin kasuwarsu da suke yi a birni ne ya karye suke son dora wani jarin dan dogaro da kai ta kowani fanni idan dai mutun zai iya tsare kansa da fadawa halaka saboda datin duniya to fa alkhairi ne, dan samun kadarar da zaka juya dinma Alkhairi ne, sunne gasunnan su su hudu, sai Balan Sabo da zai aurar da y'arsa auta kuma babar y'arsa domin ita daya tal Allah ya bashi kuma har karatun boko ta yi da kake ganninta a nan, yanzun Allah ya fitar mata da miji dan Birni domin kuwa ma'aikacin gidan wuta nema, shi yasa ya sameni da tasa bukatar kan shima yana so a saka nasa a kasuwar dan yana son yiwa Auta bajinta , ka dai san

kayanmu na aure na nan kauye da naku ba daya ba.....to wannan shine dalilansu , gasu kuma da kansu a zazaune"

Shi Kan Giwa gaba daya a bayanan yarinyar da aka nuna aka ce za'a yiwa aure ne abin ya fi bashi mamaki da kuma damunsa
Dan haka bai yi kasa da gwuiwa ba wajen duban mai gari da kulawa sosai ya ce" Aman wannan yarinyar karama za'a aurar?"

Mai garinma ya dubi budurwar da Kan Giwa ke maganar yarinya karama za'a aurar, to ai su a garinsu wannan din gaskiya tama zama babar kanta ba'ai mata aure ba, domin mahaifinta mutun ne mau bin y'aya, ko dan ita daya ya malaka a duniya bafa mai takurawa y'ar baba, shi yasa ta yi karatunta har ta gama secondary school sannan zai aurar da ita, in ba Kan Giwa ba sa'aninta ai sun tara y'aya sosai wasun har sun zuba uku ai, yanzu haka kannan bayanta ne zasu mata gorance ai, a nutse shima ya bashi amsar kwarai kuwa ita

Kan Giwa mamaki ya sake neman kashe shi a zaunen da yake yana kiyasta shekarun yarinyar da tunanin anya ta kai shekara goma sha takwasma kuwa?
Sai dai bai kuma tofa wata magana a kan abinda ya shafi yarinyar ba ya fuskance su a nutse ya ce" A cikin masu son siyar da Kwarinsu na ware masu rabiyar gado, su sunna iya komawa gefe idan aj gama a yi bayanin abinda suka yanke sai a shelanta wa mutanen kauyen idan da mai so ya siya, in babu mai so sai a siyarwa wani, "

Du gefen suka koma sannan ya dora da magana bayan ya fuskanci sauran ya shiga fadin" A cikin yan kasuwar nan da suka rage, zan so na sake jinjinar bukatarku, ita wannan da kuke ganni kwari ce mai kawo kayan itatuwa da su lambu, ku kun fini sannin cewa rufin asiri ce wa kasuwancinku harma da iyalinku kansu, waje ne da zaku shuka , shukar ta firo ta yi yabanya, a ciki dole zaku siyar, ku ci, ku yi kyauta, ku yi sadaka....., Idan har abin juyawar hannayenku akoy kwari ne bashi da shi muna iya dubawa a karra maku hannun jari, idan kuma kun riga kun yanke hukuncin siyarwa ne, koda kun barta ba zaku kuma iya ci gaba da kulawa da ita yadda ya dace ba, a nemi mai so a fansa masa ya kula da ita yadda ya dace domin mu abin alfahari ne a wajenmu"

Dan kuskus ne yake wakana a tsakaninsu bayan shirun Kan Giwa, dan haka ya juya shima wajen mai garin da ya nemi talafinsa a matsayinsa na aboki, kuma Soja wanda ya tabata idan ya shiga lamarin ya yiwa mutan kauyen gwari gwari zasu iya daidaita tunaninsu a kan yinkuron siyar da alkhairan kauyen, dan kuwa ya maimaita maganarsu ne da suka ce anfanin kadara ai siyarwa ne dan su yarda da shi ba yana son hanna su bane dan wata manufa, aman idan kace kadarar dake ajiye a matsayin taka da zarar ka hadu da wani dan tashin hankali zaka kawar ka siyar ai da ba'a ajiye komai ba a duniya, balema su biyar din nan da suka rage yan kasuwar da Baba , a gaskiya bukatocinsu bai kai na su rabu da abu mai mahinmanci ba, shi ko dan yana dan karkarar ne shima? A duniya abun nan hudu baya son rabuwa da su da dadin rai, watau GONA, GARKA, ABIN KIWO, TSIRO, yana rike nasa da mahinmancin gaske, domin da su yake bajinta iya bajinta, ga darajar kauyen kanta ai sunne, su yan birnin da suke takamar birni birni birni idan babu Noma , ba kayayakin garka ai sun shiga ukunsu, shi kam baya son siyarwar gaskiya, sai dai kuma maganar karin jarin da Kan GIWA ya yi ne ya saka shi a tunanin tabas siyarwar zasu yi, domun mutumesn kauye ya ki jinnin ka ce zaka yi wani tunanin samun kudi da shi kai tsaye kawai, domin gurguwar fahimta zasu yiwa abin

Wanda ya fi wayewar aka saka ya yi tambayar yana ta firifiritu da ido ya ce" Elhaji, mun ji bayanin nan sosai, sai dai wani hanzari ba gudu ba, shi karin jarin biyansa da zamu ringa yi du shekara shekara ne? A shekarar nawa zamu ringa zubawa? Idan

muka ji sai kowa ya je ya duba yannayin samunsa in zai iya sai ya amsa, idan ba zai iya ba kuwa sai ya siyar da Garkarsa domin ka san yannayin samun, yannayin kasuwar wani lokacin yadda ka kula ka je haka zaka lodo ka dawo har sai makocinka ya maka alfarmar kudin mauta bashi, wannan shine matsalarmu kuma abinda muke son ji".....

Maimakun abin ya bata masa rai a yau sai ya samu kansa da jin wani farin cikin reaction din mutanen, ashe dai dan sunna cikin riga irin wannan sunna tafe kamar basu san ciwon kansu ba sunna da nasu tunanin summa? Dan haka ya gyara zamnsa yana Murmushi ya ce" Masha Allah, Masha Allah, in sha Allah shi talafin jarin za'a baku ne fisabililahi, nima mutun ne mai zuciyar nema, na horu da *NEMAN NA KAINA* tunda kannanun shekaruna, shi yasa nake ba mai nema daraja nake kuma talafa masa da dukkan abinda Allah ya sa zan iya bashi talafi dan gannin ya samu ci gaba a duniyar nemansa"

Baba dake zaunensa tun dazun yana yan muzuransa ya karkato da kyau da shegen mamaki ya ce" Kanga yaro, ka tabata da maganarka kuwa? Kana nufin za'a basu kudi kyauta haka salin alin su tafi ba wani bita da kulin da zai biyo baya? Ka ga fa maman Y'ar baba kan fadin yan birni akoy iya bita da kuli, dan nan aka kawo talabijin aka kafa aake kunnata da zafin ranar garin nan dan wani tsohon wulakanci da sata irin ta yan birni sai ka biya kulin zaka kalla, ni ai bai fi sai bakwai da na je na kalla ba, tunda na ga wata karya karara naa daina kallo kar a taba min imanina ina zaman zamana"

Murmushi ne ya subucew Kan Giwa gannin tsakaninsa da Allah yake maganarsa ya ce" Eh Baba, za'a yi takafi ne domin Allah, ba su kadai ba kowama in sha Allah"
Wani mamakin ya sake kama baba ya dan sake matsowa yana kallon kan Giwa ya ce" Yaro kana nufin talafin harda ni?"

Kan Giwa ya fuskanceshi sosai dan kuwa ya kula tsohon nan idan ba amsa ya bashi yadda ya dace ba tabas yana iya rikita tunanin kowa a nan din , ga yarsa sai son hanna shi take aman yana rike da hannunta yana fadin ta barshi ya yi magana mana kar a cuci su Muntaka a banza , ko ba komai ai shine ababa a nan din

Kan Giwa a nutsensa ya ce" In sha Allah Baba, har kaima za'a yiwa Auta kayan dakinta ba sai kaa siyar da Garkarka ba, tunda ka ga ai Garkar tana kawo anfani sosai ko?"

Dif wajen ya yi na yan sekwani kafin Baba ya sake wara idannuwansa ya rage muryarsa sosai yana fadin" Yaro, da Maman yar baba ta je birni da kawarta aka tambayo gado mai runfa irin na yan birni cewa suka suka yi sai a makudan kudin da suka kai rabin millian zasu mana har kujerunsa, ka ga kuwa wannan ai dole na sigar da garkarnan tunda kudin ai da yawa"

Yanzun kam murmushinsa sai da ya jima a saman lebensa ya fuskanci abokinsa da ya gama cika da farin ciki da sannin cewa yau fa mutan kauyensa sun taki sa'a mai girma da ya yarda ya zo da kansa, ya kuma san cewa a yau farin ciki sai ya shinfidu a waje da yawa, domin kuwa ya san waye Kan Giwa, tunda mahaifinsa ya rasu aka nada shi sarkin garin ya ajiye aiki ya dawo dole dan kula da kauyensu yake missing din aiki a karkashin kan Giwa, wanda ya zamto aboki a gareshi mai matukar mahinmanci

Mai gari ya ce" Eh baba, ai tunda Allah ya sa ya ce zai yi , zai yin ne in sha Allahu duka komai da komai"

Nan fa tsoho ya so rikice masu , zane yake yana fadin kudin kaza ne fa? Ana sake tabatar masa, karshe dai ya yi shiru da bakinsa kafin ya ce" to ko dai kannen shugaban kasa ne shi din?, Dan Allah a inaa kuke samun kudi haka ne yaro? Ko da aka ce yan birni sun ci gana har shuka kudi suke haka ne?"

Kan Giwa ya yi yar dariya yana fadin" Baba, ba'a shuka kudi, NEMAN SU ake yi, sai dai NEMAN nasu kansa kala daban daban ne wannan din da izinin Allah zaku ci halal, sai dai kar kudin kowama ya rudeku, domun Wani NEMAN NA KAN da Kai ake yinsa baba....."

Ai kam da wannan ya samu ya kakashe dukkan rigimar da ya dace sannan suka shiga yawatawa a cikin kwaririka sunna shan sansanyar iskar garin sunna dan zantawa gwanin ban sha'awa, a wannan kauyen ya yi sallar azahar, da la'asar, har sai da yama ta yi sosai suka kama hanyar gida yana waya da Su hajia dake ta tambayar jikinsa a rikice domin auta ta sanar mata bashi da lafiya shi kuma sai tarota yake yana sake fadin ba fa wani abu bane rikicin Auta ne har suka karaso bangaren Hajiar da yake so ya leka yau ya ga yaya suke kula da tsaftar wajen, domin koda basa nan bai rufe wajen ba ya bari a hannun amintatunsa ana kula da wajen sosai tamkar sunna nan

"Tsaya tsaya ki ga yadda take yi ita hajiar, bara ki gani sake riken jakar ke dai Auta" Nuriyah ta fada tana sake daka fuska da wanu kwasheshen gilas baki a fuskarta ta karkace daurin nan kwali ta turo shi sosai gaban goshinta tana harare harare da lebenta jajaye ta murza yar agogon hannunta tana fadin" Ke yarinya a kudin ayabar na cire ashirin ashirin idan zaki siyar ki siyar, idan ba zaki siyarba ki karra gaba warin rana kike kar ki goga min a jikina!"

A tare suka bushe da dariya Nuriyah ta juyo tana cire bakin gilasss din zara dora da surutun dake samunta idan suka kasance daga ita sai Murjanatu tamkar aku idannuwanta suka sauka a cikin nasa yana tsaye dan nesa da su kadan aman daga bayansu yana kallonsu gaba dayansu da kallon da bata san asalin wajenda ya dace ta ajiye shi ba, harara ne na sun cika masa waje da kayan shirme sunna kuma iface iface ko me?

Da sauri ta rike table din da suka cike da Ice cream dan kar ta kifa hakan ya sa dan kwalin da ta yi daurin irin hajiyoyin dake yaga su a bakin danja idan sunna tallah sunna shan dariya ita da Murjanatu ya kunce ya fadi kasa , hakan ya bayanar da lalausan gashin kanta mai saka bawa a kokonta asalinta domin idan ya haye da farar fatarta tamkar ba tamu ba mu mu din nan

Idannuwansa ya cire a hankali a kanta, lokaci daya kuma tamkar magnet ya sake maido au ya zuba mata a kanta tun daga kan rigar dake jikinta doguwa har kasa wace zai iya kiranta tamkar buhu ta mata domin rigar kamar abaya ce budadiya sosai da sosai, sam bata lafe mata a jikinta ko kadan ba kuma dogayen hannuwa ne da ita suma a buden sai wajen tsintsiyar ne ya daure a daidai nan kawai

Gashin kanta ne ya zubo gaba a lokacin da ta duke kasa gaba dayantaa tana ta son gaishe shi, wanda hakan ya sa Murjanatu juyawa ta gane shine tana murmushi itama ta mike ya tarboshi da yi masa oyoyo tana duban hannunsa da tambayar jikinsa

Idannuwansa a saman fuskarta sosai kasa kasa ya ce" Me yasa take saka atach ne ita kuma kalar wannan?"

Sai da Murjanatu ta juya ne ta gane da wace yake, da dan mamaki da kuma dariya dariya ta ce"

□□□□□ A sha ruwa lafiya sisters□□□□□□